Mintu kusan goma ban kara kallon inda yake ba. Cikin dubara na kara kai dubana gurin ganin idanunsa nayi a rufe. Na mike da sauri na nufi toilet din ina tafiya ina had'a hanya. Karar bude kofar ce yasa ya bud'e idonsa ganinta yayi ta shiga tana rufewa da sauri.

A hankali ya maida idonsa ya rufe yana sak'a abubuwa da dama a kan yarinyar.

Kyawun da tsaruwar toilet din bai dame ni ba,abunda na shiga yi shine a gabana kayana na tube na  hita na kunna ta ruwan zafi na surka yanda nake so, tsugunawa nayi na fara Wanka tsarki zuciya ta na min zafi da radad'i lura da nayi dole sai nayi wanka saboda abunda naji yana

futa daga kasana na wanke sosai na maida kayana na futo.

Bed din na kalla na fara laluben abunda zanyi sallah dashi domin mayafi na karami ne, gashi ba muyu magariba da isha ba.

A hankali na isa bed din na sa hannuna ina laluben k'aramin maya fina.

A hankali yace." Me kike nema ne."?
Banza nayi dashi na cigaba da laluben mayafina. Caraf ya rike hannuna yana murzawa, na shiga tashin hankali sosai jin abun jiya yana nema ya dawo min, da sauri na fuzge hannuna da ya rike min nace." Tashi ni in duba maya fina inyi sallah."

Mik'ewa zaune yayi ya kunna futular gefan gado, muka had'a ido dashi, cike da fargaba na d'auke kaina daga kansa ganin yanda idanunsa yake lumshe alamun bacci hakan ya sanya tsigar jikina Mik'ewa nace wannan bawa ko aljani sai haka.

Cike da karsashi ya mike nayi saurin matsawa gefe ina domin ina tsoran ya rab'e bi ya karya min alwala ta tunda na lura ya zame min masifa a rayuwata daga haduwa dashi yau.

Wani drowar naga ya bude ya ciro wani abu cikin Leda. Karasowa yayi inda nake tsaye dashi a hannunsa, kauda kaina nayi daga kanshi.

"Ungo nan ki cire wannan tsumman na jikin ki kiyi amfani da wannan gurin yin ibadahr ki."

Shek'ek'e na kalle shi ina tab'e bakina kamar bazan karb'a kuma  sai na karb'a. Wucewar sa yayi ni kuma na koma toilet din domin in bude inga ko menene Dan na damu da inyi sallolina Ledar na yage na zazzage abunda yake ciki wata doguwar riga na gani me kyau da tsada kotton ce rigar larabawan Oman sun fi amfani da ita har da hijab dinta fari tas dashi, a fili nace "

ko a ina ya samu kayan mata oho masa.

Wata zuciyar tace min "kin manta yana mu'amula dasu mybe yana tanadar kayan ne saboda Ku kema gashi yanzu tayi miki amfani.

Jiki babu k'wari na fara kwabe kayan jikina na warware rigar na fara sawa,kamar an auna da jikina rigar tayi min dai-dai kuma ko ban tambaya nasan tayi min kyau, Matsalar ta guda yanda kirjin ya matse ni, kasancewar Allah yayi min baiwar manya manyan breast sun takure guri guda, a fili nace ya dai fi babu na zauna da hijab din a jikina har Safiya

Futowa nayi a hankali nafi gurin da naga yayi sallah na tsaya kan dadduma na fara rama sallolina cike da nadama da Neman afuwa gurin ubangiji k'arfe daya na dare banyi sallahr Isha'i ba abunda bai taba faruwa ba tunda uwata ta haife ni.

Bayan na idar nayi addu'oina kamar yanda na saba, nan kan daddumar na kwanta gami da takure jikina INA addu'a

A takaice dai nan na kwana inda nayi farkawa kusan biyar ina kallon inda yake kwance Wanda yake baccinsa cikin koshin lafiya sai daf da asubah bacci me dad'i yayi nasarar d'auke ni.

Kiran Sallahr farko ne ya farkar dashi, bargon jikinsa ya cire ya zura hannunsa ya kunna futalar gefan gado, kad'an hankalinsa na gurin da take kwance, bacci take sosai. Rigar shi ya d'auko ya sanya kai tsaye yq nufi toilet.

Wanka ya fara yi sannan ya dauro alwala ya futo yana tsane jikinsa da towol, duk da wannan motsin da yake bai sa na farka ba domin baccin me nauyi ne ya d'auke ni.

A nutse ya shirya ya jikinsa turaranshi ya fesa me kamshi da tsada Wanda yabi jikinsa da duk wani Abu nasa, cikin yanayin takun shi ya nufi inda take kwance ranshi ya baci ganin yadda take masa bacci kan daddumar sallah. K'afar shi ya sa ya zungiri tata k'afar ko motsi bata yi ba,

Agogo ya kalla so yake yayi raka'atanin fajri kafin ta futa zuwa massalaci.

Cikin wani irin muryar ya fara ambaton sunanta "Asma'u" Ke Asma'u!!!

Kamar a mafarki naji ana kiran sunana
Da sauri na mik'e zaune ina ja da baya ganin yanda yayi min rumfa, muryashi me taushi yace." Tashi ki bani guri inyi sallah."   d'auke kaina nayi daka kanshi ina Ala wadai ds tur da halinshi, ya gama aikata alfasha ya ishi mutane da sallah.

A hankali na mike na koma can gefe guda gami da takure jikina, daddumar ya daga ya karkad'eta ya mayar ya shimfid'a data, ina kallonsa ya tada sallah raka'a biyu yayi ya salle me yayi addu'oin sa sannan ya mike a nutse ya futa daga dakin.

Ajiyar zuciya na sauke zuciya ta na sake-sake akansa tabbas Akwai wani al'amari nashi dake rufe

Jin ana kiran sallah ne yasa na mike da sauri na futa daga dakin tunda ya bud'e tsayawa nayi ina bin dank'areran falon da kallo ya had'u k'arshe fad'ar kyawunshi da tsaruwar shi bata lokaci ne ko ina tar haske  Mimi nake lalube can na hango ta cikin kujera me cin mutum daya ta mak'ure jikinta da sauri na k'arasa inda take ina kiran sunanta.

Ta bude ido a furgice tana kallona sai kuma ta fashe da kuka sosai, sauri nayi na rufe mata bakinta na kamata ta tashi, hanyar futa muka nufa.

A bude take, abun mamaki muna dosar ta kofar sai ta fara tafiya suuuuuuuuu ta rufe kanta, Jan hannun Mimi nayi da gudu muke k'okarin ture  kofar, abun nasara tuni ta rufe har tana hadawa da hannu  ihu na kurma ina matse shi.

Mimi tace." Kinga Asma'u kiran sallah ake muje muyi alwala tun daga toilet can muyi sallah mu jira gari yayi haske."

Babu yanda na iya haka muka koma ciki Mimi ta shiga toilet ni kuma na zauna jiran futowar ta

Minti biyu da zamana sai ga Alina ta futo daga wani bedroom tana sanye da wata mutsitsiyar Riga da gajeran wando cinyoyinta duk a waje, Attachment din kanta duk ta duje. Shek'eke na kalleta naja tsaki gami da fad'in." 'Yar isakar k'arya da wofi."

Da sauri ta juyo tana kallon inda nake zaune domin Sam batayi tunanin akwai mutum a gurin ba.

Cikin jin zafin abunda nace mata tace." Wallahi Asma'u zagin da kike min ya ishe ki tun jiya kike zagina saboda tsaurin ido irin naki har kina kamani da kokawa,wallahi kinci sa'a a gaban *Amjad* ina tsoran fushinsa amma da sai nayi miki rashin mutumci kin San dai halina ko a skull bani da kyau bana barin ta kwana." Tsaye na mike nayi kanta cike da masifa da neman tashin hankali nace." Durun uwar ki Alina don Allah Ki dauki mataki kan abunda na miki ehee ni kinsan irin masifa da bala'in da kika sanya ni a ciki tsakanin jiya da yau? Kin fi kowa sanin wacece ni kin san na fiki rashin mutumci wallahi sai na rama abunda kika sa wannan Dan iskan yayi min."

Rik'e baki tayi cike da mamaki tace." *Amjad* din kike zagi Asma'u tun jiya fa naji kina aibata shi gami da zaginshi wallahi ki kuka da kanki, Dan baki San waye shi ba kuma baki San me ya taka ba bakin san d'aurin gindin da yake dashi na a kasarnan.".

A har zuk'e nace." An zageshi din shi waye ko a gabansa ma zan zageshi ba wani abun bane idan kin Isa ki fada masa in ya shigo, ke dashi duk 'yayan iska, 'yar durun uwa kawai.'

Alina ta fusata! Iya fusata jin ina zaginta lallai baza ta lamunta ba, da gudu tayo kaina muka

sark'e da kokawa sosai.

Mimi ta futo taga abunda yake faruwa kanmu tayi tana k'okarin rabamu muna bugeta sai ta koma gefe tana kallon ikon Allah.

Yana bud'e kofa yaga abunda yake faruwa, duk bamu lura da shigowar sa ba Mimi ce kawai ta lura tsabar kwarjinsa yasa ta kasa fada masa abunda ya hadamu sunkuyar da kanta kurrum tayi ya wuce ta cike da karsashi ya durfafo mu fuskarsa kamar an aiko da mala'ikan mutuwa.

Alina na mukure jikin bango tana kifta ido saboda shak'ar da nayi mata, sai kakari take tana k'okarin k'watar kanta ni kuma ina kara matseta tare da fadin." Nace miki ki kwaci kanki a hannuna, ni zaki yaudara ki sa muzo birthday din ki, ki jefa mu halin masifa eheeee! Kin San irin jarfar da kika sanya ni a ciki tsakanin jiya da yau, bayan wannan ma me kike so muce idan mun koma gida. Alina sai na dauki fansar abunda kika mun dake d'an Iska *Amjad* da kike damuna da shi."

Hannunsa guda ya sanya ya funcike ni daga jikin Alina ya yarfar dani guri guda, yana wani irin huci!! Da mugun gudu na mike na kara komawa kan Alina, yayi saurin tare ni da gangar jikinsa, ya matse a bango!! Muka fara kallon kallo, lumsassun idonsa ya zuba min sunyi ja saboda b'acin rai. babu walwala ko ta kwabo a tare dashi.

Kirjina ya matse da nawa kirjin sosai ya zura hannunsa ta bayana yana shafo mazaunai na cikin wani irin dan iskan salo.

Numfashina ya dunga futa sama-sama lokaci kankani na susuce  yayi lakwas duk kuzarin da nake ji dashi ya gudu, sai naji gwiwa ta tayi sanyi k'alau ina nema in zube a gurin.
[11/1, 10:55 PM] .: *BABBAN YARO*

mallakar_BINTA UMAR

LITTAFIN MALLAKI NA NE KUN BIYA KUD'IN KARATU NE KAWAI DUK WACCE TASAN ZATA FUTA DASHI WAJE DON GIRMAN ALLAH TAYI MIN MAGANA NA DAWO MATA DA KUDIN TA.

*15*

Saki na yayi na zube a gurin, ya tsaya kaina yana sakin wani muskilin murmushi tare da shafa kwantaccan gashin dake fuskar shi.

Saurin kauda kaina nayi da kansa leb'ena sai rawa yake ni kadai nasan halin da nake ciki a lokacin.

Murza hannunsa yayi kamar yarda ya saba ya kauce da kaina, a hankali ya tsugana kusa da Alina dake nishin wahala ya dagota tare da rungume kungunta suka nufi bedroom d'insa.

Kallo na bisu dashi yayin da naji wani irin k'aton Abu yazo ya tokare min a mak'ogaro ganin yanda hannunshi yake tab'a mazaunai Alina.

Mimi ta k'araso inda nake takure tace." Asma'u ina hadaki da girman Allah da Annabi ki iya bakin ki kibari mu rabu da guy nan lafiya duk wannan abun da kikeyi bakya nasara akansa, wahalar da kanki kike."

Cikin jin zafin Abunda tace." Nace." Ni kiyi min shiru don Allah don dai ke ba ke akaiwa abunda akaimin ba shiyasa kike fadin haka."

Rike baki Mimi tayi tace." Wallahi abunda ya faru dake ji nake tamkar ni akayi wa dadin da naji kawai yanda naga kin futo daga dakin k'alau dake wannan yana nuna min cewar baiyi raping din ki ba."

Kaina na sunkuyar kasa cikin zuciyata nace." Ke kike maganar raping Mimi ni kadai nasan halin da ya sanya ni tsakanin jiya da yau.

Mimi ta zauna tana rarrashina cewar don Allah ko ya futo kar in kara tanka masa kawai muyi kokari mu rabu lafiya dashi.

To nima na yarda da shawararta domin ina ganin idan ba haka ba mutumin nan zai iya sakawa na mutu saboda abunda nake ji in ya rabe ni.

Awarsu hud'u a cikin dakin sannan suka futo. Muna zaune ni da Mimi kujera guda lokacin Fleengs din da nake ji a game dashi ya rago sai abunda baza'a rasaba.

Da sauri na kauda kaina ganin yanda yayi min wani mugun kyau Sosai ya dauki wanka dress din ya mutukar yi masa kyau, yana sanye da wani bleu jinsh wanda yake gwiwoyinsa duk a fashe wanda be san tsadar shi ba sai yace yasa wando lallatace.

Tare da wata shart me k'aramin hannu itama pink color rigar ta matse shi mussaman daga gurin hannunwansa kayan sunyi masa cif a jiki kasan cewar sa mutum me kyawun jiki Sam babu rama a jikinsa ko ina a jiki take,da alama yana yawan motsa jikinsa.

Kasa hak'ura nayi a fakaice na kara kallon inda suke shida Alina itama tayi Wanka ta sanja sabbin kaya. Wuyanshi na kallah naga wata siriryar sark'e kamar daimond sai shek'i take hannunshi tsaddadan agogo ne Rolex sai walwali yake, hular shi hana sallah ya juya ta ma'ana gaba ya koma baya- baya ya koma gaba.

A zuciya ta nace kyau babu kyawun hali Allah ya sawake dube shi kamar ba shine ya gama sallah da addu'oi ba amma dubi yanda yayi wata shiga sai kace arne wanda ya futo daga kudu.

Mimi ya kalla fuskar shi babu walwala yace." Ku tashi ku muje." Mimi ta mike Zumbur . yayi gaba be ko kalli inda nake ba. Nima harara na bishi da ita na mike ina gyara zaman hijab

dina,gefe guda kuma ina tunanin k'aryar da zamu sharara a gida, domin ina sane na kashe wayata saboda nasan za'ayi ta damuna da kira bani da amsar bayarwa.

Muna futa bodyguard d'insa na tsaye bakin kofa duk suna sanye da bakaken kaya hannunwan su da safa bak'a kana kallon fuskarsu zaka San babu wasa.

Suka fara kawo gaisuwa gurin ogansu, kallon banza nayi musu nayi gaba Mimi ta biyo bayana Simi-simi.

Doh!-doh ne naga yazo ya wuce ni da sauri yaje ya bud'e wata arniyar mota ba irin ta jiya ba, wannan daga ni ma sabuwa ce kalar ta ruwan zuma ne gaskiya motar ta burge ni.

Tun kafin ya k'araso saboda k'arfin hali irin nawa naje na kama murfin baya zan bude in shiga.

Wata azabbabiyar tsawa doh-doh ya buga mun fa sauri na saki murfin na m ma gefe ina zare ido.

Cike da karsashi ya k'araso ya shiga Alina ta shiga ta zauna kusa dashi, harararta nayi ina jin wani mugun haushin ta. Doh-doh ya maida murfin ya rufe ya zaga da sauri ya shiga  Mazaunin sa.

Rambow ne ya zauna kusa dashi sai Alina sai ni Mimi ce ta k'arshe shiga.

Cike da ladabi Doh- doh yace." Boss ina muka nufa ne."?

Mimi ya d'an kalla da gefen ido yace." Wace unguwa ne."? Baki na rawa tace." Badawa ne wajan giginyu."

Yace." To kaji ko".?

"Yes sir." Doh-doh ya fada yana k'okarin futa daga gidan.

Shiru motar babu wanda ya ce ci kanka gudu kawai take kan kwalta. Ina kallonshi a fakaice, ya makala airphone a kunnenshi sai gyad'a kai yake yana bin wak'ar da yake ji, ba daina najin muryar mawak'iyar daga bakinshi na fahimci janeefar Lopez ce.cikin wak'ar me taken *a into mamah.*

Kalle kalle nake domin in tantace wace anguwa ne muke ciki, *Jambulo* sai yanzu na gane unguwar akwai wata friend dinmu dake unguwar mun tab'a zuwa duba mahaifin wani lokaci da yayi hatsari. Muzo dai-dai kan kwana inda wasu gungun almajirai suke zaune da 'yayansu maza da mata.

A hankali naji yace." Tsaya anan."

Doh-doh ya samu guri yayi parking.  Da sauri shadow ya futo ya bude masa kofa ya futa. Ido na bishi dashi cike da mamaki ganin yana zuwa gurin almajiran nan. Aikuwa suma suna ganinshi suka fara gyarawa

D'aya bayan d'aya ya dinga binsu yana saka musu kudi Wanda ban San adadin su nasan dai 'yan dubu-dubu ne. Duk yawansu sai da suka samu.

Cikin sauri ya dawo motar Shadow ya maida murfin ya rufe muka bar gurin.

Gaskiya ni da Mimi munyi mamaki sosai da sosai da lamarinsa  daga k'arshe muka cigaba da tunanin yadda zata bulle mana a gida.

Kallon shi nake so nayi zuciyata tana hana ni, a sace na d'ago kaina muka had'a ido dashi ta mirror wani miskilin murmushi ya Sakar min yana sosa sumar shi. Na kauda kaina INA jan

k'aramin tsaki, har yanzu da akwai k'ulli a kaina dangane da Alina.

Kwanar gidanmu Mimi ta nunawa Doh-doh nayi saurin dago kaina tare da fad'in." Kai sauke mu nan ma k'arasa da k'afafun mu."

Ina da manufa ta tafad'ar haka.

A hankali motar tayi parking gefen hanya. Na kama murfin motar da sauri zan bude na kasa sai da Shadow ya futo ya bude mana, na futa ina gallah masa harara.

Ido yayi wa Shadow magana naga ya zura kansa ta window motar wani abu ya mik'o masa, yana dagowa naga kud'i daure da kyuare 'yan dubu-dubu.

Shadow ya mik'o min tare da fad'in".Gashi oga yace a baki."

Kud'in na kalla shekeke ina sauri mubar gurin domin nasan halin 'yan unguwar mu abun magana baya yi musu wahala.

Mimi sarki 'yan san kudi ta dinga zungurin kafad'a ta wai in karb'a

Tuni zuciya ta tafara min wasiwasi kan wannan uban kud'in da yace a bani,wato yana nufin ya biya ni kud'in iskancin da yayi min kome oho,me yasa bai bawa Mimi ba.

A tunzure na karb'i kud'in kai tsaye gurin shi na nufa, na zura kaina ta window na motar na cire kyauran dake daure da kud'in.

Kallon juna muke ni dashi, fuskarta babu fara'a na fara zuba masa kud'in a jikinsa tare da fad'in." Wannan kud'in da ka bani basu isa su siye ni ba, baka da abunda zaka yaudare ni dashi, kasani inanan sai nayi maka illah a rayuwar ka tunda ka sake ka shiga rayuwata sai kayi daka sani wallahi."

Da mugun gudu Shadow ya kawo min duka na kifa kaina cikin motar har ina buge goshina. Da sauri na dago Shadow ya daga hannu zai kwada min mari!!!!!!!

"Shadow!!! ".
Ya fad'a cikin wata irin murya wacce ban san shi da ita ba, muryar dai tafi kama da ta Wanda yake cikin tsantsar b'acin rai."!

Shadow!! Ya sauke hannunsa yana wani irin huci!! Jikinsa sai tsuma! Yake.

Ni kuma duk na furgice so nake kawai Shadow ya bani hanya in wuce kar wani Wanda muka sani ya futo daga cikin layin mu."

K'asa-k'asa naji yace." Shigo mota mu tafi." Shadow yayi min wani irin kallo me nuna zamu had'e dake ne watarana ya bude mota ya shiga.

Ina Kallon Alina tana kwashe masa kud'in da na baza a jikinsa sai harararmu take.

Tsaki naja na matsa gefe ina taufar da yawu.

Hannun Mimi na kama muka fara tafiya Mimi bina take simi-simi jikinta DUK yayi sanyi da abunda nake aikata wa.

*Ajiyar zuciya!* kawai yake saukewa zuciyarsa tana masa sak'e-sak'e akan yarinyar tunda yake a rayuwa babu macan da ta tab'a yi masa Abu irin Wanda yarinyar tayi masa.

Sam baya so ya nuna mata hakikanin waye shi baya so ya nuna mata mugunta saboda shi mutum ne me tausayin talaka a duk inda yake ya lura kuma takalawa ne sosai babban abunda ya kashe masa jiki dasu jin abunda d'ayar take fada masa jiya cewar su marayu ne babu uba ya tabbata mahaifiyar su tana fama dasu, amma ya lura sai ya saita yarinyar domin abun nata yayi yawa, yanzu dai tayi na farko tayi na k'arshe kuma sun rabu domin babu ita a rayuwarsa a yanzu amma mutukar ta shigo gonar sa ko Allah zai sake had'a su a wani guri to tabbas zai nuna mata true colour d'insa sai ya gigita mata rayuwa, da wannan tunanin ya cire abunda tayi masa a ransa ya bawa Doh-doh umarnin tafiya.

Cike da tsoro muka lab'e soran wani gida nida Mimi muna shawarar wace irin k'arya zamu girbawa Umammu in muka je gida.

*Meye Asalinsu ne*?

Asalin su shine.............

Zamu had'u dake a pege nagaba
[11/1, 10:55 PM] .: *BABBAN YARO*

mallakar_BINTA UMAR

LITTAFIN MALLAKI NA NE KUN BIYA KUD'IN KARATU NE KAWAI DUK WACCE TASAN ZATA FUTA DASHI WAJE DON GIRMAN ALLAH TAYI MIN MAGANA NA DAWO MATA DA KUDIN TA.

*16*

Malam Sulaiman mai madara shine mahaifin Asma'u d'an Asalin garin kano unguwar k'oki a ka haife shi, su goma sha shida ne gurin iyayensu maza goma mata shida maihaifinsu da mahaifiyar su duk sun rasu ba dadaewa ba, lokacin ma an haifi Asama'u kasancewar dama ba wani arziki ne dasu ba yasa babu wani gado da suka bar musu 'yan uwansu mata duk sunyi aure suna gidajan mazajansu suna sana'oinsu da zaman aure to suma haka take a garesu duk suna da aure da yara ko wanne na buge bugen sa na kasuwanci da aiki yanda zai rufawa kansa asiri, kwata-kwata basu da zumumci ga junansu kowa kansa ya sani da 'yayansa idan ba wani taro ake ba babu me ziyartar d'an uwansa daga matan har mazan duk da cewa 'yayan mutu d'aya ne kowa harkar gabansa yake.

******

Malam Sulaiman yana aiki a company madara ta cowbell wanda yake sharad'a dake ya jima yana aiki sai suka bashi gida a Badawa sai ya bar hayar da yake yana murna ya koma gidan kansa tare da iyalinsa.

Matar shi Mariya 'yar nan makotansu ce sukayi auran soyayya suna da yara hud'u maza biyu mata biyu Hauwa'u itace ta farko tayi aure a giginyu kusa dasu tana da 'yarta d'aya Islam. Aminu shine na biyu yanzu haka yayi diploma da dabara yana so ya cigaba DOMIN ya samu digree babu kudi sai buge-buge yake, Asma'u itace ta uku gurin iyayen ta, ta kasance Mara jin magana me taurin kai tunda ta taso haka take da bushashiyar zuciya ko fada suke da yara bata kuka, tana tsananin kama da mahaifin ta sosai shiyasa yake mutukar kaunar ta duk abunda tayi dai-dai ne

Asma'u tana da kyau na ban mamaki da tsarin jiki me kyau b'aka ce amma ba sosai ba Sam baza a sakata a layin farare ba, tana hanji da manya ido gami da k'aramin baki, tana da yalwar gashi kanta da gira gashin idonta gazar-gazar dasu sun kawata mata ido tana manya nonowa a tsaye k'yam dasu sharp dinta ya futo sosai cikinta a dame yanayin tafiyar ta sauri-sauri yanayin zafin ta da yanayin saurin bakinta domin wata maganar ma in ta fada mutum bazai ji ta saboda saurin bakin ta.

Mimi marainiya ce 'yar k'anwar Mariya ce Umma kenan mahaifiyar su As'amau ta d'auko ta ta shayar da ita tare da Asam'au Mimi ta girmi Asma'u da wata hud'u.babu Wanda zai ce ba Mariya ce ta haife ta ba duk abunda za tayiwa Mimi tare take musu shima Sulaiman ya rike ta amana kamar 'yar cikinsa

Yanzu haka suna da shekaru goma sha shida a duniya matakin karatu kuma sunyi saukar alk'urani me girma, b'angaran boko kuma suna ajin k'arshe a suna jarrabawar futa makarantar da sukeyi ta kudi ce sosai da sosai wan Baban Mimi shine ya tsaya musu dake lecturer ne yana da hanyoyi da dama suna gane karatu sosai da sosai.

Alina 'yar wani hamshak'in me kud'i ne anan unguwar babanta me fada ajine Sam bai damu da abunda 'yayansa suke ba shima sharholiyar sa yake da Matan bariki duk 'yayansa maza ne Alina ce kawai mace shiyasa duk shekara momynta sai ta had'a mata birthday a guri me tsada anyi b'arnar kudi sosai Tuntuni 'yan class d'inmu suke zargin Alina da karuwan ci, nice me

zak'ewa ina cewa k'arya ne tunda basu ganta ba to su daina shedar zurur, Alina tana ji dani sosai a jinmu ganin yanda nake kare ta gurin kawayen mu, masifa ta yasa idan na saka baki sai suyi shiru ita kuma sai ta mik'o min tamfatsetsiyar wayarta k'arar Samsung ina karb'a zan shige karkashin bainci in bude ma'adanar aje video na fara kallon blue film dake tana dasu sosai a wayarta ina fara kallon a jikina zan san ya sanja tsigar jikina ta tashi k'uruciya ban San kome ye ba, zan ta mutsu-mutsu in naji suna nishin nan sai naji idona yana wani irin Abu,, yayin da zanji nonowana suna k'aik'ayi amma don jaraba bazan fasa gani ba, sai nagama zan futo ina matse cinya ta, ranar duk karatun da akayi ya wuce ni haka zan yini sukuku dani.

Mimi Sam bata San me nake kalla ba domin ko da wasa bata lekowa saboda tsoran masifa ta sai zatayi ta damuna da tambayar me yasa taga idona sun kankance sunyi jajazur, kawai zan ce Mata kaina ne yake ciwo shikkenan sai ta bar maganar

Muna komawa gida nake zubewa kan katifarmu in ta murk'ususu ina jin wani fleengs Wanda ban san ko menene ba, sai in kwana in yini kafin in samu sassauci amma fa sa'i da lokaci marata zatayi ta daurewa ban san KO menene ba, haka Umammu zata gaji da tambaya ta tayi shiru ta k'yaleni.

Tunda na gano kallon blue film din nan ne yake saka ni shiga irin wannan halin sai na daina in Alina ta bani wayarta ko da wasa bana bude video sai dai in kalli hotuna in wuce zatayi ta damuna da cewar ki shiga video akwai sabbi sunyi sosai zasu d'ebe miki kewa, masifa nake mata ince na daina kallo ita taje tayi tayi tunda baza ta daina ba. Sai tayi min Dariya kawai ta bar maganar saboda tasan halina.

Mota ce ta banke mahaifin mu yayin da yake kan mashin d'insa ya Bari gurin aiki da niyar komawa gida take a mutu ko shurawa baiyi ba, mun shiga rud'u da tashin hankalin rasuwar Babanmu nayi kuka kamar babu gobe kasan cewar nasan shine jigonmu madogararmu ni da 'yan uwana Yaya Aminu bashi da k'arfi Asalima buge-buge yake na makaranta Aunty Hauwa'u kuma mijinta bashi da k'arfi itama 'yan sana'oi take a gidanta tana rufawa kanta asiri.

Kun San dai yanda Aikin company yake baka da fansho balle garatuti farin cikinmu guda shine gidan da muke ciki Company ya mallakawa Babanmu ta kardun ma suna hannunsa bamu da fargar wannan.

Tunda 'yan uwan Babanmu sukayi mana taimako na marmari sai kowa yaja zugarsa suka gudu suka barmu da wahalar mu,

Inda Allah ya taimake mu ma abokan aikin Babanmu lokacin da suka zo. Gaisuwa sun bamu kudi sosai har da masu kayan abunci fa sutturu shine muka rufa kanmu asiri

Ummamu da Aunty Hauwa suka fara harkoki da sauran kud'in da sukayi mana saura a hannu Inda Aunty Hauwa take shiga kasuwar kwari tayi sare sare na atamfofi mayafai da takama tazo ta raba cikin unguwar su, ita kuma Umammu ta fara sana'ar siye da siyarwa na cikin gida kamar su mai kalanzir gwayi bussasun kayan miya da ice da sauransu, da wannan muka dogara Yaya Aminu ya dage yana ta karatu inda k'aramin kaninmu me bina kenan Mussad'iq yake k'aramar makaranta zasu jarrabawar futa.

*Wannan shine tak'aiaccan tarihin Asma'u*

*Cigaban labari*

Mimi tace." Anya Asma'u shawarar da kika fada tayi kuwa wallahi ba lalle ne aunty Hauwa ta yarda ba kin San halinta."

Nace muje muyi wannan k'aryar zanje gurin SQ in karb'i kati bashi in sa a wayata zan bugawa aunty in lallab'ata ko tazo gida tace hakane."

Mimi ta gyda kai kurrum tace." Shikkenan muje Allah yasa kar Ummamu tayi fushi wallahi tausayin ta nake ji."

Nace." Nasan yanda zanyi da ita kawai kiyi addu'a kar Allah yasa Ya Aminu baya nan kin san halin masifarsa ko Ummamu ta hak'ura zai iya tun zurata."

Mimi tace." Hakane to Allah yasa muje mu tarar ya tafi makaranta." Nace." Amin dai.

Muka futo a tsane ke muka doshi kofar gidanmu yara na shiga wasu na futowa masu siyayya kasan cewar safiya ce yanzu.

Umammu na zaune a kujera 'yar tsuguno tana durawa wata yarinya kalanzir cikin wata kwalba mukayi sallama muka shiga.

Amsawa tayi ba tare da ta dago kai ta kalle mu ba ta sallami yarinyar ta futa muka k'arasa kusa da ita Tare da zama kan tabarma da ke shimfide a tsakar gidan

Nace." Ummam..... Dago min hannu tayi Tare da fadin ." dakata!" Shiru mukayi gabanmu na fad'uwa ni da Mimi tace." Daga gidan ubanwa kuku a ina kuma kuka kwana."

Tuni na sanja shawarar k'aryar da muka shirya bakina na rawa nace." Daga gidan Kawu Yunusa mike."

Cike da mamaki take kallona tace." Me ya kaiku gidansa bana son k'arya fa."?

Nace." Ummamu ki yarda damu wallahi daga gidan sa muke kuma anan muka kwana ai kin San wannan kawar tamu Alina ta bayan layin nan 'yar gidan Alhaji Santana ko."

Umammu tace." Na santa mana me ya hadaku da ita mara tarbiyar yarinya."

Mimi tayi sauri tace." Umammu kiyi yafe mu jiya munyi miki k'arya zamuje gidan aunty Hauwa wallahi ba can muka je ba Alina ce ta gayyace mu birthday dinta shine muka je can."

Salati Umma tasa tace." Kuka je birthday din Alina abunda naji ana cewa ba acikin gari ake yin sa futa ake akama guri 'yan iska su taru a gurin so kuke Ku jawo min abun magana a gari ni Mariyatu."
Ta k'arashe maganar cike da takaici.

Nace." Kiyi hakuri Umma wallahi munyi kuskure ."

Tace." Rufe min baki ko i n buge shi don ubanki nasan wannan kaidin duk daga gurin ki ya futo Mimi baza ta aikata haka ba."

Shiru mukayi. Cike fa tsoron tashin hankalin da muka hango a idon Umma ta cigaba da cewa " zaku fada min inda kuka kwana ko sai na saka Aminu yaci ubanku

Baki na rawa nace." Gidan Kawu Yunusa ne ki buga waya ma ki tambaya kiji."

Na fad'i hakane saboda nasan bazata buga wayar ba saboda basa shiri dashi wan Babanmu ne shi Kawu Yunusa.

Tace." Me ya kaiku gidan sa mutumin da ya manta daku a duniyar nan ai babu abunda zancewa Yunusa ya hofintar da zuri'ar Dan uwansa.

Nace." Wallahi Umma muna futowa daga gurin da akayi birthday din muna tsaye gefen titi muna neman mota kawai sai motar. Ya Musa tayi parking yace." Mu shigo ya kaimu gida, ganin dare yayi yasa yace bari ya wuce damu gidansu in yaso ma tawo gida da safe.'

Tace." Ai ya kyauta kuwa wallahi Wallahi duk sanda kuka kara zuwa birthday din Alina sai nayi muku Allah ya Isa, yarinyar nan fa ina jin abunda jama'ar gari suke fada akanta."

Nace." Kiyi hakuri Umammu baza mu sake ba."

Fada take sosai mu kuma muna bata hakuri da k'yar muka samu ta hak'ura muka mike tare muka shiga dakinmu muna sauke ajiyar zuciya.

********

Wani katafaran Company nake hangowa daga sama an rubuta *Amjadu Abul Abbas Mai Materials* Company ni ne shaharare wanda yayi suna a jahar Kano dama kewayen ta Company yayi suna sosai gurin yin kaya masu sauk'i da k'arko da rahusa *Amjadu Abul Abbas Company* Mutane daga ko wace jaha suna zuwa domin su sari kaya kama daga kayan sawa atampa lesuka materil takalma mayafai dogwayen riguna hijab da sauran su.

Wannan Company mallakin *Amjadu ne young miloniar* yana d'auke da ma'aikata k'warori da bak'ak'en fata har da chanis ma suna aiki cikin wannan shararan company.

*15/October/ 2009*
[11/1, 10:55 PM] .: *BABBAN YARO*

mallakar_BINTA UMAR

LITTAFIN MALLAKI NA NE KUN BIYA KUD'IN KARATU NE KAWAI DUK WACCE TASAN ZATA FUTA DASHI WAJE DON GIRMAN ALLAH TAYI MIN MAGANA NA DAWO MATA DA KUDIN TA.

*17*

A hankali motar ta shiga harabar Company, ma'aikatan dake gurin suka mik'e tsaye masu aiki suka bar aikin nasu suka mik'e dukaninsu suna sanye da uniporm Riga da wando purple maza da mata kenan matan sun mak'ala guntun hijab fari a wuyansu amma suma duk wando ne a jikinsu musulmai kenan su kuwa sauran babu ruwansu da sa hijabi sun sha uban kitso na

attachment wasu kuwa ita suka saka suka baza a kafad'ar su ga uban  farce zak'ok'o  a hannunwan su.

Ya futowa suka dinga sunkuyar da kai k'asa suna gaidashi masu turanci suyi masu Hausa suyi, cike da ginshira yake amsa musu yana d'aga musu hannu, ya shige ciki inda office d'insa yake. Bodyguard d'insa suka rufa masa baya.

Manager na zaune a office dinshi ya ga shugowar Oga  ta cikin CCTV Camara, a fili yace ." madugo uban tafiya kenan yayi mamaki yake sosai yanda yayi musu zuwan bazata babu shakka akwai abunda ya kawo shi. Aikuwa bai gama tunin shi yaji shigowar kira a wayar sa.

Da sauri ya d'auka tare da fadin." Ranka ya dad'e barka da Safiya."

Yana juyi cikin wata hamshak'iyar kujera dake ofis d'insa yace." Barka Ka zo yanzu ina Neman ka."

Cikin fad'uwar gaba Manager yace." Ok Sir ganinan zuwa."

Aje wayar yayi ba tare da yace komai. Da sauri sakataren sa dake tsaye a dauki wayar ya kashe.

A hankali yace." Joy baku sauka daka kan tsarina ba,? Kar ku bana zuwa gurin nan Ku karya min dokata."
Da turanci yayi wannan maganar.

Joy  yace."  yes sir munanan kan tsarin ka a yanda na sani duk abunda kafad'a gurin meeting da mukayi bamu tsalla ke ba."?

"Are you sure."?
Ya tambaye shi yana girgiza k'afa.Joy yayi k'asa da kansa tare da fad'in." Yes sir."!

Girgiza kafadarsa yake yana jiran zuwan Manager sai gashi ya shigo cikin sallama ya zauna cikin kujera  suka gaisa a tsanake *Amjad*

Manager yace." Yallab'ai kayi mana zuwan bazata fa."

Murmushi yayi yana shafa kwantaccan sajen shi yace." Na biyo ta gurin ne yasa nazo duba Ku hope komai na tafiya dai-dai bana fatan a samu matsala ina fatan komai dana fada baku rusa shi ba."

Cike da ladabi Manager yace." Munanan kan maganar ko Yallab'ai komai yana tafiya yadda ya kamata ana samun cigaba ta ko wane guri sai dai fatan nasara da karuwar arziki kuma jama'a daga ko wace jaha suna murna da wannan sauk'i da suka samu tare da yi maka fatan alkairi gami da fatan nasara a rayuwa da yiwa iyaye addu'a samun rahama gurin ubangiji."

Muryar shi mai d'auke da amo da sauti ita yayi amfani da ita gurin fad'ar " Alhmdullahi har kullum abunda nake fata kenan naga d'an kasuwa yana walwala da farin ciki mussaman kananu Wanda basu da jari sosai ina mutukar son in tallafa musu sosai saboda haka Ku cigaba da abunda nace muku ,mutukar na samu wani ma'aikaci ya karya min dokata ta kara farashin kayana ba akan yanda na bari to babu shakka sai ya d'and'ana kud'ansa tare da azaba me tsanani akan abunda ya aikata."

Menagar yace." In Allah ya yarda hakan baza ta faruwa ba Yallab'ai."

Daga kai kurrum yayi da hannu yayi musu alama su tafi.

Suka futa suna godiya.

Doh!_doh da Rambow na tsaye a bakin kofar ofis din suna zazzare ido.!

Manager da skatare suka futo kowa ya koma bakin aikinsa.

Juyi yake cikin kujera tare da shafa gashin dake kewaye a fuskarsa da alama ya saba da haka, tunanin abunda ya faru yake shida marakunyar yarinyar nan, ya mutukar mamakin tsaurin idonta tunda ya shiga gurin birthday din Alina idonshi ya sauka a kanta suna tsaye ita da 'yar uwarta, tsarin rayuwarsa bai cika kallon mace ba shi dai tsakaninsa dasu shine idan sha'awar sa ta motsa ya nemi wacce tayi masa ya biya bukatar sa kuma baya tab'a neman wacce tasan namiji viginal yake nema wacce shi yake fara bude gurin, in yayi sex da mace sau daya baya

k'arawa shi kanshi bai San iya adadin matan da yayi sex da su, shekaru biyu kenan da fad'awar shi wannan harkar saboda wani dalili wanda shi kad'ai ne ya sanshi sai ubangjin shi.

Kwata-kwata *Amjad* bashi da jaraba son yin sex domin sai ya dauki satittika ma baiyi ba ammafa gurin romancing shine kan gaba yana bala'in son yaga ana tsotsar sa ko ina shiyasa yakan jima bai yi sexcual da mace ba, sai dai idan ya karanci mace ya fuskanci zatayi Sugar nan zayi.

Tunda yaga Asma'u jiya yaji yana sha'awar sex da ita, ganin yarinyar tar ta yasa ya cire abun daga ransa domin yana ganin kamar baza ta iya d'aukar shi ba.

Abunda ya tun zura shi game da ita tsabar tsagerancin ta gami da tsaurin idonta shine ya fara koya mata hankali tun a gurin birthday din sai ya lura kamar tunzurata yake, dalili kenan ya d'auke su ya kaisu gidansa ba da niyar yayi raping dinta kawai zaiyi romancing ne ya rage zafi, da ita sosai ya lura yarinyar tana da Quality sosai yana bukatar mace jaruma ya lura sha'awar ta a kusa take, shine dalili kawai da yakasa biye mata da ya biya bukatar sa ya mike ya barta don ya lura irinsu Romacing baya d'aukar su dole sai an shige su.

Gyad'a kansa yake yana d'an cije lips d'insa na k'asa tunda take a rayuwa babu wata 'ya mace da ta tab'a yi masa irin abunda yarinyar ta yi masa, ta kwance kudi ta watsa masa saboda tsabar bata da mutumci tana tashan balaga, sosai ransa ya b'aci d'azu zuciyar musulunci ne kawai tasa ya k'yaleta lura da yayi bata da wani galihu ko ga yanayin unguwar tasu ma da ya gani kuma yaji daga bakin 'yar uwarta cewar marayu ne shine kawai ya k'yaleta a d'azu, wannan ya wuce mutukar ta kuskura ta k'ara aikata masa wani Abu makamanci Wanda take masa tabbas zata karb'i hukunci ko ina ne ta ganshi ta nuna tasan shi ta kawo masa shirmen ta to tabbas sai yaga da wanda take tak'am zaiyi mata horo me tsanani wanda zata zo tana kuka da hawayen ta tana bashi hakuri.

Da wannan tunanin ya rufe babin Asma'u a ransa domin baya saka damuwa cikin zuciyar sa ko kankani.

Mik'ewa yayi ya d'ibi wayoyinsa ya futa duka Wanda suke gurin suka mike suna masa a sauka lafiya b'aki kuma da suka shigo company suna so su gaisa dashi babu lokaci kawai ya daga musu hannu ne ya wuce. Bodyguard d'insa na take masa baya.

*15/October/2009*
[11/1, 10:55 PM] .: *BABBAN YARO*

mallakar_BINTA UMAR

LITTAFIN MALLAKI NA NE KUN BIYA KUD'IN KARATU NE KAWAI DUK WACCE TASAN ZATA FUTA DASHI WAJE DON GIRMAN ALLAH TAYI MIN MAGANA NA DAWO MATA DA KUDIN TA.

Whasap numbar
07084653262
08089965176

Account numbar
1013851874
Ahamad gwadabe
UBA BANK

*18*

Tsakiyar dakin Mimi ta tsaya ta rik'e k'ungunta tana sauke ajiyar zuciya tace." Wallahi ban zaci

abun xai zo mana da sauk'i haka ba. Mik'ewa nayi zaune ina cire hijab din dake jikina nace." Wallahi nima haka Mimi Allah ne kawai ya taimake mu Yaya Aminu bayan da munga tujara dan sai Yaya Musa ya tambaye shi ko Dan ya kure mu."

Mimi tasa dariya tana bin jikina da kallo tace." Wai a ina kika samu wannan muguwar rigar kika saka kinga yanda tayi miki mugun kyau kuwa,tun d'azu nake so in tambaye ki tashin hankalin da muke ciki ya hana. Tab'e bakina nayi nace.' Ke a ina kike tunanin zan samu kayan gurin wancan guy ne fa, shine ya bani rigata Kin san ta yage." Mimi tazo ta zauna kusa dani gami da zuba min ido.nace." wannan kallon fa malama."

"Asma'u amma dai baiyi miki komai ko." ? Mik'ewa nayi ina shirin tub'e rigar nace." Jeki tambaye shi sai ya baki amsa.' Kallo tabi ni dashi tace." Wallahi gwara kuwa ki cire rigar tun kafin Umma ta Ankara da ita." Nace." Nima dama tunanin da nake kenan.

Mimi ta cigaba da cewa." Gaskiya Asma'u kinyi nisa da tsaurin ido kamar wannan kikayi wa iskanci gaskiya banji dad'i ba ko banza ya taimake mu tunda ya kaimu gidansa muka kwana kinsan da sai dai mu kwana a hanya Wallahi yanda motoci suke wahala in dare yayi.

Tsaki naja nace." Don Allah ja can gefe guda,waye ya fada miki irin wannan mazan ana musu da sauk'i, Bari kiji kudinsa ko kyauwunsa wallahi bazai hanani in yaga shi ba, domin nima rigar mutum ci na ya keta min gaban idanun mutane ko Baki ga abunda yayi min bane."

Mimi ta sauke ajiyar zuciya tare da fadin ." na gani mana ai kece kika jawo wa kanki saboda kaifin harshen ki, don Allah ki kula Ku sake haduwa mukayi dashi babu ruwanki dashi." Shashan kallon na watsa mata nace." Yo meye dama alak'ata dashi da har kike fatan sake had'u war mu dashi, rigar shi CE dai gata zan sanya cikin Leda in aje DOMIN ta gama min amfani duk inda na ganshi in bashi kayansa."

"Lallai ma Asma Mimi tafad'a cike da mamakin abunda nace ta cigaba da cewa." Nima fada kawai nake nasan babu a inda za mu kara ganinsa domin yayi mana nisa dalilin birthday din Alina ne ma yasa muka ganshi amma na Dade da jin sunansa na yawo a gari. Tab'e baki nayi nace." Mimi ke kika damu dashi da har kika fahimci sunansa na yawo a gari ni kam wanka zanyi ki k'yaleni da zancan guy nan haka."

Mimi ta kwanta kan katifa tana lumshe idonta tare da tunano sifar Amjad kyawunsa yana burgeta haka kurrum take jin wani abu a zuciyarta a game dashi. Soso da sabulu na d'auka na

nufi band'akin mu dake tsakar gida domin inyi Wanka, ina jawo ruwa cikin rijiya Aunty Hauwa tayi sallama ta shigo hannuta rike da yarinyar ta Islam daya hannun kuma wata katuwar Leda ce ta shigo da kallonta nayi naga tana cikin farin ciki. Gefan tabarma ta zauna kusa da Umma wacce take d'aurin gishiri,suka fara gaisawa nace." Aunty Hauwa wai ke don Allah bakya gajiya da tafiya ne, sai kace ma'aikaciya yau in baki zo ba gobe sai kin zo hana don Allah."!!! A harzuk'e tace." Wallahi zan zo in ci ubanki Anan gurin ni sa'ar ki ce na shigo gida babu sannu bare gaisuwa kin zo kina min shirmen banza da wofi." Dariya nayi nace."Allah ya baki hakuri bari nayi Wanka sai inzo mu gaisa a tsanake ." k'wafa tayi kawai ta juwa suka cigaba da magana da Umma wacce take cewa." Kece kika biye mata ma Asma'u Wanda be San halinta ba sai ta sashi hawan jini." Aunty Hauwa tace." K'yaleni da ita Umma wallahi ta jawo wa kanta bazan bata mayafin ba Mimi ce zata dauki daya kema ki d'auka nima na d'auka ita ko ta jawowa kanta tunda tana ganin Neman kud'in da nake yawo ne, ko mijina be hanani ba sai ita me bakin magana."

Cike da farin ciki Umma ta jawo ledar tana zazzage kayan ciki. Mayafai ne da dogayan riguna sabbin shigowa sunyi bala'in haduwa sai walwali suke ko ina stones a jiki anyi musu ado wasu shipom wasu kashka ne masu taushi.

Umma tace." Wannan mayafan sabibin zuwa ne da alama."?
"Wallahi kuwa Umma yanzu daga kasuwa nake naje d'aya daga cikin kantinan Mudansir And brothrs kawai naga suna sauke kaya, kasancewar mun saba dasu saboda INA zuwa sari yasa suka bani kaya akan yanda suka sauke Wallahi naji d'adi yanzu zan cire abunda yayi saura a account dina in basu in yaso in nagama had'a kud'in sai in cika musu sauran." Umma tace." Aikuwa haka yayi wallahi kice yanzu zamu fara kasuwan ci da karfin gwiwa ko." Cike da farin ciki Aunty Hauwa tace." K'warai kuwa Umma ai naji dadin abunda sukayi min wallahi. Kinga ko bani da ko kwabo zasu bani kaya in juya in kawo musu kud'in." Umma tace." Allah yayi musu albarka ubangiji Allah ya daukaka Mudansir a duk inda yake." Aunty Hauwa tace." Ameen ya rabbi ammafa Umma bashi kadai zamuyi wa addu'a ba." Umma tace." Auwo!! Dawa kuma."? Dariya tayi tace." Akwai mutumin da naji suna zancan sa wai sunanshi *Amjad* ya bude sabon company a wajan gidan governor can wajan magwan, ya zuba ma'aikata sosai fararan fata da bakake fata, can suka samo kaya masu kyau da arha suna ta murna sun huta futa Dubai da sauran kasashe kawo kaya,DOMIN kayan da company suke har yafi na wata wata kasar wajen ma kyau da karko."

Umma tace." Kai wannan kuwa Allah yayi masa albarka wallahi yanzu 'yan kasuwa zasu fara walwala da NISHAD'I."
Aunty Hauwa tace." Wallahi nima haka nace sunan company *Amjadu Abul Abbas Matireals."!* dai-dai lokacin da aunty hauwa take fad'ar wannan ni kuma lokacin na futa daga ban daki kenan , abun sabulun dake hannuna ya kusa fad'uwa nayi saurin rike shi gabana na fad'uwa jin sunan da aunty Hauwa take fada..........kallon bakin ta kawai nake lokacin da take zayyanowa Umma

mutumci da karamcin Amjadu me company sai da naji tana cewa kuma ance yaro ne karami ko matar aure bashi dashi nan na kara tabbatar wa da cewar guy nan ne domin dai ni tunda nake ban tab'a jin suna irin nasa ba *Amjadu* Hararata aunty Hauwa take nazo na wuce ina kunshe dariya don nasan abunda nayi mata d'azu take wa, nace." Bari inzo in karb'i nawa mayafin." Ko kallona ba tayi ba ta cigaba da maganar ta. Mimi na samu kwance har yanzu idanunta a lumshe. Nace."Mimi ki tashi ga aunt can tazo ta kawo mana mayafai." A hankali ta bude idonta na kalle ta cike da mamaki nace." Badai bacci zakiyi ba."? Tace." Wallahi shi zanyi jiya fa banyi wani baccin kirki ba."

"Humm ai ba k'aramin cin zalinmu guy nan yayi ba ni kaina baccin nake ji.' Na fada INA k'okarin ciro kaya cikin akwatuna.

Mimi ta mike ta futa ni kuma na sanya riga da siket na atamfa nicham na saka kudusdusar wayata a chaji na bi bayan Mimi. Zama nayi kusa da aunty Hauwa na jawo ledar ta janye abarta tana hararata nace." Haba big aunt meye duniyar kiyi hakuri wallahi wancan purple din mayafin yamin kyau ki bani shi." Tace." Ai kinyi wa kanki sai dai kiga ana yi." Marairaicewa nayi na jawo Isilam nace." Babyna cewa momyn ki tayi hakuri ta bani gyale guda d'aya." Aikuwa Islam ta jawo mayafin da Mamanta ta kwace a hannuna ta mik'o min na mike da sauri zan gudu aunty ta rike min kafafuna wai Dole sai bata mayafin ni kuma naki saki.

Yaya Musa ne yayi sallama ya shigi gidan ganin abunda yake faruwa ne yasa yace." Ke Hauwa anyi babbar kwabo sakar mata k'afafu kar ki k'arya ta na wane kud'in mayafin naki sai a sai mata." Dake sun saba wasa a tsakanisu tace." E a sai mata mana don ni nayi rantsuwar bazan bata ba." Yaya Musa ya zauna Tar da zura hannunsa cikin aljuhu ya futo da kudi yana fadin ." am ce miki ki sake ta ki fad'i kud'in gyalan naki." Hannu ta mika masa tana fad'in." Kud'in gyale dubu hudu ne da Dari biyar." Da sauri nace." Yaya Musa kar ka bata Dari biyar din kai ka nemi ragi ita ta Dora akan dubu hudin ribar ta CE."
Dariya Yaya Musa yayi yace." Kina hannu amma kina surutu ko ki bari in fanshe ki a hannunta. " aunt tace." Rabu da ita dai." Dubu biyar ya mik'a mata ta karb'a sannan ta sake ni, babu kunya ta zura kud'in cikin purse dinta.

Yaya Musa yace." Ke kam son kudin ki yayi miki yawa Wallahi. " dariya aunt tasa tace." Yo waye yak'i kudi ko dangote kullum cikin nema yake bare ni gallafiri me naiman na koko." Dariya kawai Musa yake, sai da yayi me isar sa sannan ya juya yana gaida Umma cikin girmamawa suka gaisa tana tambayar sa mutan gidan yace." Kowa lafiya. Kusa dashi na zauna gabana na fad'uwa domin ina jin tsoro kar ya fadawa cewar ba a gudansu muka kwana ba Gashi munyi wa Umma k'arya.Ashe Mimi ma tunanin da take kenan muka kalli juna gabanmu na fad'uwa

Umma tace." Yau kazo gaishe mu kenan." Sunkuyar da kansa kasa yayi yana murmushi yace." Nazo gurin Asamau ne,." Umma da aunt sun gane munufar sa, oho!! Ni San ban fahimci wai

sona yake ba. Jin abunda yace ne yasa Umma ta tashi ta shige kuryar daki cike fa kunya, aunty ma ta mik'e ta bita tana murmushi. Muka kadai ne mukayi shaura, INA kallon Mimi ta sauke ajiyar zuciya nasan ko ta mecece nasa dariya ina fadin. " kura sarkin tsoro kenan. " hararata tayi ta mike tana niyar fucewa tare da fadin "Masoya asha soyayya lafiya " kallo na bita dashi cike da mamakin abunda tace." Naji muryar Yaya Musa yana cewa. " ke Asma'u akwai Wanda ya kaiki tsoro kuwa."? Juyowa nayi ina kallonsa na gyara yanayin fuskata sosai cikin zuciyata nace kardai abunda Mimi tafad'a gaskiya Musa sona yake lallai ma kuwa. Nace." Ya Musa ni nan da ka ganni kafin kaga abunda ya furgita ni zaka jima." Ya kyalkyale da dariya kamar wani soko yana gyara zama yace." Allah tawan.". ? Allah tawan." Na maimaita a abunda ya fada a zuciya lallai wannan bashi da hankali yo ko maza sun kare a duniya ni me zanci dashi tabd'ijam ! Ya wani gyara zama yana kashe min ido tare da fad'in." Asma'u zauna sosai zamuyi magana dake ta fahimta. " nace." Ai a zaune nake Yaya Musa." Murmushi yayi min yace." Hak'ika Asma'u zuciya ta kamu da so da kaunar ki tun kina 'yar k'arama nake sonki ina fatan zaki amunce mun muyi auran zumunci domin raya sinnar Annabi MUHAMMADU ." nace slw." Yace." To kinji abunda yake tafe dani gurin ki.Murmushi nayi me kunshe da abubuwa da dama nace." Yaya Musa kenan,a gaskiya bazan munafurce ka ba, bani da ra'ayin auran zumunci a rayuwata kawai dai zan cigaba da yi maka fatan samun mace wacce ta fini na gode da so da kauna." Jiki a sanyaye yake kallona bakinsa na rawa na lura magana yake so yayi amma ya kasa. Mik'ewa nayi nace." Kar kace na wukalanta ka ni na shiga ciki." Kallo ya bini dashi cike da mamaki har na futa. Ya Dade zaune a gurin yana tunanin Asma'u yanzu shi ta kalli tsabar idonsa tace bata sonsa lallai ko taso ko taki sai ya aure ta zai gwada mata iko tabbas ruwa ba sa'an kwando bane." Haka ya mike ya bar gidan ba tare da yayiwa kowa sallama ba.

Ina shiga dakin mu na tadda Mimi na ninke kayanta ta dago ta kalle ni tare da fadin." Har kun gama soyayyar." Duka na kai mata ta goce tana Dariya . kan katifa na zube ina Jan tsaki nace." Wallahi wannan musan ya ma rainawa kansa hankali duk 'yan matan dake cikin birnin Kano ya rasa wacce zai ce yana so sai ni,wallahi ji nayi kamar in mangare shi Dan haushi." Mimi ta dinga dariya tace."To shi ke ya hango saboda haka ki bashi hadin kai kawai musha buki." Wani dukan na kaima ta raina a bace, yanzu na samu nasarar samunta a kafad'a ta rike gurin tana kallona da baki a bude, ta bude baki kenan zatayi magana na katseta ta hanyar cewa." Sallah!rufe min baki,sai dai idan kece zaki aure shi wallahi ni me zanyi DASHI yana tafiya salo-salo da kafad'u a sauke hummmm! Wannan auran sa ai takaici ne wallahi."

Mimi ta kwanta tana sheka Dariya fad'i take." Asma'u baki da kirki wallahi gaskiya kin yanki Yaya Musa santalelen saurayi haka mijin mata hudu kikewa wannan cin mutum cin." Nace." Wallahi da gaske nake wannan ya kuskura yayi mata hudu guduwa zasuyi su barshi wai baki ga yanayin sa bane babu wani kuzari da karsashi komai salo salo."

Mimi ta gyara zama tana kallona tace." Nifa ban fahimci inda kika dosa ba."? Nace." Yaya Musa bazai yi wani k'arfin kirki ba gurin sex." Mimi ta saka salati tana kallona a tsorace tace." Ke yaya akai kika sani ke ba bazawara balle kice kin San namiji."

Tsaka naja tare da fadin " ke k'yaleni don Allah DUK da nake budurwa ina gane maza wallahi masu jarumta da ragwaye Bari in miki misali da guy nan na jiya wannan shi kana ganinshi kaga jarumi a komai ma, misali kawai namiki dashi shi kuwa Yaya Musa ai sai a slow daka gani. Lumshe ido naga Mimi nayi nace." Ke meye haka kikayi."? Bude idonta tayi tace." Wallahi Asama ban san me yasa ba idan na tuna wannan guy some times sai inji gabana yana fad'uwa ina jin tsigar jikina na tashi wallahi yanzu ma da kika ambace shi haka naji." Wata irin faduwar ga bace ta rikito min tuni naji miyau din bakina ya tsinke bakina ya zama lami babu tes ko na kwabo dake ina da b'oye abu sai nayi saurin aro jarumta na aza a raina na kalli Mimi murya a dage nace." Ko sonshi kike ne.?"

Cike da rashin madafa Mimi tace." Ban sani ba Asma." Tab'e bakina nayi nace." Wannan dai duk alamar so ce da kika fada." Kwanciya tayi kan katifa tana lumshe ido naji kamar in make ta don haushi!! Nace." Ki daina wahalar da kanki kuma kar ki saka abunda kika san baza ki samu ba cikin ranki kin San dai wannan guy yayi miki nisa nesa ba kusa ba, kudi kyau mulki bayan wannan kuma duk wata mace tana so ta samarwa 'yayanta uba nagari kin San wannan kuwa mugun d'an iska ne gwara ki cire shi a ranki."

Tashi zaune tayi na kalli fuskarta naga ta sauya lokaci guda nima na sauya tawa tace." Haba Asma'u ki daina CE masa Dan iska, ita shiriya ta Allah ce wallahi bakiji yanda naji a zuciya ta ba da kika kirashi haka insha Allahu Zai dawo hanya madaidaiciya." Nace." Ke dai so ya rufe miki ido kawai kin kasa gano abunda ake so ki gano irin wad'annan 'yan barikin basa tab'a daina halinsu."

 *Amjadu* ya mik'e tsaye da sauri tare da daga masa hannu fuska a murtuke yace." Duk wani Abu da kasan mallakin mahaifina ne ina bukatar ka hado ka kawo min har gida, nasan iya adadin dukiyar mahaifina dake hannunka saboda haka mutukar kana son zaman lafiya ka zare dukiyar ka domin bana bukatar ta a cikin tawa ina fatan ga gane." Mai citta ya saki baki yana kallonsa cike da mamaki tabd'ijam ai abunda bazai yiwu bane ya fada a zuciyarsa, kwantar da muryarsa yayi zai rarrashe shi *Amjad* ya daka masa tsawa tare da fad'in " INA da labarin b'arnar da kake kan dukiyar saboda haka babu abunda zaka CE min na baka daga nan zuwa dare ka hado takkadu ka kawo min ko in sanya a rufe shagunan kowa ya huta."

Yana gama maganar sa ya fuce cikin zafin nama!

Me citta ya bishi da kallo gumi na tsiyaya a jikinsa yaran kanti suka fara murna domin zalintarsu kawai yakeyi zama yayi kan kujerar da Amjad din ya tashi yana jan numfashi, Zumbur!!! Ya mike ya futa kamar mahaukaci ya  motarsa ya shige ya zauna tare da d'auko wayarsa wasu 'yan daba ya kira da suke wata unguwa da tashahara a birnin kano sun kware gurin daba da sare kan mutane take ya fada musu abunda zasuyi masa,ya basu address din gidan Alhaji Abbas Wanda yanzu ya zama mallakin Amjadu.

Dari misalin sha biyu yana zaune harabar gidan shi kadai  da karan sigari a hannunshi yana zuka zuciyarsa na saka masa yanda zaiyi da Mai citta kawai yaga suna haurowa daga sama DUK da security da aka keyawe gurin dashi.Mik'ewa yayi a nutse *Amjad* Jarumi ne sosai babu abunda yake furgita shi can yaga sun nufa bayan window din dakunansu suna zazzaga fetur, cikin zafin nama ya tafi da gudu ya sanya gwiwar hannusa guda ya daki kan d'aya tare da tad'o k'afar d'ayan suka zube a gurin suna nishi! Da hannu daya ya dunga Kansu har ya kaisu aininhin main parlor ya zauna kan kujera fuskarsa a murtuke yace." Waye ya aiko Ku."?

Ganin yanda muscle d'insa suke motsi sai abun ya basu tsoro suka nemi jarumantar su suka rasa baki na rawa daya daga cikinsu yace." Me citta!!!!! Ne ya aiko mu mu kone gidan gaba daya yayi mana alk'awarin kudi har miliyan biyar biyar."!

Murmushi yayi murya a sama yace". Gud"!! Alhaji Hashimu me citta!!!!? D'ayan yace." Yes sir." Gyad'a kai yayi ya mike a zafafe! Ya daki bango ! Yakai  ya kawo Cikin razananniyar tsawa yace." Meye sunayen Ku."?

Hada baki suka yi

Ma'aruf Amma ana kirana da "Rambow"

D'ayan yace." Ni kuma Nasiru amma ana kirana da Doh-doh". Gyad'a kai yayi yace." Meye Matsalar Ku a rayuwa."?

Sukayi shiru yace." Baku da aiki sai kisan kai wato an turo Ku Ku kashe ni ko."?

Sukayi shiru. Tsawa ya buga musu tare da sake fadin." Meye Matsalar Ku a rayuwa ina tambayarku." Suka hada baki gurin fadin." KUDI ne sir."

"Very Gud"!! Yafad'a da k'arfi. Mik'ewa yayi ya durfafi d'akinsa sai gashi ya futo da d'aurin KUDI da yawa a hannusa ya watsa musu a jiki gami da fadin " gasu nan.

Cike da tsoro suke bin kud'in da ya watse a kasa kunya ta rufe su
suka sunkyar da Kansu kasa suna bashi hakuri zama yayi cikin kujera yana kallonsu mazaje sosai amma babu Sanar yi yace ." Ku bani takaitaccan tarihin Ku."

A takaice suka gabatar masa da Kansu yace." Zan d'auke Ku aiki zaku zama yarana INA fatan babu matsala, Har kusan kuka sukayi saboda farin ciki Ashe alheri ne ya shigo dasu gidan,lallai idan Allah yaso ka da alkairi babu mahalukin da ya iyasa ya hana, a takaice dai nan suka kwana. Da safe *Amjad* yasa suka kimtsa sosai suka shiga mota kai tsaye babu inda suka nufa sai court nan *Amjad* ya shigar da kara a ka karbo sammaci su ya sanya suka kai ma me citta har cikin kasuwa Wanda yake zaune yana jiran tsammani yaji labarin daga su Rambow kawai yaga sun mik'a masa takkada daga hair court kiran gaggawa. Ya dinga kallonsu bakinsa na rawa,ko saurarensa basuyi ba suka barshi a gurin yana zufa!!

Alkali yayiwa me citta fata-fata tare da tonan asiri gaban bainar jama'a da iyalansa me citta kuka ne kawai bai yi alkali yace dole kuma sai ya bawa *Amjad* tara ta miliyan biyar ko ya zauna gidan yari tsawon shekara biyar. A lokacin me citta ya dinga share hawaye tabbas idan ya bada miliyan biyar aka biyar na dukiyarsa ta yi kasa dama yaudarar su Rambow yake da yace zai basu miliyan biyan. Kawai sai ya zab'i zaman gidan yarin domin shi mutum ne me mugun San kud'in tsiya, aikuwa nan take Alkali yasa aka tasa keyarsa zuwa gidan kaso iyalinsa na kuka. Ganin kukan da iyalinsa suke ne yasa Amjad ya kuduri niyar futo dashi amma ba yanzu ba sai yayi shekara biyu tukkuna ya San mecece duniya

Me citta na cika shekara biyu *Amjad* ya karb'o shi daga gidan kaso tare da saka hannun alkali me makon me citta ya gane mecece duniya bayan ya futo sai ya sake d'aura damarar ganin bayan *Amjad* ko ta halin k'aka ne

Wannan shine mussababin abunda ya tsananta gaba a tsakanin sa da Alhaji Hashimu me citta.

*Zamu dawo ainihin labari a pege na gaba*

*19/October/2009*
[11/1, 10:55 PM] .: *BABBAN YARO*

mallakar_BINTA UMAR

LITTAFIN MALLAKI NA NE KUN BIYA KUD'IN KARATU NE KAWAI DUK WACCE TASAN ZATA FUTA DASHI WAJE DON GIRMAN ALLAH TAYI MIN MAGANA NA DAWO MATA DA KUDIN TA.

*23*

Kallo Umma ta bini dashi har na shige d'akinta simi-simi ina addu'ar Allah yasa kar ta tuheme ni da wata magana. Aikuwa ina cikin kuryar d'akinta bayan na idar da sallah ina Jan carbi Ta kwala min kira tana daga parlor gabana ya fad'i sosai na mike na futa lokacin gari ya soma haske Mimi na kwance a kan abun sallah a gefan ta da alama ta idar da sallah ne, tace." Zauna in yi mini tsaye aka." Zama nayi kusa da ita ta aje carbin hannunta tana kallona cikin nazari daga bisani ta ambaci sunana da "Asma'u" na d'ago kaina tare da amsawa cike da tuhuma tace "wankan me kikayi da asubar fari" shiru nayi saboda bani da amsar da zan bata domin dai tunda nake ban taba Wanka da asubah  ko da ko wankan tsarki ne na alada tace "ba dake nake magana bane." Zuciyata ta saka min wani Abu da sauri nace." Umma kin San jiya na Sha magugguna to shine na tashi naji jikina ya jike da gumi ina jin zafi sosai shine na watsa ruwa." Na kare maganar bakina na rawa. Shiru tayi tana nazarin magana ta minti biyar tace." Ban yarda da maganar ki ba Asma'u. " na dago kaina ina kallonta nace." To Umma ke wane Wanka kike tunani zanyi da asubah.? Umma tace." Na sani ko kin fara mafarki aure kike so." K'irjina na dafe ina zaro ido nace." Wallahi a'a Umma.' Tace" bana son munafurci wallahi idan aure kike so sai kicewa Musa ya futo kawai ni ba yarinya bace duk abunda kike ciki kamar a tafin hannuna kike." Ina kallon Mimi tana kunshe dariya, hararata nayi cike da takaici nace." Umma ki bar maganar nan don Allah ni kam Musa bai min ba wallahi." Na fada ina zumb'ura baki tace." To sai ki nemo wani domin naga aure ki kike so sai ai miki. " kafin ince komai sai ga Yaya Aminu ya futo Cikin shirin makaranta ya watsa mugun kallo tare da fadin." Wallahi Umma yarinyar bata da mutumci d'azu ina mata magana ta wuce tana k'okarin zagina." Yafad'a yana k'okarin zama, Umma tace." Nima fad'in da nake Mata kenan ai Yaya Aminu yace." Idan jarrabawar su ta futo Zan musu kokari su samu su je legal ko FCE ko dufoloma su samu kafin suyi aure. Umma tace." Da ko ka kyauta wallahi amma ina ganin ai ba karatun suke so ba aure su ke so." Mimi ta mike zaune da sauri tace." A'a Umma muna so wallahi ko baba Nafi'u ma yace." Zai nema mana makaranta idan jarrabawar mu ta futo mu cigaba." Umma tace." Ai fa ke da kike da me uwa a gidin murhu." Aminu yace." Wallahi na manta dashi Bari in daina wahalar da kaina kawai tunda yana da ra'ayin Ku cigaba sai Ku cigaba kawai.
Umma tace." Amma idan miji yazo dole a ajiye karatu ayi aure. Mimi ta sunkuyar da kanta wai ita kunya, nace"a'a Umma aure sinna ce haka ma karatu yana da mutukar muhimanci garemu idan mun fara sai ayi yarjejeniya da Wanda zai auremu." Yaya Aminu ya kawo hannu zai buge

min bakina na kauce da sauri yace." Shegiya me bakin magana ke ko kunya bakiji ba gaban Umma kike wannan maganar cikin kukuni nace." Ai gaskiya ce"
[10/21, 8:00 AM] 👄: Mik'ewa yayi da niyar futa na zabura! Da sauri na b'uya bayan Umma hararata yayi kurrum yace." Umma zan tafi." Umma tace." Bazaka tsaya ka karya ba." Girgiza Kai yayi yace." Muna da darasi k'arfe bakwai bana so na makara" Umma tace
" To Allah ya bada sa'a" ameen yace ya futa kafad'arsa rataye da jaka ta makaranta, murmushi nayi a fili nace "Yaya Aminu Dan makaranta" Umma tace " da kikaga ya futa ko." ? Dariya muka sa ni da Mimi Umma ta mik'e da nufi zuwa kicin tace." Ai ya kamata Ku shirya kuje gidan Kawun NAKU Nafi'u kun kwana biyu baku je ba." Nace wallahi kuwa Umma zamuje yau insha Allah" kicin ta nufa muka bita domin kama mata ayyuka yau Umma awara tayi mana da kunun tsamiya wai haka na dinga dabkar yaji duk da attaruhun da aka saka cikin awarar hummm ni kam ina son yajin barkono a rayuwata. Muna gama karyawa muka fara aikin gida ita kuma Umma tana harkar cinikin ta da yara har da Matan aure ma masu shigowa. Bayan mun gama mukayi wanka.

Mimi ta Ciro mana wani les baki da ratsin ja a jikinsa na waccan sallahr ne. Wai shi zamu sa nace "sai dai in ke kika saka wallahi kin San na tsani les din shine zaki wani Ciro mana shi." Mimi tace" naga mun Dade bamu saka shi ba." Nace." Ki saka ke ban hanaki ba." Kallo na take ina birkito kayan cikin akwatuna na futo da wata atampa haitaget anyi min doguwar Riga me madauri daga baya hannun rigar dogone amma an tsaga shi sosai duk kasan galalin hannuna in nasa rigar ana gani blue and orange ne na amma blue yafi yawa a jikinta saboda haka na d'auko mayafi orange na aje. Mimi tace" kin Mayan cewa atampar nan WALLAHI ." nace "tanayi min kyau ne Mimi." Tab'e baki tayi tace." Dinkin yana nuna tsaracin ciki kina daga hannu hammta a waje." Duka na Kai mata ta kauce da sauri tana dariya nace." K'aryar ki kice HAMMATA ta na wari ko kiga gashi ko daya kullum Cikin aski nake ke zaki fadawa wani saboda kin San na tsani warin hammata." Mimi ta kyalkyale da dariya tana fadin "wallahi har kin tuna min da Hafsat me warin." Dariya na sa nace." Ni na manta da ita wallahi." Mimi tace." Asma'u baki da mutumci WALLAHI haka kika tasa Hafsa a gaba a skull duk kika tsagwame ta da ta matso daks dimmu zaki fara tsokanrta *Me warin ham* Allah sarki Hafsa tun bata ganewa ta gane cewar da ita kike dole dai kika saka ta ta daina zuwa gurimu dimu Nace." Wallahi Mimi na tsani inga mace tana kazanta shiyasa na takurawa Hafsa in ta fahimta sai ta gyara haba!tasan zata shigo cikin makaranta cikin mutane baza ta tsaftace jikinta ba nifa wallahi mijina zai ga tsafta domin shi kanshi kullum cikin kyalkyale masa ji nake." Mimi tace." Ga manyan mata hummm mijin da bai zo ba ana masa tanadi lallai wannan me sa'a ne." Nace fad'i ki kara Mimi duk namijin da ya same ni ya tsinci dami akala domin sai na sanja masa rayuwa ummm! Mimi kenan ni nasan wacece ni." Mimi tace "maganar Umma ta futo lallai Asma'u aure kike so." Hararata nayi nace "don Allah tashi ki saka kayan ki , e aure nake so Mimi waye zaiki sinnar Annabi muhammadu." Mimi ta mike tana saka kaya tace." Babu gaskiya kam Allah dai ya zab'a mana nagari." Nace ameen ya rabbi.

Mun futo a kintse Sosai mu kayi kyau Mimi tasha kwalliyar fuska ni ko hoda kawai na saka sai kwalli Dana zirara ko man leb'e ban saka ba, Umma ta kalleni tare da fadin " Asma'u ban ce ki

daina saka atampar nan ba haka kurum kinje an miki lalataccan dinki ko."? Nace Umma duba fa ki gani atampar da kyaunta kuma ni duk cikin kayana nafi sonta wallahi." Umma tace." Ke kika sani ai ba kyawun atampar ne abun dubawa dinkin ne." Nace Umma na kai wa Ummi makociya ta gyara min hannu" shiru kawai Umma tayi min domin tasan duk tsarina ne, tace." Kar Ku kai magariba baku dawo gidan nan ba." Muka ce to Umma" tace Ku daina min da Kawun NAKU da Mamansu Munubiya" muka je zata ji insha Allah. Nan muka futa muna taku dai-dai mussaman ni sau kace wata 'yar gidan shugaban kasa. Da kafa muka k'arasa bakin titi muka tsaya domin jiran abun hawa. Wasu 'yan mata suka zo wucewa ta gefenmu nace " Mimi kinga irin handbag dina ko ajikin waccan" Mimi ta kallesu tare da fadin "aikuwa irinta CE." Nace." Anya ko Mimi bazan je in d'auko kayata ba" tace" kin dai ji abunda Umma tace don Allah kar ki jawo mana wata Matsalar " shiru nayi mata kawai ina sak'e-sak'e. A dai-dai ta sahu ta tsayar mana tayi ciniki dashi tare da fada mana inda zai kaimu, muka shiga, mun Dan yi nisa Mimi tace." Idan mun futo daga gidan Kawu Nafi'u mu biya gudansu Hafsa mana tunda kusa ne." Nace "muje mana ai babu komai. " Mimi hira take min ni ko ina can tunanin yadda za'ayi in d'auko handbag dina gidan guy nan . mu ka sauka Titin wajan gidan marigayi Ummaru ta'ambu da kafa muka dinga shiga lungunan kafin mu Isa gidan Kawu Nafi'u muna shiga yaran gidan suka rungume Mimi suna ihu!! Kallonsu nake INA dariya nace" nu baku sann ba kenan" su dawo kaina nan Mamansa Munnu ta futo tana mana maraba tace Ku shigo ciki yara sun hanaku shigowa . nan muka shiga parlor me d'auke da kujeru biyar da kafet malale a tsakiyar gefe friji ne sai kayan kallo lavuleye kewaye a parlor ka hotunan shuwagabbanin kasa a manne a bango kana ganin tsarin gidan kasan na 'yan boko ne

Muka gaisa da ita Sosai tare da fada mata sak'on Umma tace." Tana amsawa tare da cewa "ai duk laifin Ku ne da bakwa zuwa akai akai sai Ku d'ebo wattani ba kuzo ba ke Mimi haka dangi zasu yi ta cigiyar ki." Mimi ta sunkyar da kanta cike da kunya nace." Mamansa Munnu Kawu Ba yanan ne." Tace." Bai jima da futa wallahi" nace Munnu fa." Tace" yanzu ta shiga ban daki tana Wanka " muka mike muka shiga dakin Munnu kan katifar ta muka zube ni da Mimi Munnu ta baza hotona kan katifarta tana kallo duk irin tsaffin hotanan ne na makaranta da wasu lokacin muna yara. Wani hoto Mimi ta mik'o min tace." Asma'u kin ganki a nan"? Karb'a nayi ina dubawa Mimi tq fashe da dariya, da sauri na yi yunk'urin yaga hoton cike da takaici hoton anyi mana shine farko fara zuwa makarantar mu lokacin muna kwailaye muna sanye da sabbi unporm ko wanne da k'atuwar jakarsa sai murna muke mun shiga secondary skull Mimi ta fuzge hoton tana dariya tare da fadin" kin San Allah Asma kina kama da 'yar film din nan Nafisa Abdullahi" hararata nayi nace." Kin cuce ni Mimi". Tace. OK kina nufin kin fi Nafisa kyau kenan."? Nace" nesa ba kusa ba wallahi . Mimi tace "bari Munnu ta futo ta fada miki gaskiya." Aikuwa sai ga Munnu ta shigo dakin tana goge kanta da k'aramin towol tace." Ku kuma 'yan iska yaushe kuka zo" nace." Babynaaaaaa!!! Cike da tsoka na fad'i maganar Munnu ta kawo min duka tana warce hoton dake hannuna dariya na fashe da ita ina nuna ta da hannu. Ita ko Mimi dake mayyar dariya ce kwanciya tayi kan katifa tana sheka dariyarta. Munnu ta wuce mu cike da takaici take fadin "banza ye kawai wad'anda basa manta Abu." Ina dariya nace." Ya za'ayi mu manta Munnu ta Shamsu kenan baki da aiki sai kallon hoton Shamsu ki ishi mutane a skull da Baby na yayi kaza babyna yace zai siya min kaza hummmm! Shamsu ya San takan

sace zuciyar 'yan mata gashi ya sace taki ya gudu ya barki da ciwon sonsa"
Mimi tace" wallahi kuwa kin San ko a skul aka zagi Shamsu sau kunyi fada da ita ko ta d'aura gaba dakai, ummm! Ni kaina sau nawa Munnu tana gaba dani duk akan ina mata magana ta rabu da Shamsu Dan yaudara ne." Nace." Nifa WALLAHI duk son da nakewa Namiji bai Isa na nuna masa ba sai dai ya gani a aikace." Munnu tace." Ni Ku k'yaleni don Allah kuyi min addu'a kawai Allah ya cire min son Shamsu daga zuciyata" nace." Munnu kina so ki rabu da soyayyar Shamsu a zuciyar ki amma kike kallon hotan sa." Shiru tamin nace." Kinga to" juyowa tayi tana kallona na daga hoton Shamsu dake hannuna na zaga shi gida uku na watsar nace" wannan shi yafi dacewa dake amma kullum kina kallon hoton sa ta Yaya zaki mance dashi." Mimi tace kinyi min dai-dai da kika yaga wallahi" Munnu ta juya ba tare da tace mana komai ba ta cigaba da kintsa jikinta mu kuma muka cigaba da caccakar Shamsu gami da tsine masa sabo yaudarar da yayiwa Munnu wacce ta saki jiki dashi sosai ya gudu ya barta.Bayan ta gama shirya ta juyo tana fuskantar mu tare da fadin " INA kukaje ne kula biyo tanan domin nasan dai ba takanas kuka zo nan ba" Mimi tace" aikuwa kin fad'i ba dai-dai ba takanas muka zo nan domin mu wuni amma za muje gidansu Hafsa me warin Ham!! Munnu ta fashe da dariya tana nuna Asma'u dariya muka kwashe da ita dukan mu sai kace wasu tab'abb'u.

*****

B'angaran Hibbah kuwa tana zaune har wajan goma na dare tana jiran dawowar *Amjadu* shiru bai dawo ba kamar ta fasa kuka haka take ji gashi bata da numbar sa ga wata sha'awrsa na damunta tunda ya d'and'ana mata zumarsa a baki shikkenan taji tana son kara kasan cewa dashi, jiki babu k'wari ta futo daga dakin tana sakkowa kasa taga haske tar mutane sai kai kawo suke tamkar rana domin wasu ma a lokacin suke shigowa gurin cikin motocinsu wasu da 'yan matansu wasu da abokan su gasu nan dai. Duk tarin mazan da suke Binta da kallon sha'awa Sam basa gabanta domin yanzu ita babu Wanda take gani a gabanta sai Sadauki *Amjadu* shi kadai ne burin ta. Motar ta bude ta shiga ta futa daga hotal din.

**********

Bayan munci abunci munyi sallah azuhur ne sannan muka sake kintse jikinmu domin zuwa gudansu Hafsa muka futo mu ka sanarwa da Mamasu Munnu tace" to daga can zaku wuce kenan."? Nace "Eh daga can zamu wuce gida" d'akinta ta shiga tana fadin "Bari in zo to" mu kowa ni da Mimi hanyar futa muka nufa saboda mun San halinta kullum in muka zo sai tace zata bamu kudi." Aikuwa sai gata ta futo hannunta da gudar Dari biyar tare da wata Leda me Zane Zane.  Ta mik'o mana tana fadin Ku karb'a Ku kara kud'in mota" nokewa mukayi cike da kunya Mimi ta karb'i ledar tana fad'in "zamu karb'i wannan amma ki bar kud'in naki" Munnu ta karb'i kud'in tana fadin" Umma kyalesu suna so wallahi munafurci ne" kawai na basu in mun futa" Ummansu Munnu tace" to Ku gaida gida Ku gaishe min da Umman taku " mukace "zataji sosai wallahi.

Muna futa na warce Dari biyar din hannun Munnu nace." Bani to salon mu manta mu tafi ki rike

ko ai na gano ki" Munnu tace" to mayyar kudi kar ki jimin ciwo a banza" Mimi tace "Munnu har kij tuna min da wani Abu da ya faru shekaran jiya" Nan Mimi ta kwashe haduwar mu da guy nan ta fada mata harda watsa masa kud'in da nayi
Munnu ta dinga min masifa kamar wata uwata take "fadin WALLAHI kin cuce mu na rantse da ina gurin sai nayi miki duka kuma na tsinka ki a gurinsa ke wacece da zakiyi watsa da kudi masu yawa a daure a kyauwa 'yar bura uba kina fama da kod'add'iyar atampar ki haitaget sai shegen girman kan tsiya malam" ta k'arashe maganar cike da takaicin abunda na aikata, Mimi dariya take kamar Cikin zai ciwo ni ko sakin baki kawai nayi INA kallon Munnu tana zuba min masifa kamar ta ari baki, dariya ta kufce min na fada soron wani gida na zauna inayi biyo ni sukayi duk da haka Munnu bata daina surutai ba, nace." Munnu WALLAHI ban tab'a ganin me mugun son kudi ba irinki tabd'ijam!!! Munnu!! Na fada ina dariya. Tace" wallahi da ina gurin sai naje na tsince kudin na bashi hakuri, Um!!!! A wannan zamani yanda kudi suke wahala ana bahariyar tsiya" na mike tsaye tare da fadin"in kina so sai in raka ki idan zaki same shi ki bashi hakuri dama na manta handbag dina a gidan shi" Munnu tace"wallahi muje zan bashi hakuri sai dai Allah yasa ya bamu kudi" bani kadai ba har Mimi dariya take, nace" Munnu ya ishe ki WALLAHI kar ki mai damu mahaukata a hanya sai faman dariya kike saka mu. Tace" Ku muje na daina" muka futa daga soran gidan muka cigaba da tafiya babu Wanda ya sake cewa komai. Daf da zamu shiga gidansu Hafsa ne Munnu tace"Asama da gaske fa nake muje gidan guy nan don Allah" nace" zamu je in dare bai yi ba". Mimi dai shiru tayi mana muka shiga gidansu  Hafsa da sallama. Tana zaune kan kujera 'yar tsungo tana gyara wake ta mike da sauri saura kad'an ta zubar da waken nace" hankali dai ki zubar ki daku wallahi" da ihu!! Tayo kanmu tana murna nayi saurin gocewa don kar ta rungume ni inji tsaminta, duk sun gane dalilina nayin hakan har ita Hafsa din, dake ta san halina bata damu ba, ta rike hannunsu Mimi muka shiga d'akinta, nace." Ke Hafsa INA mamanku" kamar me jin tsorona tace"ta tafi unguwa" nace"sai kije ki siyo mana ruwa da Lemo mai sanyi"

Tace" Ke fa kin fiye Abu kinga ban kawo muku bane." Nace "si hali na sani ne rowa da......... Na ki karasawa ina b'oye dariya Hafsa ta d'auke kanta cike da jin haushina ta cigaba da hira dasu Mimi ni kuma na dinga bin dakin Hafsa da kallo ina kunshe dariya. Ta mike da sauri tare da fadin" ai yau ina da manyan baki bari in sanya yaro ya siyo muku ruwa da lemo ta futa da saurin ta.

Mimi ta kalle ni had'e da bata fuska tace"Asma'u babu kyau cin fuska  don Allah ki k'yale baiwar Allah nan haka wallahi tana d'aga miki kafa" nace" me nayi mata to" Mannu tace"ki daina kiranta da me warin HAMMATA" nace" na daina shikkenan" suka cigaba da shirarsu ni kuma ina kalle kalle a dakin can na hango Wani rubutu jikin bango anyi shi da blue din maka tare da wani k'aramin hoto  an manna gurin

 Mik'ewa nayi na isa gurin INA fadin "Su Hafsa 'yan gayu ken..... Magana tace ta mak'ale a mak'o gwarona sakamakon gani fuskar guy nan jikin picture din dake manne a bango gaba na fad'uwa na bi rubutun ina karantawa, abunda nagani an rubuta ya gigita ni gami da dimauta ni. _*Ilov my love my sweetheart yaya na farin cikina Amjadu ina bal'in son ko zuciyata tana

azabutuwa da kaunar ka zan iya kashe kaina saboda kai ina mutukar kaunar ka yayanaaaaa!*

Na nemi miyau na rasa a bakina ya bushe k'amas na fara tunanin meye hadin Hasfa da guy nan to? Gashi tana kiransa da yayanta kai duk yanda akai da akwai alamar tambaya, idan Hafsa suna da alaka da guy nan me ya jawo musu talauci haka duk tsiya si zai taimaka musu.

Motsin shigowar Hafsa naji nayi saurin komawa na zauna jikina na tsiyayar da gumi, Sam su Mimi ba su ankara da komai ba suna can suna hira, Hafsa ta shigo dakin hannuta rike da ledar ruwa pure watar da Lemo cocarcolar a ciki guda uku ta aje gabanmu tunda ta shigo nake zabga mata harara ina mata wani irin kallo, ita ko sai washe baki take tana mana labari,, sai dariya take tace"Asma'u ga lemon nan" hararata nayi ita da lemon nata ta d'auke kanta kurrum tana murmushi.
Hirarasu sukeyi babu ni a ciki sai dariya suke yi Hafsa sai tsoma ni take cikin hirarar tasu ina gwaleta.

Daf da magariba nace "Ku tashi mu tafi haka ke Munnu dama a gida kike". Mik'ewa sukayi a tare Munnu tace." Kin manta da maganrmu ko"? Nace" ban manta ba" nayi waje na kyalesu tare suka futo har Hafsa ta raka mu har bakin titi tana godiya sune kawai suke amsa mata ni ko ko kallo bata ishe ni ba.

Har aka idar da sallahr bamu samu abun hawa ba kun San dai tadda titin k'ok'i yake a baude bayan haka kuma muna tsakiyar kasuwar kurmi. Sai muka fara tafiya a kasa, gashi gari ya soma duhu, Wani me a dai-dai sahu yazo ya tsaya gabamu tare da fadin " INA zakuje 'yan mata "? Nace." Rijiyar zaki scound get Cikin Jambulo " Mimi ta kalle ni da sauri nima na zare mata ido tare da fad'in" in zakije kawai ki shiga mota mu tafi." Baki na rawa tace " INA tsoron fadan Umma kina ji fa tace." Kar mu Kai magariba ba ko." Ko sauronta banyi ba naja hannun Munnu muka shiga Mimi ta shigo duk jikinta a sanyaye mai a dai-dai ta yaja motar muka tafi.

*Tofa*
My fans ko me zai faru a haduwar Asma'u da Amjad a karo na biyu

Ku muje zuwa dai

*21/October/2019*
[11/1, 10:55 PM] .: *BABBAN YARO*

mallakar_BINTA UMAR

LITTAFIN MALLAKI NA NE KUN BIYA KUD'IN KARATU NE KAWAI DUK WACCE TASAN ZATA FUTA DASHI WAJE DON GIRMAN ALLAH TAYI MIN MAGANA NA DAWO MATA DA KUDIN TA.

*24*

Dai-dai jaction muka sauka nace "Mimi bashi kudinsa" nan take ta ciro Dari biyar ta bashi ya dauki Dari uku ya bamu canjin Dari biyu, muka tsalla a nutse. Estate din shiru kamar babu wani mahalukin da take rayuwa a cike sai dai haske dal-dal a ko ina duk da cewar gidaje uku ne kawai a ciki,muna shiga karnukan da suke ciki suka fa ihu!! Tare da yowa kanmu duk suka tsorata ni ko na dake yare da cewa"idan kuna nuna razanar Ku a fili sai su zata b'arayi ne." Munnu tace." Wallahi asma'u na fara da na sanin zuwa fa" gaba nayi ban saurare ta ba, suka biyo ni a baya. Daga can nesa na hango shi ya futo daga massalacin dake jikin gidansa, zai shiga gida yana sanye da doguwar jallabiya fara tas!! Irin ta Larabawa kwata-kwata su Mimi basu ganshi ba nice na ganshi, nima kuma da suffar shi na gane shine. Muna zuwa bakin get din me gadi ya bimu da kallo irin na tuhuma nayi saurin cewa" munzo gurin me gidan ne." Kallonmu yake cikin nazari yace." Kunyi b'atan kai 'yan mata banan bane" nace" kaga malam wai ba nan bane gidan *Amjad* ba" yace" nan ne 'yan mata" cike da bada umarni nace" to sai ka bude mana malam" yace." Me gidan bai bada izini ba domin da yasan da zuwan Ku zai fada min a bude muku get Ku shiga" haushin sa ya kamani na masa wani banzan kallo tare da cewa" kai malam kalle mu da kyau ka gani ba tsiyace ta kawo mu nan ba arziki ne, kuma mu 'yan uwan me gidan ne idan kana tamtama kaje ka tambayo shi kaji" kallona yayi naga yayi saurin risinar da kansa, dama ni haka nake da mugun kwarjinin tsiya in na zuba ma mutum idona baya iya ketare hukuncina to haka ce ta faru da me gadi bakinsa na rawa yace" bazan barku Ku shiga ba domun bansan da me kuke tafe ba, amma bari inje in Sanar da masu tsaron kofar shi halin da ake ciki." Ya ya bud'e karamar kofar ya shiga yana k'okarin kullewa babu zato yaji an buge hannunsa yayi saurin cirewa na fada cikin gidan INA kiran su Mimi suka shiga da sauri, nace" tunda mun shigo si munyi me wuyar kuma.

Duk abunda yake faruwa yana kallonsu ta CCTV Camara  d'inshi ya cire rigar jikinsa daga shi

sai shout nickar da kwalin Lemo a hannunsa yana sha, murmushi ne kwance a fuskarsa yana mutukar mamakin taurin kai irin na yarinyar mamaki yake sosai yanda akai har suka samu nasarar shigowa bayan sun baza karnuka a gurin saboda tsabar kokari da k'arfin hali har tana buge get man d'insa tana shigowa ko ubanta ta aje masa a gida ihu! A fili yace." Kome ta zo tayi min a gida oho cike da mamaki yake kallonsu ita dasu rambow tana fada suna fad'a kamar zata tsokane musu ido Wayarshi ya d'auka dake aje a gefansa ya nemo numbar Rambow yana d'auka yace." Barsu su shigo" ya kashe wayar ba tare da ya tsaya yaji me rembow zai ce ba.

Rambow yace." Kun fi sa'a Boss yace" Ku shiga amma da badan haka ba wallahi ba zaku shiga ba" hararsa nayi nace" shima ogon naku nakusa karya alkadarinsa" cike da mamaki Rambow ya bita da kallo jin abunda take cewa, hannun munnu naja muka shige DOMIN naga Mimi sai wani ja baya take.

Muna wucewa Doh-doh yace"wallahi ina jin tausayin yarinyar nan duk ranar da zata shiga hannun Oga sai ta gane shayi ruwa ne" Rambow yayi k'wafa tare da fadin" k'aryar rashin kunya ta dama.

A hankali muka tura kofar parlor muka shiga, sanyi kamshi ne ya buge mu mu dukan mu sai muka fara zare ido sosai nake karewa parlor kallo DOMIN zuwana na farko ban kalle shi ba, wow gaskiya na yaba da tsarin parlor gami da k'yatuwar sa, komai na parlor orange color ne ina mutukar son Abu orange Munnu tace."Asama mun banu kizo mu koma kawai na fasa" nace ke dallah can tsorone daku wallahi Ku zauna ni inje dakin shi si na sani mybe ma baya ciki.

Mimi ta rik'o hannuna tana girigiza mun kai wai kar inje fuzge hannuna nayi nai gaba ba tare da na wai wayo su ba."

Ganin tana nufo kofar shigowa ne yasa ya mike da sauri haske dakin ya kashe ya tsaya jikin bango yana saurarон shi gowarta. Ina bude kofa naga duhu d'un d'um!! Na gane inda makkuni yake aikuwa nafara lalube zab kunna". Wani abu naji ina tab'awa shi ba gashi ba shi ba fatar jikin mutum ba gashi dai yafi yawa a jiki, gabana ya fara fad'uwa jin kamar hucin nuffashin mutum, hannuna na daga da niyyar in kunna futular domin na fara tsorata, da k'arfi! *Amjad* ya jawo ta kirjinta ya daki nasa ya zura hannunsa kasanta ya rik'o kwankwanso ta sosai inda baza ta iya guduwa ba, sannan ya mik'a d'aya hannunsa sama ya kunna futula, haske ya gauraye dakin.

Cike da tsoro na kura masa ido fuskarsa a murtuke shima nasa idon ya samun kamar zai cinye ni danya, munfi minti uku muna kallon_ kallo kafin nace." Sake ni inyi abunda ya kawo in tafi." Shiru yayi min bai CE komai kuma har yanzu idonsa na kaina yana kare min kallo inda naga ya fi kalla a jikina na kalla ina dubawa, sai naga kwaurina da ya futo waje dalilin yanayin dinki bayin saurin Jan mayafi na rufe ina hararsa, hannunsa yasa ya janye gyalen ya jefar kasa ya cigaba da bin jikina da kallo kamar tsohon Maya. Cikin ikon Allah kuma time din banji wannan azabban

fleengs din Dana ke ji ba in ya kusance ni.

Karfina nasa da gaske nake k'okarin ture shi. Ko motsi kirki ya kiyi . muryar shi a harhad'e yace." Me kika dawo kimin a gida"? Ko nuffasawa ban bari yayi ba nace." Bana munafurci na dawo d'aukar handbag dina ne."
[10/22, 8:58 AM] BintaUmarAbbale👄: Kallo yake min kamar Wanda be tab'a ganina ba, gashi ya wani had'e fuskarsa tamau!! Yace." Karya kike da akwai dai abunda ya kawo ki,babu wata handbag da kika manta." Fuzge jikina nayi ina galla masa harara gefe na matsa ina bin dakin da kalo ko a ina zan ga handbag din oho min... Cikin tafiyar shi ta jarumai ya nufi bed d'insa ya zauna tare da Dora kafa daya kan d'aya yace." Zo ki duba kayan ki inda kika aje ki fuce min daga d'aki". Kai tsaye.. Na nufi bed d'in na fara duba bayan shi da lukunanshi,aikuwa sai na hango ta, da sauri na zura hannuna na d'auko abata.  Bayansa na kalla naga ki juyo bai yi sai danna waya yake. Rike da ita a hannuna na tsaya a kanshi nace." Sai sak'on da aka bani na bak'a" ya dago kanshi tare da cewa." Ina jin fad'a min ki fuce ki bani waje" cike da taikacin yanda yake kyarata wai in fuce!!! Sai kace wata tinkiya nace." Kai kaga bafa komai ne yasa nazo gidan ka ba da har kake k'okarin gaya min magana dama ko baka ce na fuce ba zan fuce in bar maka d'akin ka..... Ya katse ni ta hanyar fadin " naji ki fad'i sak'on ki, ki futa min a d'aki fitinanniya kawai wa zakiyi wa preetanding ni nasan abunda ya k'ara kawo ki gurina kuma baza ki samu ba" ya k'arashe maganar cikin sigar rashin mutumci" zuciya ta kamar ta tsage saboda zafi nace." Ni ba shashashar mace bace kuma ni ba irin 'yan Matan ka bane wallahi ni nafi k'arfin ka bare in kawo kaina gurin ka ko abunda kayi min baya ma Allah ya isa."

Murmushin gefan baki yayi ya d'an sosa sumar shi kad'an da Jan ido ya kalle ni still da murmushi a fuskarsa yace." Ok naji ba abunda ya kawo bane kin tsaya kina Jan magana fad'a min sak'on ko in sa yanzu ayi waje dake domin bana bukatar ganin wannan mummunar fuskar ta ki bak'akirin!!!!!!!!!! Asamau da tsani ace mata mummuna lokaci guda hankalin ta ya tashi taji wani irin hawaye me zafi na k'okarin zubo mata da sauri! Ta aro jarumta da dauriya ta aza a ranta, wani kallon Tara saura kwata ta mai tace." Wa kake da suna *Amjad* ko me??  Kai dai ka sani, bari kaji wani Abu da baka sani ba, kyau ba shi bane kyawun hali da nasaba me kyau da shi a ke tunk'aho Allah Ubangiji ya raba mu da kyau irin naku babu kyawun hali da nasaba me kyau Wanda nasan ni nafi ka nasaba da tarbiyya me kyau duk wannan iskancin da kake rashin tarbiya ne da rashin samun iyaye jajirtattu saboda haka tun wuri gwara ka koma islamiyya ka samo ilimin addini domin kasan meye banbanci kyau da muni." Ina karasa maganar na nufi kofar futa ina  da na sanin zuwa gidan.  Kofar nake k'okarin budewa taki nayi-nayi na juyo a fusace! tare da kaurara murya ta nace" zo ka bude min kofa in futa daga wannan annobar" ina kallonsa ya mik'e ya nufo inda nake, fuskarsa na tsurawa ido kamar mala'ikan mutuwa take naji tsoro ya shiga raina na kauce daga bakin kofar, cike da k'arfin hali na dinga watsa masa kallo ko kallona bai ba ya bude kofar zai futa na biyo bayansa, da sauri hannunsa guda ya sanya ya ingiza ni ciki dakin na fad'i kasa, ko juyo wa bai ba ya rufe kofar tare da murza key! Na mike a zafafe! Na daki! Kofar dak'afata ina janta tun karfina ko motsi tak'iyi  ihu!!!!! Na kurma sosai ina fad'in "Idan baka bud'e mun kofar nan na futa ba kai ba d'an hakan bane, d'an iska asharari"!! Duk yana jin haukan da take wai shi take zagi harda su d'an iska asharari wai ma meye alk'ar

shi da yarinyar ne da har ta samu dama akan shi shine Mara tarbiyya Wanda iyayensa suka lalata shi, ya zama dole yarinyar ta karb'i hukunci a gurin shi, fuskarsa ya kara hadewa ya Isa tsakiyar parlor inda ya hango su Mimi tsaye bakin kofa suna zare ido dama yasan dasu tunda ya gansu cikin CCTV Camera, Cikin jarumta ya durfafe su,sai ga Munnu tana rawar k'afa ganin wani ingarmar namiji na kusan to su, cike da tsoro ta zube bakin kofar. Ita ko Mimi suma ne kawai bata yi ba daga ninsa tunda ya futo ta tsora mishi ido tana kallonsa wata muguwar soyayyar sa na kara nunkuwa a cikin zuciyarta. Kallonsu yayi a nutse yace." Ku ne 'yan rakiyar ta"? Munnu ta gyad'a kanta alamar "Eh bakinta na rawa tace" ina wuni" ko kallonta baiyi ba ya bud'e kofar parlor ya futa, minti biyar ya dawo yana kallonsu tare da fad'in" Ku tashi a mai daku gida". Cikin dauriya Mimi tace" Asma'u fa". Da gefan ido ya kalleta ya d'auke kansa tare da fadin." Nace tazo a kai ku gida tace baza ta tafi ba so kuyi tafiyar Ku kawai Ku k'yaleta duk sanda ta ga damar tafiya sai ta tafi." Jikinsu ya soma b'ari Mimi tace" kayi hakuri don Allah kaji"" miskilin murmushi yayi ya Dan Sosa kansa Wanda hakan ya zame masa jiki yace." Ke ba laifina bane fa nata ne, kunga ni ita ta kawo kanta har gidana ta bude min daki ta shiga ta zage ni ta fad'a min duk maganar da tazo bakinta to babu laifi na" hanya ya nuna musu da hannu a karo na biyu yace." Doh-doh na jiran Ku a mota a sauka lafiya." Simi-simi suka wuce suna waiwaye gefe guda kuma suna mamakin abunda Asma'u ta aikata domin sun gazgata maganar sa saboda sanin halin kaifin harshe na Asma'u. Zama yayi a parlor ya rik'e kansa zuciyarsa na masa zafi sosai yake tunanin hukunci da ya kamata yayi wa yarinyar, murmushin mugunta ya saki da ya tuno wani abu kawai ya mike ya isa gaban TV ya kunna ya zauna cikin kujera yana kallonshi wani american film yake kallo ya manta da wata Asma'u dake d'akinsa a kulle sosai film din ya d'auke masa hankali.

Gajiya nayi da dukan kofar na zube bakin kofar ina mai da nuffashi wani abu me nauyi yazo ya tokare min a mak'ogwaro na a fili nace "wai me guy nan yake nufi ne da nine? Babu me bani amsa Mik'ewa nayi da sauri na Isa window na yaye labule INA lek'en waje tunani nake ko zan samu hanyar futa, ko alama babu wata hanya, nafi minti goma a tsaye a gurin gabana na fad'uwa, na juyo na kalli a gogo dake manne a dakin 9:53 na dare goma shaura minti bakwai kenan. Sai naji kafafuna baza su iya daukata ba, na duba wayata da sauri nake lalubar numbar Mimi na kira babu kudi a cikin wayar, da sauri na tafi cin bashi, da k'yar suka bani naira Hamsin dama suna bina bashi, Mimi na daga wayar nace." Kuna ina ne"? Tace." Muna gidan su Munnu yaushe zan koma gida ni kadai in cewa Umma me? Murya na rawa nace Mimi guy nan bai da mutumci wallahi ya kulle ni a d'akinsa" Mimi tace" Yace ke ce kika ce baza ki tafi gida ba". Cike da mamaki nace" Mimi sharri yayi min kawai kyaleshi" tace" nasan kin masa rashin mutumci shiyasa yayi miki haka" ga yanayin yadda Mimi tayi magana na gane ranta a bace yake nace." Mimi nayi masa din in zaki rama masa bisimillah" na katse wayar cike da taikacin ta wato ita bata jin ciwon kulle ni da yayi shi take k'okarin karewa,

Zarya na fara a dakin ina kaiwa ina kawo wa, da sauri naje na daki kofar! Da kafata kamar wata wacce ta samu tab'in hankali da k'arfi nace Idan baka bude min kofar nan ba kai ba d'an halak bane wallahi!!!Abunka da dare shiru ko INA yasa magana ta ta cika parlor murmushi ya saki a hankali yace." Yarinya inan zuwa gurin ki,zaki fada min wace irin alk'ace a tsakanin dake da har

kika samu dama a kaina....

*22/October/2019*
[11/1, 10:55 PM] .: *BABBAN YARO*

mallakar_BINTA UMAR

LITTAFIN MALLAKI NA NE KUN BIYA KUD'IN KARATU NE KAWAI DUK WACCE TASAN ZATA FUTA DASHI WAJE DON GIRMAN ALLAH TAYI MIN MAGANA NA DAWO MATA DA KUDIN TA.

*22*

Sama-sama Asma'u take jin Mimi tana  magana wani irin sarawa kanta yakeyi ga wani sanyi me ratsa jiki tana ji a jikinta,dishi-dishi ta ke kallon Mimi tana sallah  lumshe idonta tayi tana kara takure jikinta.Mimi ta idar sallahr ko addu'a bata yi ta mike tana ninke abun sallah ta futa waje da sauri.Umma na kicin tana k'okarin raba abinci tace." Umma In Kin zuba mana namu bani in je muci domin muje chamis din kinsan dole su taimabaya ko ta ci abunci nasan dai allura ce za ayi mata." Umma ta mik'o mata Fula's MA dai-dai ci cike da shinkafa da faduka da kifi d'anya abunci dai-dai na talaka tace." Aikuwa domin Kin San wannam zazzab'in na maleria dole sai da allura." Su duk a tunaninsu maleria ce take damun Asma'u. Mimi ta wuce da sauri tana shiga ta hau kiran sunanta "Asma'u tashi muci abunci muje a dubaki." Bude idona nayi a hankali nace."Mimi k'yaleni da chamis din nan don Allah." Sakin baki tayi tana kallona naja bargo na rufe kaina gaba daya ina takure wa." Tace "Dole fa ki tashi WALLAHI ke taurin kanki ne matsala." A hasale nace." Dallah ki kyale ni wai jikin ki ko nawa da zaki dame ni." K'arar!a kunnen Umma ta daga labule ta shigo rai a bace tace." Gwara ma ki tashi tun kafin ranki ya b'aci ita meye laifin ta kawai Dan ta damu da lafiyarki shine kike mata tsawa." Nace." Umma nifa

lafiya ta lao". Tsaki taja tace." Kin saba karya dama duk abunda ya same ki ke kika jawowa kanki wanka da magariba saboda haka ki tashi tun kafin raina ya b'aci." Tana gama maganar ta ta fuce daga dakin.
Cike da jin haushin Mimi na tashi zaune ina hararta had'e cinyoyina nayi ina ya mutse fuska tace." Ki sauk'o kasa mana." A hasale nace." Anki a sauko ki d'auko Fula's din abunci ki dawo dashi kusa dani in kin damu."Mimi tace." Banza masifaffiya." Shiru nayi mata ina hararata gefe guda ina matse cinyata Dan karta gane halin da nake ciki. Ta kalle ni cike da nazari tace." Wai meye tun d'azu kike matse cinjyar ki kamar wacce taji ciwo." "Ban sani ba." Abunda nace da ita kenan na sha kunu. Tab'e bakinta tayi tace." Mutum babu lafiya ma sai masifar tsiya." Share ta nayi kawai na fara cin abunci a ya tsine.Kad'an na iya ci na mike a daddafe na futa waje domin wanke hannuna, sauri sauri Mimi ta gama ci itama ta futo hannuta rike da hijabai ta mik'a min na sanya itama tasa ta wanke hannunta muka tafi. Ko da Anas me chamis ya gama duba ni sam bai ga wata maleria ba maganin zazzab'i kawai ya bani muka dawo gida, nace." Ki damu sai munje to munje muguwa kawai allurar dai da kike min fata bata samu ba." Dariya Mimi ta sanya tana zolaya ta ni ko na sha kunu.muna shiga gida na dauki buta na d'aura alwala can dakin Umma na shiga nayi sallahr mariba da Isha'i na kwanta kan daddumar ina addua'a Allah yasa bacci ya d'auke ni. Aikuwa Allah ya taimaka ni bacci me nauyi ya kwashe ni, Umma tace."tunda na samu bacci shikkinen Mimi ma ta dawo dakin a takaice nan muka kwana.

******

Granny ce take ta fama dashi ya fad'a mata abunda ta faru tunda ya shigo gidan take aikin rarrashin sa yana jin ta yak'i tanka mata sai kallon guri guda yake.cike da takaici tace." Wannan a cikin musklan ma k'arshe ne kazo ka zauna kana min dacin rai nayi tambar duniya kamin shiru shikkenan." Ta k'arashe maganar cike da takaici."

Kallon gefan ido yayi mata yaji ta bashi tausayi Sam bata son damuwar sa ko kankanuwa yace." Granny kin san Alhaji Hashimu abokin Dadyna ko." ? Tace." Ni ko nasan Hashimu me citta." Yace." To zan mai dashi prison wallahi." !! "K'ull!! Tafad'a tana kallonsa ta cigaba da cewa." Me yayi maka mutum magidanci me iyali zaka dauki hakkin su." Murya a sama yace." Yau ya assasa taro DOMIN a ci ma Dadyna mutumchi." Shiru tayi saboda tasan da kiyayar dake tsakaninsu ba tun yau ba, amma dake tsohuwa ce me hangen nesa tace." Sai ka kyaleshi ai da me rai ake ba da Wanda ya mutu ba. Mik'ewa yayi a zabure! Ya kai ya kawo a parlor yace." Impossible ina Raye a duniya granny babu mahalukin da ya Isa ya taba min dadyna ban ta kurawa rayuwrsa ba." Granny ta mike cike da tsoro tace." To me zakayi masa? Ka k'yale shi mana ba sa'anka bane." Ta k'arashe maganar tana kamo damtsen sa wai ita dole sai ta zaunar dashi kan kujera kamar tana Jan dutse yak'i motsa wa. Tace." Dube ka sai wani huci kake jiki a murde kamar dan danne"zama yayi cikin kujera yana huci yace." Granny yau me citta ya hada min taro har dasu governor da jama'a kan lallai sai na rushe company na na Magwan." Tace." Abunda bazai yiwu ba kenan lallai me citta Ashe yanan nan da bak'ar zuciyarsa. "
Granny ta sauke ajiyar zuciya tare da fadin. " Allah wannan bawa naka kai ka hallice shi kanai ka dora masa nauyin wannan dukiyar da ta hau kansa ina rik'on ka ka dafa masa cikin al'amuranshi ka tsare shi daga sharrin mahassada."

Ta k'arashe maganar tana shafa kansa cike da tsantsar soyayya. Gyara kwanciyarsa yayi cikin kujerar ya lumshe idonsa yaji dadin addu'ar da kakarsa tayi masa a yanzu bashi da wacce ta fita a duniyar nan sai dangin mahaifiyar sa da ba wani sha kuwa yayi dasu ba, granny tace." Ina Neman alfarma daya a gurinka." Bude idonsa yayi amma be kalleta ba, tace." Abunda ka kudurta kan Alhaji Hashimu ka hanye shi in ya kara sai ka dauki mataki." Kallonta yayi da jajayen idonsa yace." Kin samu amma da bakin ki kika ce idan ya k'aramin wani Abu in dauki mataki ko."? Granny ta daga kanta tana murmushi yace." Shikkenan ya wuce." Dariya tayi tace." Ho!! Dan nema kai dama soja ka zama da wannan halin naka." Tab'e baki yayi kawai ya koma ya kwanta bai ce mata komai ba. Tace." Bari in sa A kawo maka abunci ko." Girgiza kai yayi kawai har yanzu idonsa na lumshe. Tace "me yasa to."? " b'acin rai ba zai barni ba." Granny ta mike tsaye tana fadin." Dole ko kaci abunci towo ne miyar kuka." Bude idonsa yayi da sauri yana kallonta yace." Sai dai kici abunki ko kin sa an kawo min bazan ci ba." Granny ta wuce kicin tana fadin." Dama si tsokanar ka nake Abunda nasan ba cinsa kake ba, aikuwa ka bar dad'i." K'aramin tsaki yaja afili yace ." wai towo fad'ar sunansa ma a baki babu dadin ji malam Bahaushe kenan.

Wata lafiyyaye jolop rice wacce taji kayan lambu gami da kifi bushashe granny ta kawo masa cikin plate ta aje masa gabansa kamshi da take ne yasa ya bude idonsa tare da Dan tsurawa abuncin ido kad'an yace." Wannan."? Granny tace idon MA tambayi ne." Murmushi yayi kawai ya d'auko cokali yana juya ya abunci yayi bisimillah ya fara ci a nutse.
Granny ta gyara zaman ta sosai tana yi masa labari duk Dan ta d'auke hankali sa ya ci abuncin sosai DOMIN San *Amjad* cin abunci bai dame shi ba."
Cokali biyar yaci ya aje ya ya go tissue yana goge bakinsa . B'ata fuska granny tayi tace." Ka koshi ne."? Gyad'a kansa yayi yana k'okarin Mik'ewa tsaye. Tace." Kai kam matarka zata sha fama da kai wallahi abunci ma sai kayi masa felek'e kace wancan kace wannan. Yana tafiya yake fadin." To ke granny wa ya fada miki ni zanyi aure ke kadai kin ishe ni zaman duniya."
Wani tayi masa tana hararsa tace. " sai kayi kuma aure kamar kayi ka gama domin da kaina zan nemo maka matar cikin 'yan uwa da abokan arziki.'' Murmushi ya saki yana k'okarin futa dafa parlor yace." Ki nemo wa ni dai amma bani ba kamar ni zaki nemo wa mace kuma wai 'yar kano never. " tace." Sai kayi ni wannan turanci ba jinsa nake ba." Dariya yasa yace." Ni na tafi sai kin sake gani kuma Nazo kika kara min maganar aure to na bar zuwa gidan ki." Granny tace." ahaf!! Sai dai ko in baza ka zo ba WALLAHI na ma gano maka matar aure yarinyar kyakkyawa mai hankali nan makotanmu." Fucewarsa yayi yana mamakin granny wai shi zatayi wa aure lallai ta d'auko da zafi. Yana futa su Rambow suka rufa masa baya dama duk suna tsaye bakin kofar parlor.

*******

Asubah ni na riga kowa tashi cikin gidan tun kafin na mike zaune naji wani damshi a kasana sosai kuma nasan ko sati banyi da yin wankan tsarki ba. Cike da mamaki na mike zaune ina tunano mafarkin da nayi da guy din nan. Gabana ya dinga fad'uwa lokacin da na tuna gani tare dashi a gado daya muna cikin bargo daya muna rungume-rungume gami da tsotse-tsotse yana

shan harshena tare da murza min nonuwana ni kuma na kama gaban shi ina ta ja shi kuma sai nishi yake, kamar dai yanda yayi min lokacin da muka kwana a gidan shi.
Istigifari na fara yi Cikin zuciya ta kamar wacce ta aikata zunubi nan take na fahimci cewar mafarkin da nayi ne ya jawo min zubar ruwa a gabana. Cikin sauri na tashi domin bana so kowa ya tashi nasan dole sai na tsarkake jikina kafin inyi sallah. Futa nayi waje anata kiran sallah asubah na  dauki k'atuwar buta na jawo ruwa a rijiya a ganina zai fi dumi saboda sanyin asubah da ake zabga wa haka ina ji ina gani na shiga band'aki na fara zubawa jikina ruwan sanyi. Ina Wanka ina tsinewa guy nan a ganina duk shine ya jawo min WANNAN masifar. Motsi naji daga soro na gane Yaya Aminu ne zai futo daga shagonsa, gabana ya fad'i da sauri na jawo zanina na d'aura na zura rigata had'e da sanya hijab na futo ina zare ido. Yana tsaye da buta a hannunsa da alama ni yake jira na futo, ya Watson min kallo tare da fad'in." Wankan me kikayi da asubah. Jiya ina shigowa Umma take fadamin zazzab'i kikeyi shine kike Wanka da ruwan sanyi  nema mana masifa ko." Raina ya b'aci da jin abunda Yaya Aminu yake fada haushi yasa ni ina tafiya nake bashi amsawa da cewar." Wankan tsarki nayi domin bana son sallahr asubah ta wuce ni." Aikuwa karaf! A kunne Umma ta futo itama DOMIN d'aura alwala cike da mamaki ta zuba min ido tana nazarina. Ni ko na wuce jikina a sanyaye domin dai nasan Umma da saka ido akan 'yayanta tasan lokotan da muke jinin al'ada ni da Mimi kuma tasan kwanakin da muke in mun kare.

*20/October/2009*
[11/1, 10:55 PM] .: BintaUmarAbbale👄: *BABBAN YARO*

mallakar_BINTA UMAR

LITTAFIN MALLAKI NA NE KUN BIYA KUD'IN KARATU NE KAWAI DUK WACCE TASAN ZATA FUTA DASHI WAJE DON GIRMAN ALLAH TAYI MIN MAGANA NA DAWO MATA DA KUDIN TA.

*25*

Zuwa yanzu na fara tsinke wa da al'amarin na gaji da dukan k'ofar gami da zurga-zurga jikina yayi mutukar sanyi ganin da nayi k'arfe goma sha biyu na dare tayi zama nayi jikin kofar tare da takure jikina guri guda zuciya ta tana min sak'e-sak'en abubuwa da dama akan zuwana gidan domin nima sai yanzu na fahimci wautar da na tafka, a hankali na ji ana k'okarin bude kofar a shigo na mike Zumbur, ya bude ya shigo muka hada ido dashi, babu komai a jikinsa sai shout nickar k'irjinsa na kalla nayi saurin kauda kaina, zuciyata tana bugawa, ko kallona baiyi ba ya wuce ciki na bi bayansa da kallo yanda yake tafiyar sa ma zaka fahimci jarumi ne, toilet naga ya nufa naja tsaki a fili yanda zai ji, mintuna goma ya dauka a cikin toilet din ya futo kugunsa daure da towol me fad'i da wani rataye a wuyansa, gaban makeken dressing mirror dinshi ya nufa yayi shafe-shafen sa naga ya mike, da sauri na d'auke kaina, murmushi yayi a zahiri yace" daga baya kenan Ashe duk kallon da nake masa yana ganina ta mudubi inda nake naga ya dirfafo na kalleshi da idona dake k'ek'ashe nace" idan kaci ka d'an halak ne kai ka bud'e min kofa na futa, aikin banza da wofi kawa.... Kafin in k'arasa magana ta ya k'araso gurin ya sanya 'yan ya tsansa biyu ya d'ad'e min bakina da sauri ya rik'e leb'ena na k'asa dake min zugi na zuba masa idona dake k'okarin kawo ruwan hawaye ina mai dasu. Kallona yake shima fuskar sa a sake yace." K'ara cewa tak!!!! Kiga abunda zanyi miki a gurin nan." Shiru nayi tsoro na shiga ta, wani shashe na zuciyata na fad'a min da cewar "kar ki yarda yaga gazawar ki Asma'u kin manta abunda yace miki d'azu mummuna!!!! Kallonsa nayi a wulakance na bude baki zanyi magana naji tuf!! Ya tofo min miyau na bakinshi cikin nawa bakin. Da sauri na fara tattaro wa zan zubar lura da yayi da haka yasa ya mik'a hannunsa guda ya dafe min bakina tare da fad'in" Shanye shi yanzu ko in baki abunda yafi shi kisha wallahi ". Fik'i-fik'i nayi da ido ina kallonsa ya dantse min bakina cikin tafin hannunshi gashi ya daga kaina sama da d'aya hannun nasa. numfashi ma da k'yar nake futarwa, ganin ina Neman halaka yasa na shanye miyau din babu shiri. Yana fahimtar na shanye ya sake ni yana watsa min mugun kallo. Idona jazur nake kallonsa ina mai da nuffashi zuciyata a tunzure nace." Allah ya isana wallah.........hasken dakin ya kashe kafin in k'arasa magana ta ya matse ni jikin kofar da k'irjinsa gabana ya dinga fad'uwa fat!fat!fat! Naji yana gogo min gashin fuskarsa a kunci na cikin wani irin salo naji saukar numfashin sa a kunnen na yace." Nasan kin raina hukuncin da nayi miki saboda na lura bashi kike so ba, shiyasa kika kasa tafiya gida, budurwa kamar ki ki dinga yawon zuwa Neman maza da nayi tunanin kamilar macace tun farkon fara ganina dake Ashe ba ita bace, da kanki kin kawo min kanki har gidana kinga kuwa baza kiyi daraja ba, zan bugawa kaina buk'ata ba tare da ko kwabo ba nasan na taimake ki tunda na cire miki damuwa, Amma ina so ki san wani abu d'aya duk inda nakai ga bukatuwa da mace bana neman second hand sabuwa nake nema wacce bata san namiji ba, kin kirani Dan iska banza lalattace Mara tarbiyya ba d'an halak ba, duk da wannan bakin naki me kaud'in tsiya" yafad'a tare da sanya hannu yana murza min leb'e cike da mugunta gashi ya matse ni jikin bango ya cigaba da cewa, "ban nan kin wulakantani a gaban yarana da 'yar uwarki duk hakan be miki ba kin biyo ni gidana kina zagina, meye alk'ata dake ne."? Ya fada da k'arfi ta tare da sakina na fad'i a gurin.

Tsuguna wa yayi kusa dani tare da d'ago fuskata da hannshi guda ya tsuramin jajeyen idonsa yace." Ki fada min meye alk'ata dake yanzu me kike so nami ki meye yake damun ki a kaina bayan kin fada min kome sai in barki kiyi tafiyar ki."

Jikina ne yayi lak'was domin bani da abunda zan ce masa bayan haka kuma k'arfina ya Riga ya kare tunda ya kusanta jikinsa da nawa na nemi kuzarina na rasa, kallonsa kurum nake narasa tace wa. Mik'ewa yayi da sauri ya daki! Kofar dakin da kafarsa guda ya juyo kaina a zafafe! Yace." Answer me" shiru nayi tare da sunkuyar da kaina k'asa yace." Ok baki da amsa kenan ? Yanzu na fahimci tsabar iskancin ne da iya samun guri irin naku 'yan matan kano ko ni kamar ni!!!!*Amjadu* ki iya bud'ar baki ki karani da Arne!! Ki kirani da banza oh! my god!!!!" Yadda ya fad'i maganar a zafafe! Yasa na fahimci ransa a b'ace yake juyawa yayi yana kai kawo a dakin, na dinga binsa da kallo cike da tsoro, da sauri! Ya dawo inda nake. Ni kuma nayi kasa da kaina gabana na lugudan duka. Tsuganawa yayi a karo na biyu muryarsa a cunkushe yace." Ina so yanzu ki bude bakin sosai yanda zanji ki bani hakuri kan abunda kika min idan kin k'i yanzu in nuna miki waye *Amjad"!!!* Cikin zuciyata nace" Wallahi bazan bayar ba, nima si kamun laifi daka tab'a min jikina idan hakuri ne sai mu bawa juna. Abunda ya kamata in fada masa kenan a zahiri to bakina yayi min nauyi bayan haka kuma yayi mugun kwarjina ta yadda ma idan na bud'e baki zanyi magana dole muryata ta nuna. Ina Cikin rad'ani. Kallon-kallon muke dashi idon shi kyam! A kaina nawa ma haka. Yace" zan kirga goma idan baki bani hakuri ba kome ye ke kika jawo wa kanki". D'auke kaina nayi inanan kan bakana. Yafara lissafi kamar haka." 1 2 3 4 5 6 7 8 9 .... Ya maimata 9 din sau biyu yana kallona naki kallonsa ina kallonsa ya girgiza kansa tare da murmushi Wanda kana ganinshi kasan na mugunta ne, bai k'arasa 10 d' in ba ya mik'e da sauri nima na zabura! Zan mik'e hannu guda ya sanya ya d'auke ni a kafad'arsa k'aton bed din ya nufa dani, na dunga dukan bayansa na kasa cewa komai.

Jefar dani yayi kan bed d'in na yunk'ura da sauri zan tashi ya danne ni da hannunsa guda cikin yanayin duhun d'akin naga yana girgiza kansa yace." Baki da wannan damar yarinya kin shigo hannuna ni kad'ai nasan irin hukuncin da zan miki." Kafin in ankara ya keta! Rigar jikina dana abunka da dinkin dake da babban wuya gashi duk hannun rigar a tsage. Na dawo daga ni sai breziya da dogun siket bayan wandona na ciki. Cikin zafin nama! Ya d'aga kafafuna sama yana k'okarin zare min under wear na na dinga harbe-harbe da kafafuna hannu guda yasa ya rike mun k'afafuna duk biyun d'aya hannun nasa kuma ya zare min siket ya jefar k'asa, k'okarin cire mun part yake, na zabura!! Da k'arfi na kwala k'ara tare da fad'in" Kar ka bud'e min jikina ka bud'e min zan maka abunda baka tab'a tsammani ba a rayuwa sai na bar maka tabo a rayuwar ka."!!!!!!!!!!.

Damtse min baki yayi ya tsura min idonsa da sukayi jazur dasu nima nawa sunyi mugun ja saboda tsoro da fargaba kwata-kwata ma bana jin wani feelings nagama tsorata domin ina mutukar ji da budurci na, ganin ya shagala da kallona ne yasa na fara harbe-harbe da k'afafuna nasamu nasarar cire guda daga hannunsa na yunk'ura zan mik'e zaune. Hannunsa yasa ya tan kad'a ni na fad'a bed din rigingine,, wani miskilin murmushi naga yanayi yana kallonta yace." Jarumtar ki na bani sha'awa sosai ban tab'a ganin abunda ya saki kuka ba, owk yanzu zan baki kuka babu duka babu zagi.". Yana gama maganar sa ya ware min cinyoyina sama! Na kurma ihu!!!" Wayyo Allahna a kawo min dauki"! Oho! Ihu bayan hari kenan ni kaina nasan babu mahalukin da zai jini a wannan tafkeken gidan balle kuma mak'ota. Pant dina ya zare ya jefan k'asa, na rintse idona. Cike da takaici da tsantsar b'acin rai! Nace"ka tafka mummunar kuskure

a rayuwarka!!!!! daga kaina zaka daina wulak'anta ko wace mace me daraja". Na k'arashe maganar muryata na karkarwa.... Yace." Bakin ki yak'i mutuwa ko? Ok dama Ashe kina cikin mata masu daraja Ashe"? Ya fada da rainin hankali" haure sa nayi da k'afata ya rik'e da kyau. Yacigaba da cewa." Na lura kamar kin fara karaya naji kina rawar murya, kin wuce time dinki 'yan mata masu daraja." Duk cikin duhu muke wannan artabun ni dashi, kafin in ce komai naji saukar hannunshi a gabana!! Na zambara! Ihu!!! Ina yunk'urin Mik'ewa zaune still dai ya maida ni da hannunshi guda na fadin bed d'in.Ihu! Nake kurma wa yayin da nake jin ya tsansa na yawo a gabana, ya dago kanshi tare da girgiza min cinyoyina a hankali yace Shiiiiiiiii!! Na d'auka ai jaruma ce a ko wane fanni kar ki bani kunya mana mace me daraja." !!!! Wasu zafafan hawaye ne suka soma zubo min a fuskanta naji dad'i da dakin ya kasance da duhu babu haske balle yaga fuskanta ya karewa gabana kallo ko da wasa ban yarda sautij kukana ya futo fili ba,, Ina jinsa yana tamin iskanci da gabana na share shi, ina jin radadi a zuciyata!!! Babu zato naji ya kafa kansa a gurin yana tsotsa!!

Wata irin zabura! Nayi ina mik'a!! Tare da k'okarin funcike kansa daga gurin. Ya buge min hannu da k'arfi ya cigana da tsotsar gurin . Tuni cinyoyina suka fara karkarwa karrrr!!- karrrr tsigar jikina ta dinga mik'ewa yammmm!!! Wani irin mugun d'adi na ratsa min k'wak'walwata nuffashi na fara saukewa , ina cije leb'ena, hummmm!!! Ajiyar zuciya kawai nake saukewa daki-daki tuni jikina yayi mugun sanyi na daina yunk'urin k'watar kaina sharaf!! Na sakar masa jiki yana abunda ya ga dama dashi, hannunsa ya Dora kan breast dina guda yana murzawa, da sauri na dafe hannun nasa hannuna na karkarwa bakina na rawa nace." Ka bari!!!!! dain.....ahhhh!!! Wayyo !Mimi na!!!!!! " na k'arasa maganar tare da had'iye wani miyau da yayi min saura a bakina lokacin da naji bakinsa kan nono na guda yana tsotsa, still har yanzu hannunsa guda na k'asana yana min wani irin Abu, k'anshi na rik'e da mugun k'arfi ina sakin Ihu!!! Wanda ni kaina nakasa gane ihun meye dad'i ne ko na bakin cikin abunda yake min ne.

*Amjad* kuwa ganin tazo hannu yasa yayi murmushin mugunta tunda ya riga ya gama fahimtar inda ta dosa kawai ya fara k'okarin zura ya tsanshi cikin headquarter d'in. Sai da ya kusa suma saboda yadda yaji gurin a matse tsam!! Ga wani ruwa na zurarowa daga gurin, wasa yake yi da hannunsa a gurin cikin dubara yake so ya tura ya tsansa, ban san sanda na fashe da kuka ba ina rok'an shi da ya daina min. Domin a lokacin ji nayi zan iya mutuwa hankalina ya dusa she sam na kasa gane a duniya nake ko a lahira kuka sosai nake ina rok'ansa abun mamaki kuma bai rik'e ni ba ina da damar da zan kwaci kaina daga hannunsa amma na kasa wannan yunk'urin, sai aukin kuka kawai da nake.

Ya tsansa ya cusa ciki ta k'arfin tsiya, na kwala wata irin k'ara tare da k'ank'ame kanshi dake saman k'irjina na rik'e tamau! Ina nishi!!!! Ga hawaye na zuraro min.

To shima nashi b'angaran ya shiga d'imuwa da damuwa gami da tsantsar sha'awa lokacin da yaji gurin a cike dam!! Ko ina tsoka ga wani uban taushi da d'umi da yake ji, cikin futar hayyaci ya fara on and out da ya tsanya a ciki yana sakin nuffashi lokaci guda jijiyar shi ta harba babu abunda yake so in ba sex ba ya lura yarinyar budurwa ce cikin 'yan Matan ma Wanda suka

amsa sunan su. Sosai yake murza ya tsansa a gurin.yana nishi kokarinsa kawai ya samu realizing, kawai ya so yai wa ma yarinyar mugun ta ne, sai reshe ya juye da mujiya yanzu ta kanshi kawai yake.  Ina ihun kuka yana sakin nishi!! Kowa shi yasan halin da yake ciki... Brest dina da suka sha luguda a hannunsa yayi wa wata irin matsa tare da tura hannunshi ciki sosai ya kifo kaina yana wani irin nuffashi ina jin yanda zuciyarsa take bugawa......minti biyar tsakani ya mik'e ko kallona bai yi na ga ya shiga toilet....... Yana shiga na bud'e cinyoyina sosai ina nuffashi wata muguwar sha'awa nake ji cikin gabana namun wani irin tsiko duk da rad'ad'in zafin da yake min bai da me ni ba ni dai burina kawai ya cigaba da min abunda yake min ko na samu sa'idar abunda nake ji. Sosai na ware cinyoyina kamar wata 'yar kaciya wasu irin zafafan hawaye na zubo min.

*23/October/2019*
[11/1, 10:55 PM] .: *BABBAN YARO*

*Mallakar_BINTA UMAR*

_*LITTAFIN MALLAKI NA NE KUN BIYA KUD'IN KARATU NE KAWAI DUK WACCE TASAN ZATA FUTA DASHI WAJE DON GIRMAN ALLAH TAYI MIN MAGANA NA DAWO MATA DA KUDIN TA.*_

Whatsp numbar
0809965176
07084653262

Account numbar
1013851874

*26*

Motsin kirki na kasa yi ballanta in mik'e in gyara jikina kwata-kwata na rasa abunda yake min dad'i cikin zuciyata hawaye ne kawai yake zuba daga idona, bud'e kofar toilet din ne ya dawo ni hankalina da k'yar najawo bedshirt din da ya cukurkude na rufe jikina tare da rintse idona kwata-kwata bana son i n kalli fuskarsa , haske ne ya gauraye dakin, nayi saurin yin rufda ciki sautin kuka na futa a hankali. Ko a jikinsa bed din yake dan harara tare da tab'e bakinsa ya wuce jikin wardrobe d'insa domin Ciro jallabiyar sa, sabuwa dal ya Ciro a ledar ta ya sanya ash colour ce me yankakken hannu, ya tsaya gaban mirror ya fesa turare kamar yanda ya saba. Cike da karsashi ya durfafo bed din nasa da niyar kwanciya. Zaman da yayi a gefan gadon da kuma yanda k'amshin sa ya cika min hanci yasa na gane ya kusa dani sosai. Na mik'e zaune da sauri idona yayi ja kamar gauta! Bakina a bushe na kalle shi tare da fad'in"Wallahi sai kayi nadamar abunda ka aikata a gareni na rantse maka da girman Allah baka ci bulus ba sai na dauki fansa na fada maka tun farko dama daka kaina baza ka kara ketawa ko wace mace rigar mutumci baaaa!! Kallonta yake fuskarsa d'auke da murmushi yace." Kina nufin zaki kaini k'ara koto alk'ali ya hukunta ni ko me? Ko kuma zaki dauki hukunci a hannun ki? Kina maganar na keta miki mutum ci ta ina ? Ki fad'a min wane mutum ci na keta miki, ke kika keta rigar mutumcin ki da kanki so nima na samu saura saboda haka kar ki d'ora min hakki". Ya k'arashe maganar tasa babu abun damuwa a ciki. Hakan da yayi ya k'ara fusata ni, cikin tsawa nace." Babu wani d'an sanda ko alk'ali D's Zan kaiwa karara ki ni nan da kaina zan dauki hukunci saboda haka ka zauna cikin shiri d'an iska kurrum. " ranshi a b'ace ya kalli d'an ya tsanta da take nuna shi dashi cike da tsiwa take maganar, yace." Ki d'auke d'an ya tsayan ki yanzu in karya shi wallahi." K'in daukewa nayi na cigaba da nuna shi ina fad'in" kome kud'in ka da mulkin ka kome d'aurin gidin ka a k'asar nan nafika duk na San hanyoyin da zan bi gurin ganin ka wulak'anta." Hannunsa ya kawo da k'arfi ya bude min d'an ya tsana da nake nuna shi, nayi k'ara cike da jin zafi yanda hannun gaba d'ayan sa ya sage."

Fuskarsa na kalla naga ya sha kunnu sosai yace." Saboda kina da lasisi a garin kano kin gagara kina da d'aurin gindi gorin shawagabbanin k'asa kike wannan ikirarin a kaina duk abunda zakiyi kije kiyi ina nan ina sauaran ki. Ya cigaba da cewa." Ni duk abunda zanyi ado ne a gare ni ke kuwa fa? Ke zaki barwa kanki tarihin abun fada da 'yayan ki da jikokin ki, babu ruwana ina zaune kika kawo min kanki har gidana kina rigima da Masu gadi dole sai kin shigo hakan bai ishe ki ba ki shigo min har bedroom." Ya saki wani guntun murmushi yana dan shafa sajansa ya cigaba da cewa" tun farkon zuwan ki da abunda ya faru a tsakanin mu ina da vedion sa so tunda kin ce haka ma gobe idan Allah ya kaimu zan watsawa duniya su san ke wacece, in yaso sai kiji dadin d'aukar mataki." Kuka na fashe da shi sosai tare da mik'ewa tsaye! Nace."

Idan baka futa da vidio ba baka kaunar Allah  baza ka nuna min cewa kai d'an halak bane sai naga vedio nan na yawo a duniya sannan zan yadda da tacewar ka a fanni bariki,." Na k'arashe maganar ina gunjin kuka lokacin ji nake ina ma zan samu abun duka Dana dunga dukan shi ko na samu zuciyata tayi sanyi daga azabar da ya gana mata. Gani nayi ya kwanta plate kan bed din yana lumshe idonsa Sam! Abunda nake ma be dame shi ba." Da sauri na  dauki pillow na jefa masa da k'arfi! Ya bude lumsassun idonsa yana kallona a zuciyarsa yake fadin" wannan yarinyar 'yar bala'i CE, da alama tafi ni bala'i.  D'aya pillow na d'auka na jefa masa da k'arfi nace." Yau zaka San ka tab'owa kan ka bal'ai." Dressing mirror d'insa na nufa ina rangaji ga bedshirt nan nad'e a jikina yana hard'e ni, kamar zan fad'i na fara d'ebo kwalayen turaran shi had'e da kwalabe robobin mayukan shi cream and lotin kamar wata mahaukaciya nayi kansa na fara jefa masa su ina aibata shi tare da cin alwashi a kansa iri-iri, in ka gani a lokacin zaka ce sai na rasa ruwan hawaye saboda yanda suke kwarara.

Da sauri ya mik'e ya dura daga k'asa dariya yake sosai yana Neman hanyar guduwa tare da fad'in"Lallai ashe da mahaukaciya nake zaune ban sani ba." Kofar ya nufa da sauri yana lalube key jikin 3quoer din dake kasan jallabiyar jikinsa nan ya b'oye shi,, na bishi da gudu ina jifansa tare da fad'in" baza ka San da mahaukaciya kake zaune ba sai ranar da nayi maka illah a RAYUWAR ka."
 Da k'yar ya ciro key d'in ya bud'e d'akin ya futa, kafin ya ja kofar ya rufe ni nayi wuf!! Na futa, na cigaba da dukan shi da abubuwan da suke hannuna ina kuka kamar babu gobe, nace." Dama kace sai ka sani kuka to ka sani kaji dad'i hakkina kuma da ka d'auka Allah ya isa ban yafe ba." Kare jifan da nake masa yake da hannunwan sa, Sam!! Baya so ya kara kusanta jikinsa da yarinyar shiyasa ya kasa d'aukar mataki a kanta, amma yana ganin dole sai yayi hakan sannan zai samu ya shawo kanta,  da sauri ya matse ta jikin kofar tare da kafe ta da lumsassun idonsa masu dagula wa mata lissafi, wani irin cool voice yayi amfani dashi gurin yi mata magana, Yace." Kiyi mana shiru!! Ko bakin San dare bane? Hummm ok tunda ba kyaso in futa da vedio bazan futa dashi ba shikkenan, amma nima kar ki k'ara zuwa inda nake, ban sanki ba baki sanni ba, kowa yaje yayi sangar shi, kikara kara zuwa inda nake to ranar za muyi fad'an k'arshe dake kuma in futa da vedio na abunda ya faru a tsakanina dake, saboda haka babu ruwan ki dani." Ya k'arashe maganar tasa tare da d'an hura mata iskar bakinsa a fuskar ta.

Asma'u ta shiga wani yanayi Wanda idan ba Allah ba babu Wanda ya isa ya futar da ita daga cikinsa sai shi Wanda yayi silar shigar ta yanayi *Amjadu* ko be fad'a cewar ta futa daga sabgar sa ba ya zama dole ta futa daga sabgar sa saboda ta gano tarayyar ta dashi bata da wani amfani dole tayi nesa dashi da rayuwar sa.

Miyau na kalato na tofa mishi ya sauka gefan bakinsa nace." Ni sake ni ko ka kafad'a ko baka fada ba dole in futa daga sabgar ka, yanzu ma abunda ya kawo ni gidanka in dauki handbag dina shikkenan saboda tsabar mugunta ka kulle ni a daki a kori 'yan uwana, kar ka manta da cewar    nayi rantsuwar sai na dauki fansar abunda kayi min".

Girgiza kansa yayi kawai yana sakin wani  miskilin murmushi abunda yake gudu shi ya afku a halin yanzu babu abunda yake mutukar sha'awa illah yaga yana tsotsar bakinta shiyasa tun

farko yak'i kusantar ta duk wasu zantukan ta da takeyi na shirme ne Sam basa gabansa yasan duk kuri take da nuna ita lallai kar yaga damarta don haka be dame shi ba.

Lumshe idonsa yayi had'e da tallafo fuskar ta babu zato taji bakinsa cikin nata. Damtse bakina nayi tare da cije hak'orana ina ture shi. Hannusa ya zura cikin bedshirt din yana shafo mazaunai na, take na bude bakina, zan kurma ihu! Hakan ya bashi damar cafko harshen ya ya fara tsotsa kamar Wanda ya samu sweet.
Bedshirt din ya silale ya fad'i k'asa jikina yayi lub'us babu jarumta ta ko ta kwabo a tare dani, ina ji ina gani ya d'auke ni cak ya shiga dani bedroom din ya shimfid'e ni kan bed tare da yi min rumfa da faffad'an k'irjinsa ya jigaba da yin kissis dina, ni kuma nakasa tab'uwa kaina komai domin in kwaci kaina lumshe idona kawai nayi ina jin shigar wani yanayi me wahalar fassawara a jikina.

*Amjad* ya gane abunda yake damun yarinyar kenan shiyasa ta gaza hakuri take ta neman fituna dashi, ya lura yarinyar tana da mutukar k'arfin sha'awa Wanda irinsu ne idan basu samu jajurtattun maza ba suke shiga wani hali, ya zame masa dole yayi nesa mutuka da ita saboda a zuciyarsa na mutukar tausaya mata lura da yayi da rashin galihu gami da taulaci a tare da ita, idan wani Abu ya afku a tsakanisa da ita mahaifiyar ta tana iya shiga wani hali,ita kanta yarinyar tana iya shiga wani hali yanzu k'uruciya CE kawai take damunta Babban abunda ya fi kamata da ita shine kawai tayi aure ta huta Idan ba haka ba rayuwar ta tana iya shiga cikin wani irin hali.

Kissing din ta yayi sosai ya rage wa kanshi zafi sannan ya sakar mata bakinta gami da sauka daga bed din ya futa daga dakin ma gaba d'aya ya kulle ta da key, ya gwammace ya kwana a parlor domin gujewa abunda kan iya zuwa ya dawo.

Nafi minti goma tun bayar futarsa ban iya d'aga ko da Dan yatsa na guda ba, idona a tsaye k'am! Yana kallon rufin dakin. Na ma rasa wane irin tunani zanyi, jiki a sanyaye na mik'e zaune ina duba jikina babu komai sai briziya itama da ita gwara babu tunda duk ga nonowana nan a waje sun fito pant kuwa dama tuni an share babin sa, wato d'azu bedst din na saki a kasa ban sani ba, wasu hawaye suka zubo min masu zafin gaske, muryata na karkarwa nace." Ka zame min annoba a rayuwa ta, ya zama Dole inyi nesa da kai ya zama dole Ubangijji ya bimin hakkina daka d'auka nayi da na sanin saninka a rayuwata yau nayi dana sanin zuwana wannan duniyar, Ya Allahu ka yafe min, astagafirullahi Allah."!!!!!!
Na k'arashe maganar ina sakin wani marayan kuka na tsantsar tausayin kaina.
Sai da nayi kuka me isata sannan na mike a daddafe na shiga toleit d'insa na hada ruwan zafi sosai na fara Wanka tsarki inayi ina kuka tare da nadamar abunda na aikata nace" Ubangiji kai ka hallice ni kasan ba laifina bane Kaine ka hallice ni da wannan hallitar ya Allah ka saukaka min, Wanka nayi sosai da soso da sabulu na futo ina matse fuska tsayuwa nayi tsakiyar dakin ina tunani rigata dai ya yaga min, tunani na ya bani in bude cikin kayan shi ko zan samu irin duguwar rigar da ya bani farkon zuwana gidan shi, wardrobe din na nufa na fara kici-kicin budewa tana budewa na fara ware ido kaya ne ko ita ina na lura ko wane kayan sawarsa a kwai

b'angaran sa, da k'yar na hango wasu tarin ledoji daure wasu kan wasu na fara birkitosu Allah ya bani sa'a na ciro wata a baya irin ta mutan Saudiya bata da ado sosai sai kad'an kamar bubu take na zura a jina  na dauki sabon hijab me hannu had'e da nikaf shima na farke daga ledar sa, kan dadduma na nufa domin yin sallahr magariba da isha Wanda suka wuce ni. Bayan na idar sosai na kaskantar da kaina gaban Ubangiji INA rokonsa da ya yafe min kuma ya yaye min damuwa ta, kwanciya nayi kan abun sallah ina lumshe idona tare da tunanin ko a wane hali su Mimi suke ciki  oho dadin da naji kawai Mimi bata koma gida ta koma gidan su Munnu nasan k'aryar da zamuyi wa Umma cewar a gudansu Munnu muka kwana. Haka na dinga sak'e sake gami da zancan zucci har aka fara kiran sallahr asubah  na mike da hanzari ina shirin shiga toilet din naji yana k'okarin bude kofar dakin, komawa nayi na kwanta had'e da takure jikina na rufe idona ruff nayi rantsuwar har in bar gidan magana tafarar baki baza ta kara hadani da shi ba, ya shigo a hankali INA jinsa ya tsaya a kaina tsawon minti biyu sai naji wucewarsa na bude idona a hankali naga ya nufi toilet nasan alwala zai dauro, motsin ruwan da yayi yawa ne yasa na fahimci cewar Wanka yake, minti goma yayi ya futo da sauri jin ana k'okarin tada sallah wasu sabbin kayan ya sanya jallabiya da gajeran wando ya futa daga d'akin nasan masjid ya nufa, nace" kullum cikin tsoron Allah amma a gefe guda ana aikata sab'on Allah."

Alwala na dauro Nazo na tada sallah ta, bayan na idar zama nayi ina karatun alkur'ani a zuciyata har gari ya soma haske sao danayi izu biyar sannan nayi addu'a na shafa, agogo na kalla bakwai da rabi na safe, tunda ya futa ban kara jin motsin sa ba, na mike raina a cunkushe na futa dama kofar a bude ya barta, yana kwance kan 3sitar duk tsayin kujerar tayi masa kad'an saboda k'afafun shi ma kan hannunta suka sauka, idonsa a lumshe yake hannunshi da carbi me bala'in kyau yana ja ,tsayuwa nayi a kanshi a cushe nace "sai ka tashi ka mai dani gidanmu ko kuma ka sanya a mai dani."
Bud'e idonsa yayi masu d'auke da son yin bacci ya zuba mata su. Kauda kaina nayi daga kansa domin Sam bana son in kara jin sha'awar sa cikin zuciyata so nake ma in ji zuciyata na masa muguwar tsana na har abada, zaune ya mike yana kallon a gogon dake daure a hannunsa, minti biyu ya dago kanshi yana kallona da idonsa Wanda babu digon kunya ya ciki  muryar sa k'asa-k'asa yace." Ki Bari 9:00 tayi yanzu Safiya ce bana futa irin wannan lokacin idan na muhimin abune zai futa dani ba." Hannu na daga masa da sauri! Nace." Wannan ba hujja bace, ni yanzu bana neman wata doguwar magana da kai abunda kayi min na barka da Wanda ya hallice mu."  Kansa ya sunkuyar k'asa yana dan murmushi ni kuma nayi masa tsaye a ka had'e da rik'e k'ugu d'ago kansa yayi yana kallona a karo na uku yace." Shikkenan kije yanzu zan zo sai in Kai ki da kaina." Nace." Babu inda zan matsa daga gurin nan." Sai ka tashi tunda na futo daga wancan dakin bazan kara komawa ba." Hannunsa ya d'aga min duk biyun yace." Ok ok naji. Kina min hayaniya aka yanzu zan tashi." Nace ya fi maka." Minti biyar ya kara a zaune ya mike da sassarafa ya shiga d'akinsa, tsaki naja ina watsa masa muguwar harara. Ba tare da sanja kaya ba ya bude kofar ya futo tare da fadin" muje kar ki cinye ni." Yafad'a yana nuna min hanya, wuce wa nayi fuskata a murtuke, ina futa naga ya ranshi tsaye a bakin kofa wani mugun haushin su ya kamani na dinga watsa musu mugun kallo nayi wuce wata, INA kallonsa ya tsaya dasu suna magana, sannan naga ya tawo in da nake yana taka k'asa kamar zai tsaga ta. Wata mulmulalliyar mota naga ya bude ya shiga yace." Shigo. " kofar baya na bude na zauna bai ce

min komai ba yaja motar me gadi ya bude masa muka futa daga gidan.sai sannan na sauke ajiyar zuciya. Tafiya muke babu Wanda ya kula Dan uwansa sai dai mu hada ido ta mirror dashi hararace take rabumu dashi, Sam! Fuskarsa bata nuna b'acin rai ko kadai. Gani yayi ya dauki hanyar Gidanmu nace." Banan zani ba." Ta mirror ya kalle ni a nutse yace." Banan zaki fa kamar yaya."? Nace." E haka nace k'oki zaka kaini gidan 'yan uwanmu in kasan ni." Yace." Ni ko nasan koki unguwar kakannina CE, abun da na kasa fahimta shine kince ba gida zakije ba INA so ki fada min inda zakije ko kuma yanzu in juya dake in da kike futo. Fuskarsa na kalla naga yanda ya had'e ta tamau! Tsoro ya kamani nace." Gidan su Mimi ne tana can tana jirana." Cike da zargi yace." Ok kina nufi dama ba gidan Ku daya da ita ba." Nace" wannan duk ba abunda ya shafeka bane kawai ka kaini inda nace." Yace. " idan nak'ifa"? Shiru nayi masa, gyada kansa naga yayi yace. " sam ban yarda dake ba wallahi amma muje gidan in da kaina kuma sai kin kirawo min Mimi sannan zan barki ki futa daga motar nan." Share shi nayi kawai. Ya kunna motar mu dauki hanyar zuwa koki.

Dai-dai kwanar gidan nace a sauke ni ya gyara parking tare da juyo wa yana kallona yace." Kira ta a wayarki ta futo mugani." Nace "bani da kudi a wayata." Dube-dube ya fara cikin motar wayarshi yake nema tana gida, dafe kansa yayi na minti biyu ya dago kansa tare da kallona, handbag dina na rike da kyau domin nan wayata take, ganin yanda nake dama- dama da ita ne ya sa ya fuzge ta daga hannuna ya fara zazzage min kayan dake ciki. Akwalar wayata ta fad'o k'asa batir din ya yayi nasa guri dama baya zama sosai jikin wayar sai nayi masa ciko sunkuyawa yayi ya dauki wayar yana dubawa ina kallonshi yana sakin wani munafikin murmushi, sauri kauda kaina nayi cike da kunya da takaicin sa, batir ya sanya ciki da dubara ya kunna wayar INA kallonsa ya fara laluben ma'adanar aje numbobo har yazo kan sunan Mimi inda nayi serving numbar da Mimina  ya danna kira minti biyu ta shiga har ta katse Mimi bata d'aga ba ya k'ara kira a karo na biyu tana shiga ta d'auka Muryar ta radau naji tana fad'in " Asma'u kiyi kokari ki futo daga gidanan Wallahi hankalin ummansu Munnu ya tashi jiya Umma tayi mata waya wai anan zamu kwana tace." Mata eh shine take tambaya ta ina kike." Wayar ya mik'omin ba tare da yacewa Mimi komai ba,na karb'a da sauri hannun mu na haduwa da nashi ko a jikina nace." Mimi ki futo bakin titi ganin nan kinjiiii." Tace." To ganinan zuwa." Kashe wayar nayi nasa a jikin jakata naki kallonsa, Wanda INA kallonsa tunda nafara magana da Mimi cikin waya yake kallona ta mirror.

Mintuna goma na hango su Mimi ita da Munnu suna sanye da hijabi har k'asa, Sam hankalinsa basu cewar ina cikin motar nan ba  tunda motar me tintac ce.
Kalle-kalle kawai suke suna Neman inda nake, kallonshi nayi nace." Bude min kofa ga sunan suna nema na." Kamar da dutse nayi maganar ya shareni  murya a sama nace." Kaji. "!!!!! Juyo wa yayi a hankali yana kallona naga ya Sosa kansa kad'an wani munafukin murmushi a fuskar sa, kauda kaina nayi Ina jijjiga murfin motar naji muryar sa a k'asa yana fad'in" Baby zanyi missing din wannan tsiwar ta ki sosai hummmm!! *Asma'u mata masu darajah.!!!* nayi saurin kallon shi jin ya ambaci sunana kamar shine ya rad'a min hararasa nayi kawai tare da d'auke kansa, ya b'ata fuskarsa yana kallona yace." Na tsani tsaki! A rayuwata na lura dab'iar ki ce hakan kan mu rabu dake kar in k'ara ji kinyi min tsaki." Cike da taikaci nake kallonsa nace." Me

zakayi min in na k'ara, ka tsaya kana neman magana dani kawai ka bud'e min k'ofa na futa." Tsurawa mata ido yayi yana kallon tare da lumshe ido. Takaicin sa yasa nakasa cewa komai na tsani wannan d'an iskan kallon da yake min.

Shiko nashi b'angaran yaso ta k'ara masa tsak'in saboda ya samu yayi kissing d'inta na k'arshe sai ya ga takiyi masa, shine dalilin da yasa kawai ya zuba mata idonsa yana tunanin ya zaiyi sa ita. Kwantar da kujerar motar yayi ya hauro kusa dani. Da sauri na takure jikina jikin kujera ina kallonsa a tsorace gabana ya fara dukan uku-uku. Fuskarsa yake matsowa da ita dab da tawa na rintse idona da k'arfi tare da fad'in." Kar kayi!!!! Ka bude min kofa na futa wayyo!!! Nace kar Kay.................maganar tawa ta katse lokacin da naji saukar bakin shi ana wa. Ya fara tsotsar harshe ne cikin zafin nama!! Ajiyar zuciya na sauke tare da sakin jikina kan kujerar ina lumshe ido hannusa yasa cikin nawa ya rintse da k'arfi daya hannun nasa ya tallafo kaina dashi sosai yake kissing dina kamar wani mayunwacin zaki!! Mintuna kusan biyar muka kwashe cikin wannan halin kafin dmya sake ni ya koma gurin zaman shi, ido jazur na ke kallon k'eyar shi na marasa me zanyi, da sauri na fara dube-duben can na hango su Mimi suna k'okarin juya gida domin sun duba ni basu ganni ba. Kuka nasa sosai nace " nace maka ka bude min ka bude min kak'i bud'ewa gasu can suna tafiya gida." Hannunshi ya zura ya bud'e motar ya d'ora min kudi dauri biyu a jikina ya gyara zamanshi tare da fad'in ." A sauka lafiya."

Da sauri na bud'e murfin motar na futa tare da watsa masa kudinsa kan kujera kamar zan kifa nabi bayan su Mimi.

*24/October/2019*
[11/1, 10:55 PM] .: *BABBAN YARO*

*Mallakar_BINTA UMAR*

*LITTAFIN MALLAKI NA NE KUN BIYA KUD'IN KARATU NE KAWAI DUK WACCE TASAN ZATA FUTA DASHI WAJE DON GIRMAN ALLAH TAYI MIN MAGANA NA DAWO MATA DA

KUDIN TA. _*

What's App number
08089965176
07084653262

Account numbar
1013851874
Ahamad Gwadabe
UBA BANK

*Duk Wanda yake da buk'atar cigaba da karanta littafin nan naira Dari uku ne kacal  sai ka tuntub'i numbobin waya ta gasu can a sama domin in fada maka yanda zaka biya*

*27*

Kallo ya bita dashi yana daga cikin motar ya d'an ciji lips d'insa na k'asa had'e da gyad'a kansa motar ya kunna a hankali ya bar gurin. Sai da nazo dab da su sannan na kira sunan Mimi da sauri suka juyu jin murya ta duk suka bini da kallo cike da mamaki, tambaye-tambaye suka tsaya zasuyi min nace ." Ku muje gida." Shiru sukayi da bakinsu muka kama hanyar gida babu me cewa komai. Sai da muka shiga gidan ne sannan gabana ya fad'i na fara tunanin wace irin k'arya zanyi wa Ummansu Munnu, tana kicin tana raba abun kari ta kalli a tsanake tace." Asma'u Ku futa tare da 'yan uwanki su dawo su barki ko da yake Mimi tace." Gidan Kawu Yunusa kika wuce ko." Da sauri nace. " Eh wallahi can na kwana  kuma da naje suka hana ni dawo wa wai sai na kwana." Dariya Ummansu Munnu tayi tace." Ai sun kyauta domin kuwa kema irin 'yar Uwar ki ce ba kya Kai musu ziyara shiyasa, nayi dariya cikin wayan cewa nace 'aikuwa suma haka suka CE." Tace." Sai Ku shiga ciki yanzu zan sanya a kawo muku kayan

kari."
D'akin Munnu muka shiga duka muka zube kan kujera hijab din wuyana na fuzge na aje shi gefe ina numfarfashi Mimi da Munnu sun ka zuba min ido kawai bakin su da alamar tambaya nace." Wai meye kuke ta kallona ne kamar wacce kuka kama da kwarto." Mimi tace." Ba Dole mu kalle ki Asma'u Allah ya baki nasarar d'auko jakar ki amma ga dukkan alamu an sha artabu da guy nan ko." ? Kafin in bata amsa Munnu tace." Ni rigar jikin ki ma nake kallo tayi min mugun kyau lallai Ashe soyayya kuke dashi tunda gashi har da yi miki siyayya." Nace." Kinga Munnu inda kina son rigar zan cire in baki ne kawai a yanzu bana bukatar wani Abu da ya shafi guy nan domin bashi da mutumci ko kad'an." Mimi tace." Allah yasa dai bai miki komai ba." Cike da takaici nace." Mimi jiya naga masifa a rayuwa domin ban yi tunanin zan dawo gida da budurci na ba wallahi jiya guy nan sai da yayi min sintir kamar matarsa haka ya dinga mu'amula dani." Dafe k'irjinsa sukayi baki na rawa Munnu tace." Laifin ki ne tunda yace kizo ki tafi kika k'i." Nace." Munnu guy nan sharrin sa yafi k'arfin sa kawai ki barshi a inda kika ganshi." Mimi tace." Lallai Allah ya tsare ki amma nima nafi ganin laifin ki Asma'u." Nace." Dole kice haka mana tunda kina sonsa."

Munnu ta kalli Mimi cike da mamaki! Nace hakane Munnu Mimi sonsa take tun ranar da muka fara ganinshi har da gudumawar ta ma naje gidan shi domin in fada masa." Dariya Munnu tayi k'asa-k'asa tace." Ki kai kanki dai ita me yasa Mimi dake tafi ki wayo bata je sai ke sarkin kankanba, tab!!! Gaskiya kin tsalle ke rijiya da baya." Nace." Ke dai bari Munnu dake d'an iska ne kuma wai sai ya zube min kud'i sai kace ce masa nayi su nake so." Tace. " suna ina kud'in"? "Na bar mishi abunsa cikin mota." Tsaki tayi tace." Kin kwafsa banza da kin d'auko abunki tunda jikin ki ya mora." Hararata nayi nace "in d'auka yace dama su nake so hummm sharrin guy nan fa sai ya baki tsoro ni kam jiya si na dauki darasi na rayuwa." Dariya kawai Munnu take sosai tace." Meyasa bamu ganki ba da muka futa bakin titi." ? Nace." Ni ina ganin Ku ai.". Ta ina kike ganinmu."? Nace." Ba kiga wata bak'ar mota ba a gefe."? Munnu tace." Au!!! dama kina cikin wannan azababbiyar motar."? Nace. " Eh mana ina ciki nayi-nayi ya bud'e yak'i sai da yaga kun tafi sannan ya bud'e min nan ma sai da nayi kuka." Munnu ta kwanta tana ta dariya tace." Lallai yau Asma'u kin had'u da Wanda ya fiki rashin mutumci tab!! Ammafa gaskiya guy nan ya burge ni ya kashe bakin rashin kunya." Nace." Munnu ke dai bari! Wallahi duk iskamcin ka akwai Wanda ya fika a duniyar nan." Mukayi dariya ni da ita, duk wannan hirar da muke Mimi na kwance taki tanka mana na kalli fuskarta naga kamar tana cikin b'acin rai! Girgiza kaina nayi kawai saboda nasan abunda yake damun ta. Haka aka kawo mana abun kari muka karya Mimi sai faman salo-salo take taki sakin jikinta, nace." Wai ke Mimi meye haka ne."? Kallona tayi tare da fadin "me nayi kuma"? Tsaki naja nace " ban sani ba." Dan murmushi tayi tace." Kin fada masa kuwa"? Cikin mamaki nake kallonta domin nagane inda ta dosa. Nace." Mimi ina ta kaina yaushe na samu damar fada masa kina sonsa don Allah ki cire shi daga zuciyar ki, mu shafe babinsa a RAYUWAR mu." Munnu tace." Yau ranar mai da martani yazo. Kuna min dariya akan Shamsu kema gashinan so ya sark'e miki wuya hahahahaha" ta k'arasa maganarta tana kyalkyala dariya.

Mimi idonta yayi rau-rau kamar zatayi kuka na kalleta cike da mamaki girgiza kaina nayi nace." Wallahi duk isa da k'asaitar namiji bai isa in masa kuka ba akan ina son shi kome ye sai dai ya

gani a aikace,lallai Mimi a inda ba asan ma kina yi ba kike shirin yin kuk.........kafin in k'arasa sai ga hawaye shar-shar yana kwaranya a fuskar Mimi.Ni da Munnu muka zuba mata kallo cike da mamaki!
Ita ko Mimi tun lokacin da taji Asma'u na bawa Munnu labarin abunda guy nan yayi mata taji wani irin kishi na cin zuciyarta wani k'aton Abu yazo ya tokare mata a mak'ogwaro sosai take jin kishin Asma'u saboda shirme irin nata ma cikin zuciyarta tana fad'in "dama ita yayiwa abunda yayi wa Asma'u n." Cikin fusata! Na dinga balbalawa Mimi masifa nace." Mimi ko kukan jini zakiyi bazan fad'a masa ba dama ni nace zan fada masa to yanzu na fasa fada masa idan kin damu kije da kanki ki fada masa aikin banza aikin wofi, yanzu akan shi kike kuka ? Mimi kinyi asara Wallahi. " Munnu tace." Kinga Asma'u ki k'yaleta mana saboda ke baki san masifar so ba shiyasa kike fad'in haka ni da ita duk mun San meye so saboda haka ki k'yaleta taji da abu guda." Mik'ewa nayi nace." Sai kuje Ku k'arata ke da ita kune wahallalu." Futa nayi na barsu. ruwan Wanka na hada na shiga nayi a gurguje na futo, sunanan inda na barsu suna maganganu k'asa-k'asa nace." Ke Munnu zo ki d'auko min kaya ga rigar nan na cire." Da sauri ta mik'e ta bude akwatin kayanta tare da fad'in" gashinan zab'i Wanda yayi miki." Ina mutukar son atampah a rayuwata nan na hango atampar Munnu da take masifar so. Wata supar ita na nuna, sai na ko a jikinta ta Ciro ta bani, na karb'a ina duba dinki nace "Allah yasa ta shige ni" domin dai munnu bata da wani kib'a duk cikinmu na fisu cika da kwarjini, da k'yar na zura rigar dake zani ne mara ado  sai na daura kawai na zauna ina shafa mai a nutse nace."Mimi ki tashi kiyi Wanka mu tafi ko inyi tafiya ta ne."? Banza tayi min.nima sai na share ta na cigaba da kwalliya ta. Minti biyar tsakani ta mike ta futa na bita da kallo cike da tausayi wai *Amjadu* zata ce tana so har da kuka tabd'ijam Mimi ta had'u da jaraba.

A gurguje ta futo daga Wanka ta kimtsa jikinta muka futo domin tafiya nan Ummansu Munnu ta kara bamu kudi bayan Dari biyar din jiya Nace baza mu karb'a Dole ta samu sai da muka karb'a mukayi mata sallama, Har bakin titi Munnu ta rako mu sai da ta tabbatar mun shiga a dai-dai ta sahu sannan ta koma gida.

Tafiyar kurame mukayi ni da Mimi tana jin haushina INA jin haushin ta haka muka je gida wannan karon Umma bata d'aga hankalinta ba, saboda sunyi waya da Ummansu Munnu ta fada mata inda muka kwana, shiyasa bata tuhume mu ba.

******

Shiko Amjadu yana komawa gida ya kulle kanshi a daki bacci ne fal a idon shi jallabiyar jikinsa kawai ya cire ya haye bed da ko shimfid'a babu dalili bedshirt din da Asma'u tayi shagalin ta dashi yana ya she gefe guda, pillow ya jawo  idanunsa sukayi masa tozali da pant din Yarinyar, a jirkice ya d'auka sa a hannunsa yana dubawa, murmushi ya saki iya leb'ansa yace." Wato yarinyar nan babu wando a jikinta kenan, amsar hakan na gurin shi tunda ga pant din nan a hannunshi  minti biyu yayi yana kallon pant din zuciyarsa na masa sak'e-sak'e a kanta, cilla shi yayi kan bedshirt din dake yashe a k'asa yana tunanin bawa me wankin sa zai yi tunanin ina ya samu pant din mata dole dai shi ta ya kama ya wanke mata,, lumshe idonsa yayi had'e da Dora hannunshi saman goshin sa, yana sakin murmushi shi kad'ai, yaji dad'i sosai da ta manta pant

dinta yasan zata dawo d'auka kamar yanda ta dawo d'aukar jakarta. Da tunanin abunda ya faru tsakanin sa da ita bacci ya d'auke shi.

******

Haka muka yini ni da Mimi kowa yana sabgar gaban shi har Umma taso ta fuskanci wani Abu da na lura da haka sai na fara shigewa Mimi ina bata labari duk Dan kar Umma ta gane abunda yake faruwa. Dare nayi kowa ya nemi gurin kwanciyarsa ni da ita babu um babu umum babu hira tsakani na  da ita kamar yanda muka saba kafin muyi bacci. Ina kallon sanda bacci ya d'auke ta. Ni ko idona tarr!!! Ina ta tunanin jiya iyanzu ina gidan guy nan muna artabu dashi, kafin in an kara na fara jin mood dina na sauyawa nipple d'ina naji ya fara min k'aik'yayi kamar yanda ya saba, naji yana wani kumborowa, tuni na fara addu'a a zuci da fili Allah yasa kar abun ya tsananta nasan ba karamar wahala zan sha ba kafin Safiya.

Tsigar jikina ta dinga mik'e da na tuno kammanin sa da suffarsa sai gabana ya fad'i sosai  naji k'asana ya fara zubar da ruwa  na dinga mutsu-mutsu ni kadai kan katifa ina jin kamar ya tsansa ne a gurin yake mun wasa dashi yanda ya dinga mun jiya, a hankali na saki nishi tare da rintse idona na ciji leb'ena na k'asa sosai, nace" Allah kaga halin Dana ke ciki. Ka kawo min dauki." Ni kadai na dinga surutu k'asa-k'asa ina  wani irin nishi! Da tuno lokacin da yake tsotsar gurin sai inji wani ruwa ya zo bi min kamar jiya, ni da kaina nasan idona ya kankance saboda yanda nake kasa bude su sai da dubara, babu abunda nake bukata a time din illah inji shi a jikina yana irin abunda yayi min jiya, nishi! Nayi a hankali nayi ruf da ciki na rungume pillow ina addu'a a cikin zuciyata ta samun sauk'i da rangwame.

Zuciyata na sak'a mun kawai in tashi in tafi gidan shi saboda na rasa yanda zanyi tun ina addu'ar a zuciya ta fara futowa fili dake Mimi me nauyin bacci ne ko motsin kirki ta kasa haka nayi ta juyi ni kadai kan katifa ta hawaye na zubo min na rasa wane irin taimako zanyi wa kaina, sai daf da asubah bacci b'arawo ya kwashe ni, Mimi tayi min tashin duniya na kasa tashi haka ta futa taje ta dauro alwalar sallahr asubahi

Sai misalin bakwai da rabi na tashi shima Ya Aminu ne ya shigo har dakin namu yana tashi ne da masifa tare da fad'in "na kwanta bacci na manta yau zamu je dubo jarrabawar mu, na mike zaune ina mutsika idona, kallona yayi cikin tuhuma yace." Ciwon ido kike yi naga idon ki yayi jazur." Mimi tace." Nima abunda zan tambaya kenan. " Mik'ewa nayi a daddafe saboda yanda nake jin marata nayi min wani irin suka . kwata kwata nakasa had'a ido dasu simi-simi na futa daga dakin, INA addu'ar Allah yasa Ummamu bata tsakar gida, aikuwa Allah ya amshi addu'a ta na cikin d'akinta nayi saurin shigewa ban d'aki.

*25/October/2019*
[11/1, 10:55 PM] .: *BABBAN YARO*

*Mallakar_BINTA UMAR*

*LITTAFIN MALLAKI NA NE KUN BIYA KUD'IN KARATU NE KAWAI DUK WACCE TASAN ZATA FUTA DASHI WAJE DON GIRMAN ALLAH TAYI MIN MAGANA NA DAWO MATA DA KUDIN TA*

*28*

Raina a b'ace na futo daga band'akin, na shiga dakinmu Mimi ta bini da kallo d'auke kaina nayi na fara birkito da kayan sawa ta, tace." kizo mu fara karya sannan ki saka kayan." A fusace! Nace.' Dole sai da ni sannan zaki karya to ki daskare anan." Tab'e baki tayi ta juya kawai ta fara kurb'ar kununta tana had'awa da soyayyar Dan kalin Hausa, a hankali naji tace." Da sanyi Safiya zaki fara rashin mutumci." Shuru nayi mata kawai ina jin zafi a zuciyata Wanda na rasa ko bakin cikin me ye yake damuna oho. Ina gama shiryawa na mik'e tare da kallonta nace." Idan baki yi sauri ba wallahi tafiya zanyi." Mimi ta hasalo itama tace." To kiyi tafiyar ki mana Asma'u ai na San hanya,kawai sai ki dinga min tsawa kamar uwata wallahi baki isabah!!!"" Tsaki naja na futa daga d'akin fuuuuu!! Umma na zaune a rumfa tana lissafa kud'in cinikinta na shiga da sallama, kallona take cikin nazari sai nayi saurin gyara yanayin fuska ta na zauna kusa da ita ina gaisheta.Ta amsa babu yabo babu fallasa tace." Me ya hanaki tashi da wuri  yau abunda ba sabon ki bane." Kasa nayi da kaina ina shiryo k'aryar da zanyi mata. Tace." Tambayar ki nake." Da sauri nace." Umma kin San dama bana sake wa a gidan mutane inyi bacci Wallahi jiya kwata-kwata banyi bacci a gudansu Munnu ba shine dalilin da yasa na makara." Tace." Yayi kyau hakan." Yanda ta fad'i maganar yasa na soma zargin kaina sunkuyar da kaina nayi  ina addu'ar Allah yasa kar ta fahimci wani Abu. Kamar daga sama naji tace." Nishi! Da surutun me naji kinayi jiya da daddare." ? Gaban yayi bala'in fad'uwa." Jarumta na aro da dauri na d'ago kaina ina kallonta nace." Umma nishi! Kuma."? Hararata tayi ta cigaba da lissafin ta, tace." Ko

k'arya nake."? Girgiza kai na nayi nace." A'a."!  Murmushi tayi kawai tana girgiza kai tace."Asma'u nice na haife ki babu abunda zaki layance min, dukanin Ku a tafin hannuna kuke na dad'e da sanin halin da kike ciki saboda haka nake baki shawarar ki tsare kanki da martabar ki ta d'iya mace ki kula kada sha'awa tasa ki jefa kanki cikin halaka kad'a shaid'an ya ribace ki ki aikata sab'on Allah ko kice zaki nemi hanyar biya wa kanki buk'ata ta ko wace siga ki tsare kanki daga nan har lokacin da Allah zai futo miki da mijin aure." Umma ta k'arashe maganar ta babu abunda ya dame ta.
Wata irin kunya ce ta lullub'e ni dama nasan Umma sai ta fahimta nasan ta da mugun saka ido akanmu sunkuyar da kaina kawai nayi domin bani da tacewa. Haka Mimi ta shigo ta same mu ,da sauri na mike na futa ko sallama banyi wa Umma ba, Mimi CE ta tsaya ta karb'ar mana kud'in abun hawa.

Ban jira Mimi ba nayi tafiya ta har na Isa bakin titi bata k'araso ba, tsaki naja kawai ina kallon hanya can na hango ta ta tawo na d'auke kaina cike da haushin ta, me a dai-dai ta na tsayar mana,  muka shiga tare da fad'a masa inda zamu . haka mukayi tafiyar kowa zuciyarsa babu dad'i.

Tun daga bakin get din makarantar mu muka soma cin karo da k'awayenmu da ihu!! Suka zo suna rungume ni tare da taya mu murna ni da Mimi mun ci jarrabawa nima sai na saki fuska sosai na kutsa cikin jama'a domin idona ya gane min,  duk mun cinye maths ne kawai muka fad'i  shima ba sosai ba, wasu na murna wasu na bakin ciki nima tsabar murna tasa na manta da komai na shiga cikin k'awayenmu muka fara ihu! Da dariya wadan da suka fad'i ciki ko har da Alina tana tsaye jikin motar ta kamar ta kurma Ihu! Munnu na kalla cikin dariya na nuna mata Alina ina fad'in" Munnu dubi Alina da fuska sai kace soyayyan k'osai sai maiko take cikin rana." Munnu ta shek'e da dariya tana fadin" shegiyar ba fuska taci bleecing ciki ko oho dama yaushe zata ci jarrabawa tana can tana yawon iskan ci." Dariya muka shek'e da ita. Mimi tace." Ku Wallahi kun fiye Neman fitina kuzo mu tafi tunda dai mun gama abunda ya kawo mu" hararta nayi nace." Wallahi baza mu tafi yanzu ba sai nagama kallon 'yan bakin ciki da masu kuka irin su Ooo" na nuna Alina da bakina . a fusace! Ta tawo inda muke tsaye ta nuni da ya tsa tare da fad'in" ke Ki shiga hankalin ki wallahi ko in sauke fushina a kanki yanzu". Kallon banza na watsa mata nace ."da gaske kike." ? Tace." Zan sanya ne ayi min k'asa-k'asa dake shigeya 'yar gidan malam Shehu sai tsabar girman kan tsaya." Wawan mari na Kai mata ta dafe kuncin ta cike da tsoro! Ina numfar fashi nace." Wato har kin manta dabi na dake ko? Shine kike ikirarin sawa a dake,to don durun Uwar ki ki saka ayi gunduwa-gunduwa dani shine kad'ai zai nuna min ke 'yar gidan Bulget ce ubanki ba Santana ba ne."

Ca kumo wuyana tayi ta hau d'ura min ashar!! Idonta yayi jazur!! Kafin ta Ankara na daki bakinta da gwiwar hannuna nace." Dama Neman ki nake ruwa a jallo shegiya karuwa." Ai kafin kace kwabo gurin ya soma cika da mutane Alina ta fad'i a gurin tana wani k'ifkifta ido bakinta na kumfa,dama ta saba daga zarar an fara fada da ita zata fad'i kasa tana burgima wai ita me aljanu.

Mimi da Munnu hankalin su ya tashi suka nufi offece din principal da sauri sauran 'yan

makaranta suka fara guduwa domin sun tsorata da abunda Alina take ni ko ina tsaye a kanta ko d'ar ba nayi.  Malama Rakiya ce da aunt Lahira suka k'araso gurin hankali a tashe suka fara yi mata tofi, mintuna kusan ashirin sannan ta dawo dai-dai duk suka tattaramu suka tasa mu gaba zuwa offece din principal me gaba d'aya.
 Fad'a sosai shugaban makaranta yayi mana tare da gargadin cewa idan mun San rigima za mu zo muyi ta zai soke mana  shagalin murnar da mu tana da ranar candy sai kawai kowa yazo ya karb'i takkadun sa, ya tafi, hakuri muka bashi sosai sannan ya sallame mu muka futa daga ofis din gruop-gruop an tsaya sai gulma ake haka Alina ta futo jiki babu k'wari ta shiga motar ta ta tafi, mu kuwa sai bayan sallahr azuhur sannan mukayi sallama da k'awayenmu bayan mun tsaida ranar da zamu gudanar da murnar kammala makaranmu sati guda me zuwa, tare da futar da anko har kala uku duk ranar zamu sanya shi. Muka futo titi muna Neman abun hawa rana ta kwalle sosai gumi kawai nake ga wata irin yunwa na damuna dama ban karya ba gwara Mimi ta karya da k'yar muka samu a dai-dai sahu muka shiga, ya dauki hanya sai gida. Hira muke sosai cikin adai-dai tar kowa na fadin albarcin bakinsa, danja ta tsai damu, cike da jin haushi nace." Na tsani ina cikin abun hawa danja ta tsaidani wallah.........maganar tawa ta katse hango gefan fuskar sa da nayi kwance a cikin wata mutsiyaciyar mota silver sai shak'i take a can tsallakenmu, da sauri na d'auke kaina gabana na dukan uku-uku addu'a nake kar Allah yasa Mimi ko Munnu wata ta hango shi, a sace na k'ara kallon gefan haguna sai naga ya mak'ala airpix a kunne shi tare da gyara zaman shi ya d'ora pcap me wani irin ado a jikinta  gani nayi yayi min wani bala'in kyau ban gane ko wane dressing ne a jikinshi ba, amma na tabbata k'ananun kaya ne tunda INA hango hannunshi yana latsa wayar sa, ga Rambow a gefan shi sai zare ido yake.

D'auke kaina nayi jin miyan bakina ya daskare ban tab'a tsayuwa na kare masa kallo ba sai yau, a zuciyata Nace "Ashe haka yake da bal'in kyau!!!!!

*25/October/2019*
[11/1, 10:55 PM] .: *BABBAN YARO*

*Mallakar_BINTA UMAR*

*LITTAFIN MALLAKI NA NE KUN BIYA KUD'IN KARATU NE KAWAI DUK WACCE TASAN ZATA FUTA DASHI WAJE DON GIRMAN ALLAH TAYI MIN MAGANA NA DAWO MATA DA KUDIN TA.*

*29*

Ban sake kallon gefan da yake ba har aka bamu hannu, muka wuce Munnu ta kalle ni tare da fad'in"wai ya kikayi shiru sarkin kaud'i." Ya mutse fuska ta tanayi nace." Yunwa nake ji Wallahi." Tace." Ba Dole ba wannan uban ihu da kika sha, shiru kawai nayi mata zuciyata nacan ga tunanin guy nan, cikin zuciyata nace sai kyau amma babu kyawun hali. Munnu aka fara saukewa ta kalli ni tare da fad'i wa kika ce zamu bawa dinkimu "? Nace." Kinsan dai ba zamu bawa Ummi ba ta lalata mana yadi maza zamu bawa dinkimu." Tace." Shikkenan yaushe zamu gidan aunty Hauwa ko kuma da kanmu zamu shiga kwari." Nace." Ki rabu da aunty Hauwa kawai muje da kanmu."tace." To shikkenan sai goben" muka ce "Allah ya kaimu ni da Mimi .me a dai-dai ya ja mu muka tafi ita kuma Munnu ta tsallaka titi ta shige layinsh.

A hankali motar ta silala ta shiga cikin harabar gidan. Rambow ya futo da sauri ya bud'e masa kofar motar tare da k'okarin karb'ar wayoyin hannunsa.
Girgiza masa kai kurrum yayi ya wuce shi cikin sassarafa, suka rufa masa baya.

Dattijiwa kamillaliya na zaune cikin kujera tana sanye da atampah Ghana kamar ko da yaushe sai kamshi parlor yake tana zaune tana kallon tv tashar sunnah tv suna wa'azi, gefan ta wata matashiyar budurwa ce a zaune tana kallo ita.

Ya shiga da Sallama a bakinsa. Da sauri Hafsa ta kalli kofar shigowa jin muryarsa taji wani sanyi na kwarara a cikin zuciyarta. Cike da kunya ta d'auke kanta.

Granny tace." Dan halak kaki jinin ambato dama yanzu nake fada miki zai shigo tunda yau juma'a."

Hafsa ta yi k'asa da kanta tana murmushi . cikin yanayin tafiyar sa ya k'araso kusa da kakar tasa ya zauna gefan ta, tare da gaishe ta. Ta amsa cike da walwala da farin ciki tace." Ga k'anwar ka nan tana zaman jiran kazo Ku gaisa." Cikin rashin fahimta yake kallon Hafsa dake sine kai yace." Granny wacece wannan."? Cike da takaici tace." Hafsa zaka ce baka sani ba kai kuwa." Sosa kansa yayi tare da fad'in" banda abunki to a ina zan santa na dai ga tana kama da Innah Suwaiba." Granny tace." To 'yar autar ta ce ai." Sosa kansa yayi a karo na biyu yace." Ayya! Ai kin San ni ba sanin 'yayan ta nayi ba sosai wallahi in banda Musbahu da Zaraddini suka kadai zan sheda a cikinsu."

Granny tace." Ai dole kai da ba ziyara kake ba dole ka kasa saninta , sunanta Hafsatu." Fuskarsa babu yabo babu fallasa ya kalli Hafsa a nutse yace." Hafsa ya gida ya makaranta." Ba kinta na rawa tace." Lafiya Lou alhamdullahi. " yace." Ina Ina Suwaibah tana lafiya."? "Lafiyan ta lau tace ma a gaishe ka tunda ka daina zuwa." Murmushi yayi kawai be komai ba." Granny tace. "Ai ka saba dama da anyi magana ka sosa kai ya kamata dai cikin wannan satin kaje." Yace." Insha Allah zanje ayyuka ne suka min yawa ke kanki kin sani." Tace" na sani amma ai ana barin halak da kunya." Shiru kawai yayi mata tana surutai wayarsa yake dannawa yayin da Hafsa take ta satar kallonsa tana ji kamar ta had'iye shi ta huta.

Ina Suawaiba mahaifiyar Hafsa yayar Aisha ce wato mahaifiyar Amjadu itace babba a d'akinsa Hafsa kenan a matsayin kanwarsa take.

Kallon da take masa ne ya dame shi kwata-kwata a rayuwarsa ya tsani kallo shi kam, b'ata fuska yayi ya mik'e tsaye tare da kallon agogon hannunsa, ya kalli Granny tare da fad'in ni zan tafi." Cike da mamaki tace" zaka tafi kamar yaya? Baza ka tsaya ka ci mutumin naka ba gashi na kwad'anta maka." Tana nufin zogale. Girgiza kansa yayi kawai ya nufi hanyar futa, kallo tabi shi dashi cike da takaici tace." Ka tsaya ka ragewa Kanwar ta hanya mana." Ba tare da ya wai wayo ba yace." Ki bata kud'in abun hawa mana." Yayo fucewarsa ya gane manufar granny na aje yarinyar da tayi Dama wancan satin da yazo ta fada masa tayi masa budurwa lallai granny tana da aiki a gabanta.

Hafsa kuwa ji tayi kamar ta tashi ta dawo dashi domin Sam bata gaji da kallonsa ba, ita dai Allah ya sanya mata k'aunarsa a ranta tana fatan Allah ya sa granny tace dole ya aure ta tunda ta lura Sam bata gabansa amma tayi mamaki sosai yanda ya amsa mata gaisuwarta a sake ta d'auka yana da girman Kai ashe ba haka yake ba.

Yana futa wayar shi ta fara k'ara dubawa yayi cike da mamaki numbar me girma governor ya gani, sai da ta kusa katse wa sannan ya daga wayar da muryarsa irin ta jarumai, suka gaisa da shi cikin nutsuwa daga d'ayan b'angaran me girima governor yace." Kazo Gidan gwamnati musalin k'arfe biyar na yamma ina Neman ka." Yace." Insha Allah inan tafe." Sallama sukayi gaba dayansu kowa ya kashe wayarsa. Murmushin gefan baki yayi kawai yasan karshen zancan wato shime governor yana goyawa su Me citta baya kenan , lallai dole ya tashi tsaye akan haka.

*******

Tunda nayi masa wannan ganin shikkenan na nemi kuzari na na rasa haka muka shiga gida jikina babu k'wari Mimi CE kawai take ta murna tana baya Umma labari, itama sai murna take tace." Nasan kun kwaso yunwa to ga abunci can cikin Fula's a kicin yau har nama na siya muku na sanya muku a miya." Mimi ta tashi da sauri taje ta d'auko mana, tare da d'ebo mana ruwa me sanyi na cikin randa, cin abuncin kawai nakeyi kwata-kwata bana jin tes d'insa a bakina, ganin Umma tana kallona a fakaice yasa na fara yak'e INA biyewa Mimi muna ta labari. Mimi tace." Umma kinga ankon da muka futar za muyi." Umma ta karb'a tana dubawa tace." Aikuwa dai atampar tayi kyau kuma daga ni me tsada CE." Nace." Umma ai material din yafi ta tsada shi dubu goma sha biyu ne fa." Umma ta b'ude bakinta cike da mamaki tace." Da ubanku ina zan samu kud'in siya muki har dubu ashirin da hudu bayan kud'in dinki." Nayi karaf nace." Umma gaba daya Dana lissafa kud'in sun kai dubu arba'in da bakwai da atampar da material din da shaddar." Umma ta gyad'a kawai tare da fadin " kun shirya ruguza ni kenan yo ni ina naga dubu arba'in har da bakwai a Hamsin kad'an ne babu, so kuke in rusa jarina inyi muku anko kunga daga baya sai mu koma mu tsuguna muna tsotsar tsamiya." Jin abunda Umma tace yasa gabana fad'uwa dan gaskiya bana kaunar harkar k'aranta a rayuwa ta bana so ace ba muyi ko wane anko ba, in San samu ne ma da sabbin takalimi da jaka da mayafi." B'ata fuska nayi ina cin abuncin kamar bana so. Ta kalle ni a nutse tace. " naga kin b'ata fuska don ubanki so kike in siya muku anko ni kuma Ku karya ni ko, to bazan siya duka ba, Ku zab'i daya a cikin guda ukun, dama si kullum abunda ake fada muku kenan Sana'a tana da dad'i da kuna Sanar Ku da duk babu abunda zai gagareku, ko kuyi bakwa yi da aunty Ku tasan duk hanyar da zata bi ta nemi kudi saboda haka ni babu ruwana." Shiru mukayi duk murnar mu ta koma ciki. Wasu hawaye ne suka fara zubo min na takaici! Mimi ma ina kallo idonta duk ya ciki mda k'walla Umma tace "kuyi kukan jina ma ni babu ruwana." Yaya Aminu ne ya shigo dakin da sallama a bakinsa Umma ta amsa masa ya zauna yana kallonmu cike da mamaki hankalin shi yafi karkata kan Mimi yace." Meye suke kuka." Nan Umma ta warware masa abunda yake faruwa.

Dariya yasa tare da nuna Mimi da hannu yace." Sam kuka baya yi miki kyau gwara ma ki daina."Mimi ta zumb'ura bakinta yace." Nawa ne kud'in atampar."? Da sauri nace" dubu hudu ce ." yace." To zan bada shikkenan ko." Sakin fuska mukayi dukaninmu nace "to shaddar fa."? Hararata yayi yace." Wannan kuma sai Ku nemi Wanda zai siya muku." Mimi tace." Asma'u ina ganin in muka samu guda biyu ma ai mungode Allah." Shiru nayi mata domin ba haka naso ba." Umma tace "sai Ku nemi kud'in dinki don wallahi kuka d'auko dinki me tsada me cin kayan dinki to bazan biya ba." Nace. " Umma kinsan shi material din fa dole sai anyi masa bauta an siyi shafi da sauransu gaskiya zai ci kudi sosai, bayan haka kuma don Allah ki siya mana sabbin takalma". Hararata tayi kawai ta juya suna magana da Ya Aminu.

******

Biyar dai_dai yana gidan gomnati nan aka yi masa ido har ofis dine me girma governor ya zauna kan wata lumtsime miyar kujera suka gaisa a tsana ke, me girma governor ya kallashi sai

ya ji gabansa na fad'uwa ganin yanda Yaro yayi masa mugun kwarjini, yace." Bisimillah ga ruwa kasha." Amjad yayi murmushi tare da fadin." Nagode me girma shugaba." Bayan yasha ruwan ne me girma governor ya kalle shi a nutse yace." Hausawa suka ce maganar gizo bata wuce ta k'ok'i na San ka fahimci dalilin da yasa na kira ka."? Yace." Ban fahimci komai ba ina Neman Karin bayani." Governor ya gyara zama tare da fadin." Har yanzu muna kan bakanmu na ka rushe company naka ko kuma ka tsawwala farashin kayanka, saboda ni kaina na zauna nayi nazari da tunani ba 'yan kasuwa kad'ai abun yake tab'awa ba har da gomnati ina fatan ka fahimta, gomnati na karb'ar haraji a hannun 'yan kasuwa idan ba k'ara farashin kayan ka ba to tabbas zamu tsawwala wa 'yan kasuwa kud'in haraji kuma za mu rushe shagunanmu Wanda gomnati ta gina zamu kori duk wani dan tebur da Wanda bashi da shago zamu watsa su daga kan titi, wannan shine matakin da muka d'auka.

Ido jazur! Ya d'ago kansa yana kallon governor din yace."Allah shi baka nasara da kanka kake wannan ikirarin? Wato har kamanta ranar rantsuwa kenan ? Ka manta ranar da ka dafa alk'urani me girma ka rantse dashi? Ka manta ranar zab'e da wahalar da talakawa suka sha akanka rana zafi sanyi ruwa talaka ya tsaya kai dafata ya dangwala maka kuri'a duk ka manta wannan ranar me girma Governor. " ya k'arasa maganar tasa cike da tuhuma."

Me girma governor yaji duk jikinsa yayi sanyi jin yaron yana so yayi masa warwara nan take ya fara nad'e tabarmar kunya ta hanyar buga tebur din dake gabansa yace." Duk wannan abunda kake fada basu shafeka ba, lokacin zab'e na futo da kudi Wanda ni kaina bansan iya adadinsu ba, an rabawa talaka INA so ka sani talaka a yanzu ya fi bukatar ka bashi Dari biyar ko ka bashi sabulun Wanka sink'i d'aya akan 'yan cinsa, saboda haka rik'e alkawari da sauransu duk bai shafe ka ni dai ga hukuncin da na yanke! Idan kuma kak'i karb'a kai kanka sai mun rusa ka da duk abunda kake tak'ama dashi."

Murmushi me ciwo yayi ido jazur yake kallon governor din yace." Ita kuma rantsuwar da kayi fa? Allah ba abun wasa bane."
Governor ya daga masa hannu a fusace! Yace." Kai kasan Allah ne ? Dubi askin dake kanka, duk abunda kake muna da labarin sa ka bude hotal har guda biyu ana tata iskanci a ciki kai kanka kana iskancin ka da mata zaka zo kana fada min Allah anan gurin." Murmushi Amjad yayi cike da takaici wai shi governor zaiyi wa gurin yana Neman mata, mutumin da kowa yasan shi mugun asharari ne me mugun son mata da shaye-shaye shiyasa lokacin zab'e 'yan daba ya baza ko ina suna raba kudi tare da tsorata alumma da jajayen idonsu mik'ewa yayi a fusace! Ya kalle shi yace." Ina nan kan bakana babu gudu babu ja da baya company kuma yana zaune daram! Sannan kuma bazan kara farashin kaya na ba." Yana gama maganar sa ya futa daga ofis din cikin zafi.!

Governor ya bishi da kallo da baki a sake, waya ya d'auka ya kira shugaban kasuwar k'wari yace." Yanzu-yanzu a rufe a shaguna kuma a watsa 'yan tebur da suke kan hanya.

Aikuwa haka ce ta kasance 'yan kasuwa na hidima da kaswancin su tare da customs kawai

sak'on shugaban kasuwa ya riske su, da ya yawun me girma governor, hankali a tashe suka fara rufe shaguna kowa na fad'in." Albarka cin bakinsa.
Tun kafin ya isa gida labari ya riske shi, ranshi a b'ace ya dauki wayarsa ya kira governor din shi kuma a nashi b'angaran ya dauki wayar da sauri yana wani mugun murmushi ya d'auka Amjad din ya sauko daga kan kudirinsa yasan dai yanzu labari ya same shi, muryar shi sama-sama yace." Ina kan hanya ta ta komawa gida na samu labarin abunda ya faru yanzu, ina so in fada maka wani abu, daga nan ba zan zame ko INA ba sai gidan redio zanje in warware musu zare da abawa." Saura kad'an governor yayi hantsile daga kan kujerar da yake zaune baki narawa yace." Kar ka kashe min waya ka bari kaji abunda zan ce da kai." Murmushin takaici yayi yace." A banza abunda baka sani ba shine duk wata shira da ta gabata a tsakanina da kai ina d'auke da ita cikin wayata so a tafin hannuna kake." governor ya goge wani zazzafan gumi da yake tsatstsafo masa a goshi lallai yaron nan bashi da mutumci wato ya samu zagin da jama'ar gari suke masa kwana biyu ya lafa shine zai dawo dashi, baki na rawa yace." Kar........Amjadu ya katse ta hanyar fadin " baka da abunda zaka ce min a halin yanzu kawai ka janye kudirin ka nima in janye nawa." Governor yace." Na janye gobe kowa ya futa kasuwa kai kuma ka saurari abunda zai biyo baya." Murmushi kawai yayi ya kashe wayar ba tare da yace uffan ba."
.governor ya tsaya kawai yana kallon fuskar wayarsa yana mamakin yaya akayi yaron ya samu dama akanshi har ya raina shi, da matsayinsa yana matsayin shugaba amma yake kashe masa waya lallai ya zama dole ya hukunta shi.

Rai a bace ya shiga gida ana ta kiran sallahar magariba alwala ya d'aura nan cikin bedroom d'insa yayi sallah, waya ya kira Rambow ya je ya siyo masa abunci domin wata yunwa yake ji,ga uban hayak'in sigari da ya babbakawa cikinshi a mota sai da ya shanye a kwali guda kafin su shigo gida.

Mintuna ashirin tsakani Rambow ya shigo dakin hannunsa rik'e da wata Leda me kyau da k'yalli ya aje masa tare da jira ko akwai wani umarni daga masa hannu kurum yayi alamun ya futa, cike da bin umarni ya futa daga dakin. Ledar take away din ya jawo yana dubawa abuncin be masa ba ya rufe jingina yayi jikin gadon shi yana tunanin yanda za'ayi ya warware wannan Matsalar da take tun karo shi.

*******
11:00 dai-dai abun ya afku gidajan redio na shirin rufewa suka samu labari babu shiri suka tafi domin d'auko rahoto, yana zaune inda yake tun d'azu ya fara jin kira na shigowa wayoyin shi, daukowa yayi yana dubawa Wani d'an kasuwa ne da ya shara ya kira shi suka gaisa hankali a tashe yace." Yallab'ai Ashe abunda ya faru kenan kai Ubangiji Allah ya tsare ya kiyaye gaba gaskiya muna cikin tashin hankali." Amjad ya kasa fahimtar maganar sa kawai ya aje wayar ya dauki dayar zance dai guda ake masa, Zumbur ya mike ya futo parlor yana shirin bude kofa ya futa sai suka buga karo da rambow zai shigo hankali a tashe, abunda ya d'auke masa hankali abunda yaji wani Dan jarida na fada a wayar Rambow inda yake cewa" *Inna lillahi wa ina ilahi raji'un, a yanzu ne muka samu labarin mummunar gobarar da ta afku a katafaran company nan

na Amjadu ABUL Abbas company da ya shahara gurin kawo kaya masu kyau da karko gami da sauk'i da saukakawa talaka......."*

*26/October/2019*
[11/1, 10:55 PM] .: [10/26, 11:33 PM *BABBAN YARO*

*Mallakar_BINTA UMAR*

*LITTAFIN MALLAKI NA NE KUN BIYA KUD'IN KARATU NE KAWAI DUK WACCE TASAN ZATA FUTA DASHI WAJE DON GIRMAN ALLAH TAYI MIN MAGANA NA DAWO MATA DA KUDIN TA.*

*30*

*Innalillahi wa'inna ilahi raji'un."* shine abunda ya futo daga bakin *Amjadu* da sauri ya koma

bedroom din nasa jikinsa na kyarma! Ya dauki wayarsa yana laluben numbar manager, har wayar ta katse bai d'aga ba, ya kara kira a karo na biyu shiru bai d'auka ba. Parlor ya futo yana kara kiran wayar.wannan karon tana shiga manager ya d'auka babu abunda ya futo daga bakin Amjadu sai "Bashir ina fatan babu Wanda ya rasa ransa ko."? Manager yace." Eh yallabai babu Wanda ya rasa ransa sai dai akwai wad'anda suka samu rauni gurin ceton ransu." Yace." Maza ka had'a Kansu Ku wuce hospital me zaman kansa ganin zuwa." Manegar yace." Insha Allahu haka za'ayi." Kashe wayar yayi ya dauki dayar da take aje kan bed an kira yafi sau goma, Sam bai tsaya daga wa ba domin yasan duk zance daya ne. Futowa yayi rambow da doh-doh suka rufa masa baya.

Kai tsaye company suka nufa cike da tashin hankali da tarrarabi, kafofin yad'a labarai sun rud'e da zancan ko wacce ka kamo maganar gobarar ake wanda suke fad'in an rasa meye musabbabin ta. Kafin kace kwabo labari ya watsu a birnin kano da kewayen ta, cikin daran 'yan kasuwa suka dinga futowa daga gidajansu suna jajantawa junansu kungiya wasu sukayi suka nufi company cike da alhini da tashin hankali.

Ido jazur!! Yake bin company ninsa da kallo ya k'one kurmus! Ko ina ka d'aga kai sai hayak'i yana tashi gurin ya hautsine da 'yan kwana-kwana gami da mutanan gari kowa na bada gudumar sa." 'Yan jarida sun kewaye shi sun fi su goma dukaninsu suna son suji ta bakinsa. Duk inda yayi sai sun bishi suna fadin." Young millionaire *Amjadu* "Ko zaka fad'a mana wane irin hali kake ciki na wannan Abu da ya faru da company min ka me tarin albarka muna bukatar jin ta bakin ka." Shiru yayi musu kawai hannusa goye a bayansa yana zaga loko da sako na ko ina hannunsa ya mik'a ya karb'i wayarsa gurin rambow, nan ma 'yan jarida suka yi masa caaaa!!! Masu d'aukar sa hoto nayi masu vedio nayi masu kafa masa lasifika a dai-dai bakin sa nayi, wai Dole sai sunji me zai ce a wayar.
Numbar Manager ya kira bugu d'aya ya d'auka tare da fad'in." Ranka ya dad'e." Cikin jarumta da dakiyar zuciya yace." Yaya ina fatan babu wata matsala duk Wanda yake bukatar taimakon gaggawa ayi mishi kan lokaci. " manager yace." Insha Allah ranka ya dad'e gashinan ma ana musu dressing raunin ka da suka samu." "Kuna wane hospital ne."? Manager yace." Malam. Aminu kano." Ok ganin zuwa." Ya fad'a yana kashe wayar." Yuuuuuuuu!!! Suka bi bayansa tare da sake maimaita masa maganar d'azu. Doh-doh ya juya da sauri yana zare musu ido!! Oho ko a jikinsu, hummm! D'an jarida da nacin tsiya. Wani ne yayi tsagal!! Ta tari gabansa ya kafa masa lasifik'a a baki Tare da fadin." Ranka ya Dade ka taima kayi mana magana muna mutukar bukatar muji ta bakin ka akan wannan al'amari da ya afku."!!
Murmushi yayi Wanda kana ganinsa kasan na bakin ciki ne, yace." Kuna so ku ji ta bakina."? Duka suka ce k'warai kuwa ranka ya dad'e. Cikin basarwa yace." Komai dai ya samu bawa daga Allah ne cikar mutum mumini yarda da k'addara me kyau da mara kyau.amma wani abu yakan samu d'an adam wani ya zama shine mujaza faruwan al'amarin,saboda haka ina me tabbatar muku da cewar wannan abun da ya faru to daga sama ne kuma wasu ne suka zama silar faruwan shi,  zan muku misali. D'azu misalin k'arfe shida da rabi na yamma kun Sanar  a k'afafun yad'a labaran Ku cewar 'yan kasuwa su dakata da futa sai zuwa ranar da gomnati ta umareshi, kafin awa guda da yad'a labaran Ku kuma Ku k'ara 'yada wa cewa umarni daga gidan

gomnati wannan magana an janye ta, da wannan nake rufe magana ta, dukkanin ku kuje ku tsaya kuyi binkice kanta sai Ku samu abun yad'awa a duniya." Tsitt!!! Gurin yayi tun sanda ya fara magana har ya k'are kowa na sauraren sa, wucewa yayi da sauri yaran shi suka rufa masa baya. Kafin kace kwabo gurin ya kara hargitsewa kowa na fad'in albarkacin bakinsa, mutane da dama sun fi zargin wannan al'amari daga abokan adawar sa ne, wasu kuma suna zargin daga gidan gomnati ne kowa dai da abunda yake fad'a.

Kai tsaye hospital Malam Aminu kano suka nufa, sai da ya tabbatar da duk Wanda ya samu hadari a jikinsa ya samu kulawa sannan hankalinsa ya kwanta. Suka kara dawo wa da company Wanda har yanzu ake aikin gurin tare da futo da kayan da sukayi dame ji wasu a jibgi-jingi wasu sun ci wuta wasu kuma ta fara cinsu basu gama k'one wa ba, sama da k'asa ko ina ka kalla bak'ikirin babu kyawun gani babu wani abun da za'a mora a gurin. Wani ofis ne a harabar gurin, nan yaranshi suka shiga suka gyara mishi dake akwai guraran da wutar bata same su a kasan gurin, nan ya shiga ya kwanta kan wata k'atuwar kujera ya rintse idonsa zuciyarsa kamar zata futo fili.babu Wanda ya fad'o masa a rai sai mahaifin sa, a take ya mik'e ya dauro alwala ya shimfid'a abun sallah dai-dai ta tsayiwarsi yayi gaban sarki jallah wa ala yana mik'a mishi bukatunsa, sosai yayiwa iyayansa addu'a ya shafa, sai yaji zuciyarsa tayi sanyi, a gogon hannunsa ya kalla uku da rabi na dare, har yanzu yana jiyo hayaniya,jama'a a waje da alama har yanzu basu gama futo da kaya ba, mik'ewa yayi ya nufi window tare da dage labulen yana lek'en gurin. Aiki kurum suke kamar kara cab'a gurin suke, ga uban kaya nan dila-dila a watse a harabar gurin duk sunyi dame ji. Ko mawa yayi ya zauna yana tunanin wane mataki zai d'auka kansu Alhaji Hashimu me citta dashi kanshi me girma governor nan.
A takaice dai *Amjad* da duk wani me kaunar sa a ranar kwana sukayi cike da bakin ciki gami da damuwar abunda ya faru. K'arfe shida dai-dai na safe k'afafun yad'a labarai suka fara labaran su, inda kowa ce tasha ka kunno a lokacin sautin muryar *Amjadu* ce inda yake yiwa 'yan jarida baya ni. Tofaaaa!! Gari ya haustine kowa na zagin me girma governor tare da fadin cewar da sanya hannunsa haka ta faru tunda shi Amjadu a baya nin da yayi yayi magana me kamar jiryewa Wanda hausawa suke cewa me kamar Wanka. Tuni k'ananun'yan kasuwa suka shirya zanga-zanga tare da makamai da tayoyi suka nufi gidan gomnati. Matasan gari marasa aikin yi suma suka rufa musu baya. Hankalin me girma governor ya kai k'oluluwar tashi! Sam! Ba zaici haka jama'ar gari zasu tada hankalin su ba, tuni ya baza matakan tsaro cewar a tsare hanya kar a bari kowa ya k'araso a rufe titi gami da dakatar da ababen hawa.

Muna zaune a rumfa ni Mimi Ummanmu muna karyawa sai ga Yaya Aminu ya shigo hankali a tashe! Umma tace." Yaya ka dawo kuma."? Cike da tashin hankali ya zauna kusa da ita tare da fad'in" Umma ina naga ta futa zuwa skull gari ya hautsine!!! Tace." Me yake faruwa ne. " yace." Wai ina redion ki ne tun jiya ake tashin hankali a gari an je an kone company nan me zaman kansa. " tace." Wane company ni ne."? Baki na rawa Aminu yace." *Amjadu AbulAbbas materials* dummmm!!!!!? Gabana ya buga na tsurawa bakin Yaya Aminu ido ina kallonsa. Umma tace." Ni ko a bakin wa naji wannan sunan."? Mimi tace." Bakin aunty Hauwa." Tace "yawwa hakane " sai kuma ta rafka salati tana tada hannunta cike da tashin hankali.
Ni da Mimi muka kalli juna rai duk babu dad'i. Umma tace." Ni ina zan sani redio ta ta lalace dama wayata nake kunnawa to kasan jiya bamu kwana da wuta ba." Yaya Aminu yace." Aikuwa

gari a hargitse yake domin 'yan kasuwa sunan nam suna zanga-zanga kuma an hana futa da abun hawa. Umarni daga governor. "
[10/27, 12:00 AM] 👄: Umma tace." Gaskiya na jinjina wannan al'amari ikon Allah ko meye ya haddasa gobarar oho. " yaya Aminu yace." Mutane dai suna zargin 'yan adawarsa ne, wasu kuma suna zargin da sa hannun gomnati har yanzu dai an kasa gano meye ya haddasa gobarar." Cike da al'ajabi Umma tace." Ai dole yaron nan yayi makiya da mahassada wallahi tunda yana son talakawa da tsoron Allah, kaga kuwa masu kud'in kasa zasu sanya shi a gaba." Yaya Aminu ya mike tare da fadin 'Bari in karb'i wayar Garba yayi rocouding din muryar shi lokacin da yake jawabi ke kanki Umma ki ka sauarari maganar sa zaki San abun shiryayye ne." Futa yayi ya barmu da jiki a sanyaye, niko tsabar zura jiki sai na fara tunanin ko a wane hali yake ciki.har na k'agara Ya Aminu ya kawo wayar inji muryarsa wani irin mugun tausayin sa na damun zuciyata, to b'angaran Mimi ma haka yake domin ita har ta fara k'ananun hawaye.

Ya Aminu ya shigo da waya a hannunsa ya zauna kusa da Umma ya kunna mata voice din *Amjadu* lokacin da yake magana da 'yan jarida jiya.

Tunda ya fara maganar nayi sak! Ina sauraron sa, muryarsa radau! Kamar Wanda baya cikin tashin hankali babu karaya da rawar murya a lafazin sa, kana ji kasan shine me gaskiya, Umma tace." Ai daga jin wannan maganar ma kasan shiryayyiya ce makirci ne, kawai da hassada kuma zakaran da Allah ya nufa da cara sai yayi." Yaya Aminu yace" Wallahi kuwa Umma, nake fada miki, guy yayi a rayuwa yana mutukar kaunar talaka da cigaban matasa Sam dukiyarsa bata rufe masa ido ba, dukiyarsa ta talakawa ce gami da mabukata da marayu, to Kin San an ce mutum tara yake bai cika goma ba, duk da haka mutanan gari suna zarginsa da neman mata wai har hotal ne dashi da karuwai suke watse wa." Umma tace." Wa'iya zubbilah kai jama'a mutane ba a iya musu dama hakane duk inda Allah ya daukaka bawa to sai ya samu yan hassada Allah kasa mufi k'arfin zukatanmu." Yaya Aminu yace" ameen suma ameen. Suka cigaba da tattauana maganar.ni da Mimi shiru babu bakin magana, tunda ya Aminu ya fara maganar sa nake addu'ar Allah yasa sharrin mutanan gari ne guy baya Neman mata, domin a lokacin ji nayi wani irin Abu yazo min wuya na bakin ciki. Wani gefe na zuciyata Yace min a kanki zaki gazgata shin shi din mane min mata ne ko kuwa bayan ke ga Alina,, kuma zuciyata ta dinga min sak'e-sak'e a kanshi gefe guda kuma ina tunanin ko wane hali yake cikiA yaanzu

******
Duk inda aka zauna can kenan gungun matasa da magidanta 'yan kasuwa kai har da ma'aikatan ma suma wasu daga cikinsu suna jajanta al'amari, waya kuwa *Amjadu* har daina d'agawa yayi da k'arshe ma da abun ya dame shi, rambow yasa ya kashe wayoyin gaba d'aya. Ya kulle kanshi a daki shi kad'ai duk irin mutanan dake zuwa gurin shi ya hana a shigo dasu." Tv ya k'ura ido yana kallon labarai na k'arfe goma dai-dai tashan NTA sosai ya girgiza ganin yanda matasa suke tashin hankali a gari tare da kona tayoyi had'e da rigima da 'yan daba mutanan me girma Governor jama'ar gari sai gudu suke, wannan al'amari da ya faru ba iya kacin najeria ya tsaya har kasashen waje suma sai da suka nuno Company tare da rigimar da ake yi a kano din cikin labarai su na safe.

Mik'ewa yayi da sauri ya futa waje. Suna ganin futowar sa suka k'araso dukkanin su. Ya kalli Doh-doh tare da umartar sa da maza yaje gidan redio na express ya d'auko masa d'an jarida daya yana so zai yi magana.

Doh-doh ya wuce ya tafi cikin sauri. Nan harabar gurin ya zauna gurin hutawa yana sauraran dawowar sa, minti talatin a tsakani sai gasu sun shigo, ba tare da b'ata lokaci na Dan jarida ya gyara na'urarasa domin d'aukar muryar Amjadu

A nutse yayi bisimillah ya bude da addu'a sannan ya fara magana kamar haka.

*Ni Amjadu Abul Abbas ina kira ga jama'ar gari  da duk wani d'an kasuwa matasa majiya k'arfi da duk wani me kishin kasa da duk wani me kishin kansa ina kira da babbar murya cewa in dai akaina kuke wannan zanga-zanga da ta hankalin Wanda basu ji ba basu gani ba, to maza Ku janye bana buk'atar haka ni Amjadu!! Nafi bukatar zaman lafiya a garin kano, saboda haka ina kira a gare Ku Ku aje makaman ku mu fuskanci abunda yake ga banmu ina me tabbatar muku da cewa ko yanzu kun tauna tsakuwa domin aya taji tsoro, shi Wanda kuke yin abun dominsa na tabbatar yanzu yana can hankalin sa a tashe, hausawa suka ce ruwa cikin cokali ya ishi me hankali yayi wanka tsalla d'aya  tak!!! Za kayi ka fad'a rijiya amma sai kayi dubu baka futo ba.......Daga k'arshe nake muku albishiri da cewar duk wani Dan kasuwa da yake jin takaicin abunda ya faru to Ku kwantar da hankalin Ku sati guda yayi yawa gurin kara k'irkirar muku sabon Company me zan kansa wannan karon abunda company na na baya baya kawo muku to wannan sabon zai kawo muku samfura kaya kan farashi me sauk'i........Ni ne naku *Amjadu Abul Abbas Mai nasara!!!!!!!!*

!Yana gama maganar shi ya mik'e da sauri! Ya bar gurin d'an jarida yayi saurin nad'e kayansa yana k'okarin tafiya. Nan doh-doh ya umareshi da ya tsaya kar ya tafi.  Amjadu ya futo da kud'in cikin wata farar takarda ya mik'a masa, ya karb'a yana godiya sosai da sosai sannan ya tafi.

Cikin gidan ya koma a gurguje yayi ya wanka ya futo yana goge jikinsa wani mutsiya cin yadi ya dauko piltex me mugun kyau da tsada gashi cotton bashi da nauyi ko kad'an kamar net haka yake kalar shi darkblue!! Sai yayi amfani da singilet fara tas!! Ya dora rigar akai kana ganin hasken singilet din, shi kansa d'inki abun kallo ne,  ya gaji da had'uwa sosai ya tsaya gaban mirror yana gyra links din hannun rigar ya taje sumar sa tare da sanya mata maya mayai sai shek'i take. Mugun turaran shi ya d'auka  ya feshe jikinshi, hula irin ta hausawa sam! Bata dame shi shiyasa bashi da ita ko guda d'aya suma kayan hausawa din yana d'inka su ne domin amfanin wata rana kamar zuwa d'aurin aure gaisuwar mutuwa ko shiga cikin wani babban taro amma Sam! A tsarin sa babu manyan kaya. *Ni ko nace *Amjadu da kasan yanda kayan hausawa suke maka kyau da ka dinga sakawa oh! Dama dai zaka sanya hula damanga nasan ba k'aramin kyau zaka yi ba, hummm!! Kuna ina ne  mutanan Amjadu ya kuka hasko mutumin NAKU cikin manyan kaya😄👌🏼 nima na dan gwala masa domin na k'yasa😉🏃🏻‍♀️🏃🏻‍♀️*

Wani helf cover naga yana sanya wa a k'afar shi fara Tass! Da ita kafa kamar bata namiji ba, ga wani ya tsunsa gashi sun bi sun kwanta abun sha'awa takalimn blue ne amma sky ya d'aura agogon shi Rolex mai mugun tsada. Cike da karsashi da jarumta ya futo , suna tsaye bakin kofa suka rufa masa baya. Rbow ya bude masa mota ya shiga suka futa daga gidan.

********

Take tashar express redio ta saki muryar Amjadu a gari, gari ya d'auka dattawa wadanda sukan sa meye duniya suke fadin "Yaron nan mai hankali ne da sanin ya kamata gashi dai karami ne me k'ananun shekaru amma yana aiki irin na manya ya iya lafuza masu kyau abunda ya kamata ace gomnati ita zata tsawayar ta kasayi shi ya futo yanayi tabbas wannan yaron zai dace da zama shugan kasa kuma shugaban al'umma domin irinsu ake so masu sanin ya kamata"!!!!........ Tofaaa!! Muna zaune muna zancan Yaya Aminu ya shigo da sauri hannunsa rike da wayarsa yana fad'in Umma kinji kalaman Young millionaire ko kai!!!! Gaskiya guy nan Dan aljanna ne wallahi." Umma ta karb'i wayar tana sauraron muryar Amjadu fuskar ta cike da farin ciki. bayan ta gama saurara tace." Allah yayi masa albarka kuma ya bashi mace ta gari wannan yaron sai naji ya shiga raina sosai." Yaya Aminu ya futa da sauri yana fad'in "Bari in mai da wa Garba wayarsa . Jiki a mutukar sanyaye na mike salau-salau na shige kuryan dakin Umammu na haye gado tare da rintse idona gabana na fad'uwa tun da Naji muryarsa na rasa kuzarina narasa wace irin masifa ce wannan.

**

Babu inda suka yi wa tsinke sai Company nan ya tarar da Aiki yayi sauki domin duk abun futo da matattatun kayan da suke ciki gami da na'urorin da suka samu matsala matasa majiya k'arfi suna ta aiki, gaskiya ya yabawa korarin su da kuma kaunar da suke masa, tsaye yayi a harabar gurin hannunshi goye a baya yana nazari, abun mamaki sai ga 'yan jarida sun yi masa caaaaa! A ka dama shi suke jira ya zo.

A nutse ya kalle su. Shi dariya masa suke bashi yace." To yanzu me kuke so nace wai." ? Daya daga cikinsu yace." Ranka ya Dade kace mutane su janye zanga-zanga da sukeyi shine muke Neman Karin baya ni."
Sosa kansa yayi ya saki wani killer smile wanda shi kadai ne tasan ma'anar sa yace."duk wani bayani da zan muku yanzu bazai gamshe Ku b, so yanzu dai abunda zance shine, duk wani mubukaci yana iya zuwa wannan company ya dauki duk abunda ya ke so na abunda akayi

asara saboda ina so in fara aiki a gurin." Daga haka yaja bakinsa yayi shiru . aikuwa sun samu abun ya ya tawa atake suka fara sanarwa kafin kace kwabo zance ya baza gari mutane suka fara tururuwar tafiya domin su kwashi garab'asa

*27/October/2019*
[11/1, 10:55 PM] .: *BABBAN YARO*

*Mallakar_BINTA UMAR*

*LITTAFIN MALLAKI NA NE KUN BIYA KUD'IN KARATU NE KAWAI DUK WACCE TASAN ZATA FUTA DASHI WAJE DON GIRMAN ALLAH TAYI MIN MAGANA NA DAWO MATA DA KUDIN TA*.

*31*

Muna shirin cin abunci na rana sai ga aunt Hauwa ta shigo da sallama a bakinta. Muka amsa tare da yi mata sannu da zuwa, Umma na kicin tana rabon abunci tace" ke kuma daga ina kike ana rigima a gari kika futo."? Aunt hauwa na dariya tace. "Wallahi Umma daga gida nake ina gidana ina nan si babu nisa." Umma tayi shiru bata ce komai ba. Nace "aunt Hauwa ina Islam take."?
" Tana gidan Maman fa'iza na barta, saboda cikin jama'a zamu shiga." Nace." Aunt Hauwa ina zakije gari babu lafiya. " tace." Bonanza zan je in kwasa a kyauta kuyi maza Ku gama ci mu tafi don Allah kar a kwashe kayan." Umma tace." Wai ina zaku ne."? Aunt tace" Umma duk abunda ke faruwa baku sani ba."? Umma tace" sai kin fada mana yanzu."

Aunt hauwa tace." Garab'asa ga me rabo Umma kinsan anyi gobara a wannan company Dana ke baki labari ko." Umma tace"eh mana ai tun dazu muke cikin jimami da alhini." Aunt Hauwa ta cigaba da cewa"yanzu ya bada damar duk wasu kaya na ciki aje a kwashe su zai fara aikin gurin shine fa na wanko kafata in je in kwaso garab'asa." Girgiza kai Umma tayi tace." Ke kam ban San inda zaki kai kudi ba wallahi!" Dariya mukayi ni da Mimi aunt ta hau zaginmu tare da fadin " in baku zuwa inayi tafiya ta wallahi kuma duk wacce taga Abu a gurina tace tana so ubanta zanci" cikin dariya nace" zamu je Wallahi ko Dan mu bawa idonmu abunci, ko Mimi"? Daga kai tayi tana dariya aunt tace." To maza Ku tashi mu ganshi omin ban yarda ma Ku tsaya wani Wanka da kwalliya ba." Zare ido nayi nace." Gaskiya sai nayi Wanka dube ni fa, sai maiko nake. " mik'ewa tayi da sauri tana kallon Mimi tace "tashi mu tafi Mimi" ta mike da saurin ta! Nima na mike dakinmu muka shiga muka d'auka zurma-zurman hijabai muka futo, Umma tace"tafiya zakuyi baza bari Ku ci abunci ba" aunt tace" Umma in mun dawo maci" tayi gaba da sauri!

Tsayawa nayi bakin kicin din nace." Umma bamu kud'in ankon sai mu biya kasuwar kinga mun huta ma." Mik'ewa tayi ta shiga daki minti biyu ta futo da kudi a hannunta tana lissafawa dubu goma sha bakwai ne tace." Akwai kudi hannun auntnku ta cika muku." Na karb'a da sauri ina fadin" sai mun dawo Umma" tace"Allah ya kiyaye kar kuyi dare kun jiko" nace" insha Allahu Umma.

Can nesa na hango Aunt Hauwa da Mimi suna tafiya kafin in karasa hat sun tarar mana me a dai-dai muka shiga da sauri aunty cewa take" yayi sauri sauri" aikuwa ya fafari mashin kamar zai tashi damu sama.

Wai!!!!!!!!! Cunkus!! Kenan tunda muka sauka daga babur nake hango dandazon mutane bakin wangameman gete din suna turereniyar shiga gurin sai buge-buge ake maza da mata.
Aunty Hauwa nake kallo dake k'okarin tsalla titi nace." Aunt Hauwa tana ina zamu kutsa mu shiga cikin jama'ar nan."? Hararata tayi tace." Ta inda kowa yake shiga muma tanan zamu shiga." Kallonta nayi cike da mamaki nace." Ni kam wallahi bazan shiga a dauje ni a banza ba bayan haka kuma guri duk ya cika da garada maza daga ganin su za suyi tsamun hammata! Takaicina bai bar aunt tace komai ba ta kama hannun Mimi suka tsallaka titi suka barni tsaye a gurin. Ina kallonsu suna ta kutsawa cikin mutane har na daina han go su. Mintuna ashirin ina tsaye a bakin titi rana sai dukan fuskata take ga uwar yunwa dake sasakar cikina, tuni goshina ya soma tsatstsafo da gumi na fara jin jiri. K'okarin tsallaka titi nake in samu wani guri in zauna in jira su domin ni kam bazan shiga cikin wannan wahalar ba." Gefen wata bishi na zauna ina kallon yanda jama'a suke futo da kaya a daure wasu na shiga wasu na futowa. Da sauri na mike tsaye ganin wata budurwa ta futo hannunta rike da wani dogon abu tana ja da k'arfi k'ura idona nayi sosai sai naga irin material dinmu ne sak!! Na anko har kalar bandir guda ta samo a ciki 'yan uwanta sun biyo ta yuuuuuuuu! Da sauri na k'arasa gurinsu ina mik'a kaina domin in gani sai naga Sam! Bai samu matsala ba illah jik'ewa da yayi da kuma bak'in da ya fara kama jikinsa Dan ma kalarshi me haske ne, amma Sam bai kone ba." Sai murna sukeyi suna kasafi tun basu

je gida ba, sai naji kamar in ce musu su yan karmana domin komai abunsu yayi musu yawa Dole su bawa wani.
Zuciyata tace min kema ki shiga ki gani ko Allah zai sa ki samu kin ga kud'in Umma sun huta, kun samu kud'in siyan takalma da haka, aikuwa ban tsaya tunani ba na durfafi kofar shiga,INA addu'ar Allah yasa na samu nima ko Mimi ta samo mana.

Daf! Da zan shiga ciki. Na hango rambow yana buge mutane dake kan hanya tare da fadin" tunda dai magana ta fatar baki batai muku ba to bari a gwada muku k'arfi da bulala duk idon Ku ya rufe, ana ta magana tun d'azu Ku bada hanya za a wuce kun ki Ku bayar."
Aikuwa sai mutane suka fara bud'e hanya cike da tsoro ganin babu Imani a don rambow.
Kafin in ankara na hango shi ya tawo cikin yanayin tafiyar sa ta jaruman maza doh-doh a bayansa da wasu 'yan jarida guda uku masu mugun nacin tsiya sunk'i tafiya. Neman gurin b'oya nake duk na gigice, da ganinshi Sam! Na tsani raini, nan take na fara Dana sanin zuwana gurin , bayana na waiwaye babu gurin b'uya mutane ne cukunsu suna Neman bangaje ni in fad'i saboda son ganin shi, 'yan matan dake gurin kuwa kamar su shid'e dan dad'i sai kara zura kai sukeyi tun kafin ya k'araso gurin ya hautsine da ihu!! Kowa na fad'ar albarka cin bakinsa akan sa,, nayi diri-diri dani gashi dai hanya ta rabu biyu gashi ina kusa da gete, daf da zai k'araso na sunkuyar da kaina kasa cike da takaici nake bin kojalallan hijabin jikina da kallo duk ya kode Allah ya isa nayiwa aunt Hauwa.

Dai-dai saiti na wani Dan jarida ya tsaida shi dole ya tsaya yana bashi amsa dai-dai da abunda ya tambaye shi.

Dan jaridar yace."* Young millionaire muna son mun san cewar yanda kake da masoya gaba da baya shin kana sha'awar siyasa ko kuwa domin ga dukkanin alamu matasa da dattawa na mutukar kaunarka kuma kai ma zakayi kyau da mulki domin anfi bukatar jajirtattu irin Ku.." Wannan maganar tasa ya tsaya yana basu amsa kamar haka.

*Sam!sam bana sha'awar siyasa bani da ra'ayin ta domin babu komai a cikinta sai zubewar mutumci bayan haka kuma ka dauki alk'awari ka kasa cikawa bana sha'awar mulki ko wane iri ne shine magana ta* gurin ya hautsine da sowa matasa na fadin "Mu muna sonka kuma zamu tsaya maka lokacin zab'e." Abun mamaki har 'yan matan dake gurin ma ihu suke yi cike da rashin kamun kai. Takaici yasa na kasa dago kai na kalle su, Allah-Allah nake ya bar gurin. To shima nashi b'angaran haka ne lallai ya yarda da aikin Jarida su ne suke tsokalowa mutum tsuliyar doh-doh yana zaman zaman sa zasu jawo masa wata uwa Siyasa sun ki su k'yale shi sai tambayar kwakwa suke masa..........Dama abunda suke so su ji kenan daga bakinsa don haka sai suka k'yale shi. Gani ya kusanto inda nake tsaye yasa na kara sauke kaina kasa kamar wata muna fuka, ya karaso cike da jarumanta yana dagawa mutane hannu fuskarsa a sake, take sosai. Wani matashin saurayin ne majiyin k'arfi ya ingiza ni gaba duk a. K'okarin shi na lallai sai Amjadu ya ganshi
Saura kad'an kaina ya daki k'irjinsa nayi saurin rik'e gefan rigar shi Dan kar hakan ta kasance, gabana ya dunga bugawa fatt!!!fatt!! Kasa d'ago kaina nayi i n kale shi domin nasan k'aryar b'oye b'oye ta kare, Allah ya Isa kwai nake wa saurayin nan................ Gefen fuskarta ya kalla

ya gane ta, mamaki fal! Cikin zuciyarsa me ya kawo ta gurin nan cikin garadan maza don tashi kamun kai...Fuska!! Yayi kamar bai tab'a ganin ta ba ya mugun had'e fuskarsa tam!! Ya wuce abunsa! Ya ransa na binshi a baya, jama'a sai a sauka lafiya suke masa.

Zama yayi cikin motar zuciyarsa babu dad'i, ya kalli Rambow murya a sama yace"waccan yarinyar me ya kawo ta gurin nan.?" Rbow ya diririce! Ganin yanda ogan nasa ya tsare shi da ido! Yace." Boss myebe tazo itama ta samu rabonta ne." Cike da taikaci yace." Jeka zo min da ita." Rambow ya tafi da sauri! Dube-dube kawai yake a gurin bai ganta ba, ciki ya shiga nanma ya dunga ware ido cikin jama'a babu ita,  ciki ya shiga sosai yana dubawa.

Ni ko na shiga ciki sosai ina Neman su auntn Hauwa sun bace min cikin mutane, nan cike da takaici da haushi na futo daga wani sako inda naga wasu mata sun taro a gurin suna jidar kaya, hanyar futa na nufa raina a dugunzume ! Ina jin takaicin kallon banzan da guy nan yayi ya ma nuna kamar be sanni ba  lallai ma!! Ga takaicin su aunt Hauwa ya hana ni magana. Kawai naga an tari gabana. Ina daga kaina muka hada ido da Rambow naji faduwar gaba, amma dake ina da taurin rai! Nace." Meye haka." Yace." Boss ne Yace." Kizo." Hararársa nayi nace "ni matsa don Allah 'yan uwana nake nema mu tafi gida." Rbow yace." Yace in kiyi gaddama to in daukoki aka in kai masa ke.."
[10/28, 10:35 AM] .: Shek'e ke na kalle shi na sha kunu mutuk'a nace." Bisimillah sai ka d'aukar masa ni ka kai masa wallahi idan baka matsa min daga nan ba zan maka ihun kwarto in tonawa uban gidan naka asiri a gaban bainar jama'ar da suke ganin mutumcin sa." Ganin yanda nake zare ido ne yasa rambow Ciro wayarsa ina jinsa yana fadin" Boss gatanan tana gadda had'e da surutai." Ban ji me ya ce ba, kawai naga rbow ya mik'o min wayar. A banza ce na kalle shi shi da wayar na watsar tafiya na fara yi, rambow ya biyo ni a baya, ganin rbow ya nufo kofar futa ne yasa jama'ar dake kan hanya suka bud'e hanya na wuce huff!!! Da sauri na b'uya bayan wata mata, aikuwa yaron ta dake goye a bayanta ya kwala ihu ta juyo da sauri tana k'okarin sauke shi, wannan ya bawa Rambo damar gani na. Tsaki nayi na futo daga bayan matar domin bana so jama'ar dake gurin su fuskanci wani Abu,kawai sai nayi gaba, to dake suma hankalinsa na kan duba kaya Sam! Babu Wanda ya damu dani.

Tunda ta doso bakin titin yake kallonta yaga fuskarta sai shaining take ta wani kara bak'i. Tsaki yaja cikin zuciyarsa yace." Saboda rashin abinyi ta futo daga gida sai kace korarriya ko 'yar gudun hijira. Daba Dan yayi mata kyakyawan sani ba Sam ba zai ce ita CE ba. Yana kallon rambow nayi mata magana ta share shi. A fili yace "dama irinku munana kun fi wulakanci.

Asma'u kuwa kai tsaye titi ta nufa ta fara tafiya domin yanzu hankalinta yayi Gida ta nemi su aunt Hauwa ta rasa ga Uwar yunwa na damunta gefe guda kuma matsanancin tsoron rbow ya fara shigar ta ganin da tayi yana bin ta duk inda ta sanya k'afar ta sai kace tsohon maye titi ta mik'a sosai tana Neman a dai-dai ta sahu. Tsoro take kar mutane sum ganta da rambow din.

Umarni ya bawa doh-doh kan ya ja motar a hankali ya fara Jan motar har suka iso daf! Da ita, sauke gilashin motar yayi . gabana ya fad'i nayi saurin kauda kaina gami da kara sauri!!! Rbow

ya tari gabana cike da b'acin rai! Yace
" kawai ki bi umarni shine mutumci ki domin duk Babur din da kika tsayar baza mu barshi ya d'auke ki ba, kije kiji me oga zai fada miki."

Babu yanda na iya haka na koma baya fuskata kirne....... Na tsaya gaban motar INA kallonsa gami da fadin "gani" girgiza Kai yayi fuskarsa a had'e yace." Shiga mota mu tafi."

Shiga mota mu tafi." Na maimamata maganar da yayi a fili cikin sigar tambaya.?
Kai ya gyda min yana wani lumshe min mutsiyatan idanunsa masu dafi.! Kai tsaye! Nace" ina zaka kaini in na shiga motar taka."? Kallona ya danyi a fakaice yace." Gidanku. Naga rana tayi kingaji ga alamu nan sun nuna fuskar ki sai maiko take sai kace an toya mankuli.
Da sauri! Sanya gefan hijab dina na hau gogewa ina zabga masa muguwar harara. Murmushi naga yayi ya Dan kanne min ido daya cike da iya shege! Kauda kaina nayi cike da takaici nayi gaba da sauri!! Hannusa ya zuro ta tagar motar da k'arfi ya rike min gefan hijab dina, yana fad'in " yarinya za'a taimake ta tana k'i saboda tsabar gaddama idan baki shigo ba zan zo in d'auke ki a ka". Yanda ya fad'i maganar yasa na juyo ina kallonsa a fusace!!! Nace "Sakar min hijabi na." Shan kunu ! Yayi sosai ya kalli rbow yana masa magana da ido! Tsorata nayi ganin rambow yayo kaina gadan-gadan, da sauri na bude mota na shiga! Gefe naga ya matsa yana d'an ya mutse fuskarsa bai ce komai ba Rambow ya maida murfin ya rufe ya zagaya kusa da doh-doh ya zauna sannan muka tafi.

A hankali naji yace. " Rambow mik'o min turaran k'amshin nan." Wani durmeman turare rbow ya miko masa cikin kwalinsa ya bude ya hau fesawa cikin motar ya dawo kaina yana min feshi, saurin kauda kaina nayi ina kare fuskata, lokaci kankani na fara atishawa, sai da motar ta d'umame da kamshi sannan a maida turaran cikin kwalinsa.

Yanzu na gane dalilinsa na fesa turare cikin motar wato yana nufin wari nake kome? Aikuwa kafin in gama tunani na naji shi yana fadin." Duk kin sauya min k'amshin motar da warin rana 'yan mata masu daraja." Shiru kamar ruwa ya cinye ni, ji nake kamar in d'aura hannu aka in ta kurma ihu! Ko nasamu sassauci a zuciyata nace ban tab'a ganin Mara mutumci ba irin guy nan wallahi.

*Ni ko nace Ashe babu dad'i Asma'u ita Hafsa ba mutum bace kenan😄*

Kafin in gama tunani na naji shi yana fad'in" muje gida ki dauki a jiyar ki dama Neman ki nake." Kallonsa nayi da idona da ya fara ciko da kwallah nace" wace ajiyr ? Kaga malam ka kaini gida kamar yanda kace cikar mutum rike alkawari." Murmushin gefan baki yayi na kauda kaina ganin yanda yayi wani bala'in kyau kullum kara mishi kyau ake da kwarjini yadin jikinsa yayi masa bala'in kyau!!! Yace." Kin manta ne kawai amma muje zan nuna miki ko meye? Nace." Babu

inda zanje ni."

"owk wai ma me ya kawo ki gurinan ne kina a matsayin mace me daraja kin zo kina bugun kirji da gogayya da maza wannan shine darajar."? Ya fada cikin sigar tambaya gashi ya wani sha kunu!
Rashin abun cewa ne yasa nayi shiru ina sadda kaina kasa nasan dai wannan tambayar da yake min ta rainin hankali ce tunda dai ya san ko meye ya kawo ni........."Uhum ke nake sauraro."? Yafad'a cikin wani irin hosky voice, ji nayi jikina ya soma rawa muryar da yayi amfani da ita tayi bala'in tasiri a gare ni.... Shiru nayi kawai yace." Ok na fahimta." Yanda ya fad'i maganar yasa na d'ago Kai ina kallonshi cike da jin haushi nace" kar kayi tunanin muma munzo ne domin mu d'ebi sharar company nin ka, ko d'aya hanya ce ta biyo damu ni da 'yan uwana." Na k'arashe maganar a daburce!! Wani kallo yayi min kana ganin kallon kasan na iskan ci ne a hankali yace." Allah ko."? Nace." K'warai kuwa domin ni banzo nan domin in samu sutturar sawa a jikina ba tunda ina dasu." Munafukin murmushi yayi yace." Shiyasa naga kin dage kina gogayya da garada kina turmutsawa cikin jama'a domin ki shiga to me zaki shiga kiyi uhummmmm."!!!!!! Wasu tagwayen hawaye ne suke k'okarin tsinke min.sai na aro dauriya da jarumta na kalle shi had'e da kankance idona nace." Eh hakane to yanzu ai sai ka duba ka gani ko na d'auko wani Abu da na shiga ciki. Ma 'yan uwana nake nema mu tafi gid............. Katse ni yayi ta hanyar fad'in" wannan duk preetandig din da kike bashi da amfani ni dai nasan duk Wanda yazo gurina to akwai abunda ya kawo shi." Da sauri na bude handbag dita na Ciro kud'in ankon mu cikin gadara nace." Kaga kudinmu nan yanzu haka kasuwa zamu shiga muyi siyayyar kayan sawarmu babu abunda kayan ka zasuyi mana." Kud'in ya wafce!! Daga hannuna." Na kalle shi a tsorace! Cikin aljuhu ya zura. Nace "me kake nufi"? Ba tare da ya kalle ni ba yace." Nima Dan kasuwa ne bayan haka kuma dama na karye makiya sun taso ni a gaba ina Neman jari ki taimaka ki bar min su." Nasan Neman magana yake kawai sai naja bakina nayi shiru.

Shima shiru yayi bai sake cewa komai ba, minti biyar a tsakani wayarsa ta fara k'ara, d'auka yayi cike da karsashi yayi sallama, naji yana fad'in"Kanwa takar tsami kwarnafi ya kwanta me citta burinku ya cika." Banji abunda yake ce masa, sai dai ganin da nayi ya zabura!!! Had'e da dukan glass din motar da hannunsa yace." Da kai da shi me girma governor dukanin Ku a tafin hannuna kuke wallahi akawai ranar tonan asiri. Kuma Ku zuba ido nan da sati guda kuga abunda zai faru."

Yana gama maganar shi ya kashe wayar gaba daya yana wani irin huci!
Kallonshi nayi a sace sai naga fuskarsa a had'e kamar bai tab'a dariya ba, kauda kaina nayi kurrum ina sak'e -sak'e a zuciyata a game dashi.

Shiru motar sai gudu take zubawa kan kwalta babu Wanda yayi magana, a hankali naji yace." Doh-doh juya da motar nan muje Mudansir and brothers dake Sharad'a kwanar ganduje." Da sauri doh-doh ya juya motar yana fadin "Yes sir" ni dai shiru kawai nayi ina bin titi da kallo har muka Isa make kenan gurin inda naga manya manya motoci a fake a gurin had'e da had'addan 'yan mata masu aji da waye wa wasu na shiga wasu na futowa.

Parking yayi gurin da aka tana da ya futo da sauri had'e da budewa oganshi motar ya futo fuskar nan kamar hadari ya kalle ni cike da bada umarni yace." Futo mu shiga ciki ji zab'i duk abunda yayi miki."

Gabana ya fad'i! Na hau duba jikina cike da tsarguwa. Shima kallona yake yi minti biyu yace." Ki futo mana ai naji dad'i da kika sanyo wannan hijabin domin ya kara miki masifar muni nasan babu Wanda zakiyi wa kwarjini." Hararsa nayi tare da cewa." Ce maka akayi ina bukatar wani Abu a gurin nan." Girgiza kai yayi yace." Baki fada ba ni nayi niyar siya miki ai nasan kin fi k'arfin su Big girl."""" Yanda ya fad'i maganar a tsaye yasa na gane shagub'e yayi min. Cike da takaici na bude motar na futo duk sai na tsargu da kaina sai gyara hijab nake ina goge fuskata cikin wayancewa.

Gaba yayi cikin takunshi na jarumai na bi bayansa kamar munafuka, su rbow suka rufa mana baya.tunda muka doso kofar shiga mutane sukayi mana chaaaa!! Da ido sosai mussaman 'yan Matan dake gurin kai har da Matan aure ma, ma'aikatan gurin sai kwasar gaisuwa a gurinsa, yana amsawa ta hanyar daga masu hannu, ganin yanda 'yan Matan suke kallonsa ne ya bani haushi wasu kuma sai watsa min kallon kyama suke yi cike da raini da takaicin ganinmu tare dashi, sunkuyar da kaina nayi a zuciyata nace"Allah yasa dai kar jama'ar dake gurinan suma suyi min kallon 'yar gudun hijira.....

*28/October/2019*
[11/1, 10:55 PM] .: *BABBAN YARO*

*Mallakar_BINTA UMAR*

*LITTAFIN MALLAKI NA NE KUN BIYA KUD'IN KARATU NE KAWAI DUK WACCE TASAN

ZATA FUTA DASHI WAJE DON GIRMAN ALLAH TAYI MIN MAGANA NA DAWO MATA DA KUDIN TA.*

*32*

Masu tsaron kofar ne suka mik'e tsaye cike da girma mawa suke gaishe shi ya amsa a nutse, had.e da hawa stepe domin shiga ciki bayansa nake bi kamar munafuka, muka shiga, da sauri rambow ya d'auko masa wata lafiyyayer kujera ya zauna yana d'an nazarin gurin a nutse yace." Ku shiga da ita ciki duk abunda take so ta d'auka." Rambow yace." OK sir." Suka yi gaba ni kuma na tsaya, so nake mu hada ido dashi ya k'i ya kalleni har yanzu ina jin ciwon rashin mutum cin da yayi min a mota, na fi minti uku a tsaye bai ce min komai ba, nace" bani kudina ." ko kallo ban ishe ba. Ya d'auko wayarsa yana dubawa, k'aramin tsaki naja nabi bayan su Rambow ..... Shi kuwa Amjadu a tsarge yake zaune s gurin yasan dama dole haka zata kasance dashi a rayuwarsa ya tsani kallo wallahi bai San me yasa ba mata suke damunshi da kallon tsiya, tsaki yayi ya mik'e da sassarfa ya futa daga gurin, kai tsaye mota ya nufa

Yana barin gurin jama'a suka fara surutu wasu 'yan mata dake gefena naji suna fad'in" Ikon Allah ko meye alak'ar young millionaire da wannan 'yar talakawan dube ta don Allah wata mummuna da ita."

Ta gefanta tace." Kin San guy fa yana da tausayi da tausayawa talaka mybe kawai tausayi ta bashi ganin bata da sutturar arziki yasa ya kawo ta ta zab'a amma nasan yanda yake da kyau uwa uba dukiya babu abunda zai ci da wannan abar dube ta fa ki gani kamar kwancan hauka." [10/28, 5:44 PM] .: Wani k'ululun bak'in ciki ne yazo ya tokare min a mak'ogwaro na,wai me 'yan mata suka d'auki mutumin nan ? Ya ilahi sai kace shi kad'ai ne namiji a duniyar nan da har suke wannan maganganun, raina a dugunzume na isa inda suke, wacce tayi maganar na nuna da hannuna cikin kaushin murya nace." Ke ki kishaga taitayin ki, duk naji irin surutun da kuke a kaina to bari kuji wallahi nafi Ku iskanci idan tak'amar Ku a kano kuke to nima haka kuma ni 'yar bakin kasuwa ce karewar tashan ci dai-dai nake daku, duk muni na ban kai ki ba ke maganar banza kawai dube ki fuskar ki a k'one da bleccing. " ina huci!! Na karasa maganar. Cike da mamaki suke kallona wacce nayi wa rashin mutumci tayo kaina a fusace! Kamar zata Doke ni!! Dayar tayi saurin rik'e hannunta tana hana ta, kallon banza nayi musu nace." Tsautsayi yasa ki hannun ki ya taba jikina wallahi sai na karya shi." Dariya suka saka had'e da zare ido naji d'ayar na cewa "Kema Safiyya me zai sa ka ki tsaya fada da wannan kucakar salon ta gogo miki karzuwa talauci ne kawai yake damunta shiyasa ta zauce!!!! Suka kwashe da dariya. A zafafe! Na futar da hannuna na tsinka ma me maganar mari, ina kallon d'ayar nace" kice takk!! Kema ki

samu rabon ki." Shiru sukayi cike da mamaki suke kallona,, su Rbow suka k'araso gurin da sauri suna tambayar ba'asi banza nayi musu na matsa gefe gami da duba kaya kamar gaske har yanzu ban dauki komai ba.

Ina jinsu suna fada musu abunda ya faru wacce na Mara din tana share hawaye tare da cin alwashi a kaina ko kallo bata ishe ni ba, rambow ne ya tasa su a gaba har gurin biyan kudi suka biya sai da ya tabbatar sun shiga motar su sannan ya dawo gare ni yana min hayaniya, zare masa ido nayi cike da jin haushi nace "ni nace ina bukatar kayan gurin nan da za'a kawo ni har wasu banzaye su zage ni kuma in kyalesu bazai yi wu ba, kar ka dame ni."

Cike da mamaki rambow yake bin yarinyar da kallo chaaaa!!! Gaskiya tana da tsiwa!! Babu Wanda zai yi maganin ta sai *Amjadu* gurin ya bari kawai cike da jin haushin ta

Gaba nayi ina duba kaya burina kurum in hango material irin na ankon mu in d'auka tuna ya karb'e min kudina, da k'yar na hangu irin shi nacewa yaron gurin ya d'auko da sauri ya d'auko yana warware wa nace." Yanka Mana yado goma, sha biyar,har Munnu sai ta samu. Aikuwa da sauri ya fara yankawa ya nade sosai had'e da dauko wata k'atuwar Leda ya zura ya d'auko landing din shi ya yanka shima ya sanya a Leda da ban, karb'a nayi na bar gurin na nufi gurin takalma wasu plate na hango set uku had'e da jakkunan su golden ne sai shaki suke da alama fatar da akayi su mai tsada CE, nace wa yaron dake gurin ya Ciro duk ukun aikuwa ya Ciro da sauri ya dauko wata doguwar lede me tambari sunan Mai gurin wato Mudansir and brothers ya zura su dama jakar bata da girma sosai nan ya mik'o min nace" ka biyo ni dasu a baya don bazan iya d'auka ba." Aikuwa jiki na kyarma ya mike da sauri ni kuma na nufi gurin sark'oki wasu lafiyyayun Fashion na d'aukar mana sunji stons sai k'yalli suke da walwali daga zasu ja kudi masu kyau!! Nasa yaron gurin ya ciro mana agogo uku na zallar fata multi coular, gaba nayi yaro ya biyo bayana hannunsa nike nike gurin mayafai na nufa, nan ma na duba kalar material dinmu wato purple nace ya dauko guda uku jiki na kyarma ya dauko masu mugun tsada... Daga haka kawai na kad'a kaina nayi han har futa, rambow da doh-doh suka taso daga inda suke suka biyo bayanmu ni da Dan dakona suka karb'i kayan a hannunsa,, INA futa tana kara daure fuska tamau!! Na isa gurin motar tare da tsayawa tunani nake ina yake Sam banyi tunani yana cikin motar ba tunda me bakin glass ce tintac Rambow ya bude bayan motar ya zuba kayan ya rufe da sauri ya bude murfin motar. Gabana ya fad'i ganin shi a ciki nace Ashe yana kallonmu da duk abunda muke shiga nayi ina d'auke kaina, sautin wak'ar Joy ne yake tashi a hankali me taken *Because love me* shiru nayi ina saurararan wak'ar ko wane baiti kalaman soyyaya ne, muryar Joy akwai sanyi da saka nutsuwa sai naji wani irin yanayi a jikina nayi kasak'e ina sauraron wakar......... Shiru bai ce komai ba yana kwance cikin motar idanunsa a lumshe! Na saci kallonsa kad'an.. Sai naga bakinshi yana motsi da alama wak'ar yake bi...

*28/October/2019*
[11/1, 10:55 PM] .: *BABBAN YARO*

*Mallakar_BINTA UMAR*

*LITTAFIN MALLAKI NA NE KUN BIYA KUD'IN KARATU NE KAWAI DUK WACCE TASAN ZATA FUTA DASHI WAJE DON GIRMAN ALLAH TAYI MIN MAGANA NA DAWO MATA DA KUDIN TA.*

*33*

V

Sai da motar ta fara tafiya kan kwalata sannan ya bude lumsassun idonsa yana Dan gyara zaman shi. Agogon hannun shi naga ya kalla ya Dan girgiza kansa, kallona yayi nayi saurin d'auke kaina ganin yanda idonsa yayi ja, cikin  kasalalliyar murya yace." Kin samu abunda kike so." Banza nayi dashi kamar ban San yana gurin ba." A hankali yace." Mata masu daraja ina magana fa." Cike da takaici na kalle shi had'e da cewa"tunda ka karb'e min kudina ai dole in dauki abun kudina kuma dole ka biyasu." Babu yabo babu fallasa yace. " ni ko duka kayan gurin kika ce kina so sai in siya miki mutukar zaki min Abu daya." Ya karashe maganr a hankali saboda su Rbow. A hangunce na kalle shi muka hada ido a karo na biyu, gani nayi idonsa ya

kankamce ba kamar d'azu ba, nace" wane Abu ne."  Da idon shi ya nuna bakina." Na kasa fahimtar sa, yace." Kin gane ko"? Girgiza kai nayi cike da tsarguwa ganin yanda ya kurawa fuskata ido kome yake kallo oho!! Hannu ya kawo zai tab'a leb'ena nayi saurin gocewa ina watsa masa harara. Takure jikina nayi jikin kujera gabana na fad'uwa domin yanzu na fahimci abunda yake nufi.

Shima fuska! Yayi kamar bashi ba, ya dauko wayarsa yana latsawa ammafa fuskar nan tasa babu dad'i
Daf da zamu shiga layin mu nace "a sauke ni anan ya Isa." Umarni ya bawa doh-doh yayo parking yana tsayawa na soma k'okarin bude motar da sauri ya rike min hannuna. Cike da bada umarni yace." Doh-doh Ku bamu guri zamuyi magana." Aikuwa suka futa daga motar da sauri. Ni kuwa ai tuni na fara rawar disco jin yanda yake murzamin hannuna, so nake ince ya sake ni na kasa fad'i

Fuskarta ya juyo da tafukan hannunsa ya kurawa bakina ido a hankali yace." Ki zo muje gida ki dauki pant dinki kinji!!!! Na fuzge fuskarta da sauri ina addu'a kar Allah ya bashi nasara a kaina, yace." Meye haka kike ni babu abunda zan miki kawai ina so in rage damuwar da take damuna ne." Muryarta na rawa nace"kaji tsoran Allah Wanda ya hallice ka ka bude min kofa na futa.". Sosa sumar shi yayi yana min munafukin kallo yace." Zan bude miki yanzu amma ki bani in sha." Na kasa fahimta me yake nufi. "Kinji!!!!!!* Yafadi maganar cikin wani irin voice tuni naji kuzari ya sare jikina ya soma sanyi,, nace " ban fahimce ka ba."? Bakina ya nuna da idonsa yana lumshe min su. Suma ne kawai banyi ba a gurin tsigar jikina ta mike sha'awar shi ta yunk'oro min sosai, nima sai naji ina sha'awar abun. Nasihar Umma na tuna hankalina ya tashi sosai nace." Ni ba 'yar iska bace au!! Yanzu nagane nufin ka shiyasa kace dole sai kayi min siyyaya wato badan Allah bane ko? To ko ka bude min mota ko in Tara maka jama'a a gurin nan, nan dai unguwar mu CE,wallahi yanzu zansan ya a fasa maka gilashin mota a raka da dutse." Na k'arashe maganar cikin tsiwa tare da girgiza jiki cikin sigar rashin mutumci.

B'ata fuska yayi had'e da gyara zaman sa sosai cikin motar yace." Duk abunda kika fada zaki iya yi iya zama na dake na fuskanci halayyar ki, tab'e baki yayi yayi k'asa da muryarsa had'e da fadin " nima da wasa nake miki me zan ji a wannan bakin naki me cike da tsiwa da rashin mutumci." Nace." Oho! Dai Dan dai baka samu bane." A d'age yace." Ko na samu bana so a kai kasuwa dama dan naga kamar kina so ne yasa na fadin haka, kanki kika cuta." Yanda ya fad'i maganar yasa na fahimci nade tabar kunya yake da hauka, ganin yak'i yarda mu hada ido dashi nace." Ni dai bude min kofa na futa."! Handbag d'ina ya d'auka dake kan cinya ta ya bude lalube yake min cikin jakar babu ko kwabo sai cingum dina da wayata da kwanata biyu babu chaji saboda matsalar NEPA..... Wayar ya d'auka yana dubawa fuskarsa d'auke da murmushi ko name ye oho!! Yace." Wannan matacciyar wayar meye amfanin ta a gurin ki."? Kaina na sunkuyar kasa cike da kunya da taikaci wannam guy dan tonan asiri ne, ko ina ruwansa da wayata oho!!! Yace." Magana nake mata masu daraja." Ba tare da na kalle shi ba nace." Wayata tana da amfani a gurina tunda ana kirana kuma nima ina kira da ita babu ruwanka da ita..... Kai tsaye yace." Yar da ita zanyi kawai domin bata da amfani gashinan a kashe babu chaji!! K'okarin cillata waje yake ta window motar, cikin azama! Na rike hannunsa ina fadin kar

ka jefar mun da waya domin tana yi min rana..." Muje in siya miki wata." Yafad'a bayan ya jefar da wayar waje, cikin tsantsar takaici nace." Kai duk fa inda kasa gaba na sani wallahi duk wayon ka wato kwadayin waya yasa na bika ka kaini gidan ka kayi iskanci dani to na gane."!!! Kallonta yake cike da nazari wato ita tana zargin zai kaita gidansa da wata munufa Wanda shi kuma har ga Allah ba haka bane a zuciyarsa yayi niyyar siya mata wayar. Gyada kansa yayi yace." Ko yanzu ina da damar da zanyi duk abunda nake so dake a cikin motar nan, na k'yaleni ne kawai saboda son raina lukatan baya na samu dama akanki sosai bai sa na keta miki mutumci ba, so ki cire wannan maganar daga ranki duk sanda kika kara zagina da haka ranar zan baki mamaki wallahi, har sai na Kai ki gidana zai yi iskanci da ke, gaki a gabana baki karfina ba, ke kanki nafi ki sanin wacece ke. Kike min wannan maganar bazan. "
Yanda ya kausasa harshe yake magana yasa na soma yin sanyi, zumb'ura bakina nayi had'e da cewa"Ni duk ba wannan nagaji da zaman motar nan ka salla me ni." Ina kallonshi ya bude wani guri a cikin motar ya futo da d'aurin kudi guda uku ya tusa min a handbag jefo min yayi cinya ta tare da fadin " kika kuskura kika watsar min da kudi cikin motar nan sai ranki ya b'aci! Yana gama maganar sa ya bude murfin motar... Futowa nayi ba tare da nace mishi komai ba, wayata na fara k'okarin hadawa batir yayi nasa guri haka ma layi ka na.

Sai da suka futo da kayan tsaf! Suka jibge min su gaba suka shiga motar da sauri suka bar gurin... Yara na fara kira da gudu suka nufo ni na basu umarnin d'aukar min kayan muka tsallaka titi tare dasu.

Aunty Hauwa da Mimi Umma na zaune a tsakar gida sun baza kaya suna dubawa suna hirata ko ina na tsaya oho!! Sai sukaji sallama ta, dukaninsu suka dinga bin yaran dake sauke kaya da kallo cike da mamaki na salami yaran." Aunty Hauwa tace." Wato Dan ubanki nitsa kikayi ciki kika barmu da wahala muna Neman ki." Nace." Aunty Hauwa wace irin nitsa kuma ni da kuka barni a waje,, nayi neman duniya ban gan Ku ba."

Jawo kan ta farayi tana sambato! Cike da mamaki ta d'ago kai tana kallona had'e da fadin "Yana ga ledar Muddansi&Brots kuma." Shiru nayi. Take ta fara zazzage kayan suna dubawa cike da mamaki.

Umma tace." Asma'u duk a gurin kika samu wannan kayan, naga duk sabbi ne babu inda ya b'aci." Nace" A'a Umma me gurin ne ya siya mun su
Da sauri autn Haa tace." Kamar yaya me gurin? Kuna nufin *Amjadu*? D'aga kaina nayi cike da tsarguwa Mimi tayi saurin kallona jin abunda nace. Aunt Tace." Baki da hankali a ina zaki ganshi har ya siya miki wannan kayan.". Nace." Wallahi shine ya siya min, ya ganni a waje cikin rana mutane na turmutsutsu shine yace." Na shiga mota muje a siya min yaga ina bukatar suttura,shine fa mukaje muddanssr&brothers na sharada yace in zab'i duk abunda nake so, ni ko na duba mana anko mu." Kallona suke tunda na fara maganar sun kasa cewa komai. Nace "

kunga ma kud'in da ya bani." Zazzage jakar nayi kud'in suka fado kasa, da sauri aunt ta d'auka tana zare ido, lissafawa ta fara yi  duk dauri d'aya dubu Hamsin ne, dubu dari kenan. Umma tace." Zan ci ubanki Asma'u ki fada min gaskiya ko budurcin ki kika siyar gama naga take-taken ki kwana biyunan ,ni Sam ban yarda da cewa wannan yaron ne ya baki kudi nan ba, na fi tunanin yawon ki ki ka tafi." Kuka na fashe dashi sosai INA rantse wa da girman Allah, aunt Hauwa tace." Gaskiya nima nayi mamaki Asma'u ta yaya har zaku had'u da mutum irin wannan yayi miki siyayya akwai dai abunda kika b'oye." Kallonta nayi ina goge hawaye nace." Aunt kema abunda zaki ce kenan."? Tace" eh mana nasan halin ki fa da shegiyar k'aryar tsiya dama da akwai inda kikayi niyyar zuwa shine yasa kika ki binmu ciki ko." Ina kuka nace" Allah ne shaidata wallahi ni babu wani Dan iskan namiji da na bawa kaina."

Umma ta kalli aunt ranta a bace tace" kira min Aminu a waya yazo ya fi ubanta ko ta fad'i gaskiya. " aunt ta dauko wayarta da sauri ta fara kiran numbar Aminu, da gudu na tashi na shige dakinmu ina kukan takaici.

Minti goma tsakani sai ga Yaya Aminu ya shigo nan suka Zayyane masa komai, a fusace! Ya shigo dakinmu yana fadin"futo ko na ci ubanki." Sanin muguwar zuciyarsa yasa na mike zaune harara ya watsa min yace." Muje tsakar gida ki fada min uban da ya baki dubu Dari." Ina kuka na futo duk suka zuba min ido, bulala katuwa ya dauko a daki ya tsaya a kaina yana huci, gami da fadin"Dan ubanki gidan uwarwa kike je." Shiru nayi ina kuka ya daga bulalar ya zabga min a jikina, ihu na kurma Mimi tayo kaina had'e da rungume ni tana kuka had'e da rokon Ya Aminu.Bulalar ya daga had'e da zabga mana dani da Mimi din muka rungume juna muna kuka yace." Ni ubanku zan ci munafukai kawai bakinku daya Ashe ? Wato talaucin namu har ya kai kuje gurin samari Ku rokesu kudi ko? Ina ce jiya nace zan baku kud'in Atamapar ko zaki fada min ko sai na karya ki."!!!! Ya k'arashe maganar had'e da sake shimfid'a mana bulalar a fatar jikinmu.......Cikin kuka nace." Ya Isa!! Haka nace ya isa haka ka daina dukanmu alhalin bamu aikata abunda ake zargimu dashi, idan ni baku yarda dani ba to ita Mimi meye laifin ta, da zaka dinga dukanta."!!!!! Hannu ya kawo ya buge min bakina yace." Zagina zakiyi ne Dan ubanki. " da k'arfi nace." Ni ba zagin ka zanyi ba gaskiya ce na fada maka, idan baku yarda ba, Ku tashi muje gidansa tunda dai ba b'oyayye bane sai Ku tambayshiiiii.". Yace" ai ko baki fada sai munje dama ai an ce mane min mata ne, koma dai meye zai fada mana, talauci si ba hauka bane"!! Ya karasa maganar had'e da jefar da bulalar yana kuka. Ni da Mimi muka rungume juna muna kuka.

Umma tace" Maza tattare kayan da ta shigo dasu ki mai dasu ledar su had'e da kud'in bayan sallahr magariba sai kuje har inda yake  muji, nifa nafi zarginta ita Asma'un karya kawai take masa domin zuciya tana bani yaron bazai aikata wani aikin assha ba." Cikin zuciyata nace" Umma domin ba ki San waye *Amjadu* bane yanzu da yaya na kwaci kaina daga hannunsa.

Mik'ewa nayi na shige dakinmu Mimi ta biyo ni a baya muka zauna kan katifa muna sauke a

jiyar zuciya Minti biyar a tsakani tace." Asma'u wai da gaske kike guy nan ne yayi miki siyyaya"? Nace" Mimi kin San dai ni kaifi daya ce, wallahi duk abunda na fadawa su Umma hakane, babu karya. Tace" kuma babu abunda yayi miki." ? Kallonta nayi nace." Kema zargin da zakiyi min kenan." Girgiza kai tayi nace" To Allah dai guda ne, in kin yarda dashi wallahi babu abunda ya shiga tsakanina dashi." Shiru mukayi ta mike had'e da fadin Bari in dauko miki abunci naga kamar kina jin yunwa."

Mimi da kin barshi kawai ni bakin ciki ma bazai barni inci abunci ba duk akwai yunwa a tattare dani." Wuce wa tayi ba tare da ce komai ba, minti biyu ta shigo dakin hannunta da plate da shinkafa da wake a ciki gami da salak da tumaturi, duk da abuncin da nake mutukar so ne, amma naji ko sha'awar sa ban yi ba, ta aje min ta futa ta d'ebo mun ruwa ta aje min. Nace"Mimi nagode K'warai Allah ya kara zumunci." Shiru tayi kawai ta tsura min ido tace
" ki sako ki ci." Domin kar in watsa mata kasa a ido yasa na sako na fara cin abuncin ba Dan dad'i ba.
[10/29, 9:51 A ********

Kai tsaye ba su wuce ko ina ba sai gidan granny, tunda al'amarin ya faru bai je ba yau kwana biyu kenan,  mai gadi ya bude get din yana mik'a gaisuwarsa ga Amjadu ya amsa ta hanyar daga masa hannu. Motar ta shige ciki gami da samun gurin tayi parking, Rambow ya futo da sauri ya bude masa motar ya futo da sauri ya karb'i wayoyinsa hannunsa ya shige ciki suka rufa masa baya. Tsayuwa sukayi bakin kofar palo shi kuma ya shiga bakinsa d'auke da sallama, tana zaune kan kujera hannunta rike da carbi kana ganinta kasan tana cikin damuwa dattiijuwa me sanin ya kamata kenan. Tana ganinsa ta sauke ajiyar zuciya had'e da sakin fuska tace." Ashe kana tafe."? Da sauri ya k'arasa kusa da ita yw zauna had'e da Dora kansa kafadar ta, wani irin tausayi tsohuwar yake ji

Kanshi ta shafa muryar ta na rawa tace." K'ato haka Abu ya faru ko." Girgiza kansa yayi dake kafadar ta yace." Waye k'ato kuma."? Kanshi ta rank'wasa tace" ga kanan a gabana." Gyara zama yayi yana Dan bata fuskarsa yace." Bana son sunan fa." Murmushi tayi tace." Yanzu na fara fada ni kuma." Shiru yayi mata. Minti biyu tsakani tace." Amma mutanan sun cika azzalimai, wallahi tunda nake ban taba ganin mutum maciyin amana ba irin Alhaji Hashimu. Nasan da hadin bakinsa komai ya faru."

Girgiza kanshi yayi cike da b'acin rai yace." Granny ni nafi zargin me girma governor domin dashi mukayi sa'insa a ranar." Tace." Koma dai waye ka barshi da Allah da sannu zai saka maka."

Murmushi me ciwo yayi yace." Dole ne Granny Allah ba abun wasa bane amma zan basu mamaki wallahi nafi su k'ananun shekaru nafi su kuma dabaru sosai governor sai ya gagara

futowa wani taro domin sai jama'ar gari sun jefe shi tunda ya nuna kansa a gurin su."

Granny tace." Ai naji a redio sai zaginsa akeyi Allah dai ya kyaua wasu masu mulkin su dauki alk'awari su kasa cikawa su Da Wanda ya hallice su."

Shiru yayi yana girgiza kansa, ta mike a nutse ta nufi kicin da kanta minti biyar tsakani ta dawo hannunta rike da k'aramin tire jere da kayan abunci. Zama tayi tana k'okarin zuba masa, ya bata fuskarsa, tace." Kome zakayi sai kaci abunci ayi mutum yayi ta rayuwa babu cikkaken abunci sai yame-yame." B'ata fuska yayi yace." Si kece komai naki sai kin sanya masa daddawa yayi ta wari."

Hararasa tayi tace" karya kake ba komai nake saka mishi daddawa ba. Kallon plate din yayi yaga wata lafiyayyir wainar shinkafa fara tas da ita, wani kwano me kyau ta bud'e farfesun kayan ciki ne sai kamshi yake yaji kayan kamshi tace." Nasan dai wannan zai yi maka dad'i ko." Murmushi yayi yace." Nagode granny gaskiya kina ji dani sosai, zanci wannan delicious din naki yayi min kyau a ido Allah yasa yayi min dad'i a baki." Duka ta kai masa yasa dariya, hannunsa ya nan nade ya dauki Fork ya fara cin abunci zuciyarsa a sake duk damuwar da yake ciki mutukar yazo gurin kakarshi  yana Neman kashi Hamsin  ya ras.

Yana cin abuncin tana kara tausar zuciyarsa gami da nasiha na cewar kar ya dauki fansa akan duk Wanda yayi masa haka ya barshi kawai da Allah zai saka masa cikin kan kanin lokaci.

Robar ruwa ya d'auka ya bude ya kafa kanshi Yana sha Sam bai tsaya tsiyayawa a cup ba, sai da ya kusa sanye rabinsa ya aje robar ya aje  Fork din had'e da jin gina jikinsa jikin kujera yana lumshe idonsa, shi kadai yasan tunanin da yake. Ta kalle shi had'e da fadin kaga da kana da aure sai kawai ka mik'e matarka tayi maka tausa  yanzu ko sai dai ka zare ido." Bude idonshi yayi yana Dan kallonta tace" K'warai kuwa ai gaskiya na fada" zama gyara yana fuskantar ta sosai yace." Kina son inyi aure ne."? Tace" sosai ma kuwa ai ka kai munzali Dan baka da auran ne ma yasa wasu suke samun dama akan ka, kasan shi aure yana karawa mutum Martaba. "

Yace." Nifa ko budurwa bani da ita Granny." Da sauri tace." Ai me sauk'i ne wannan ni idan ka yarda sai in nemo maka matar aure." Murmushi yayi yana Sosa kanshi yace.' A'ina"?  Gyara zama tayi cike da murna tace. " ko d'azu mun Dade da Innah ka Suwaiba tazo yi maka jaje shine muka yanke shawarar kaje ka nemi auran Hafsa yarinyar da ka gani ranan a gidan nan."

Bude idonsa yayi sosai yana kallonta Yace." Granny nine zanje in nemi ta ko ita ce zata zo."? Tace." Ka tab'a ganin inda mace tazo Neman aure K'ato." ? Sosa kansa yayi yace." Um!Um kawai ki bar wannan maganar Sam! Yarinyar batai min ba, inan zan kawo miki budurwa ta ki

ganta." bata fuska tayi tace"Ai ka saba fad'ar haka, ni dai nace Hafsa nake so ka aura saboda na Yaba da halayen ta."

Kallonta yayi cike da mamaki yace." Granny ni ba tayi min ba in kuma kina so na maida musu da yarinya k'aramar bazawara shikkenan." Jin abunda ya fada ne yasa granny dawo wa nutsuwar ta tace" shikkenan ai yaushe zaka kawo min budurawar taka." Yace." Kar ki damu zan kawo miki ita da ko wane lokaci."

********

Muna idar da sallahr magariba aunty hauwa ta shigo dakin namu tace." Sai Ku futo mu tafi ai naga alama bakin Ku d'aya. " hibaj dina na d'azu na zura fuskata kojale kojale muka futo duk nayi wani zuru-zuru dani. Yaya Aminu na tsaye a bakin kofar futa sai zare ido yake kamar wani dogari , harara ya bimu dashi muka futa simi-simi.... Suka biyo bayanmu bayan sun yiwa Umma sallama.

A dai-dai muka samu muka shiga aunt ta kalli Aminu tare da fadin " yanzu kwatancan gidan zamu nema." Yace." Ai gidansa ba b'oyayye bane a jambolo baza mu sha wahala ba." Su kadai suke hirarsu munyi shiru. Sai da muka zo second get muka sauka muka tsallaka titi da kafa muka fara tafiya, har muka Isa Estate din da muka gani a kulle ga wasu iyayen karnuka a ciki a kwankwance masu tsarin gurin suna zazzaune a gurin zaman su da, ya tsayawa mukayi jikin get din muna shawarwarin yadda za'ayi.

*29/October/2019*
[11/1, 10:55 PM] .: *BABBAN YARO*

*Mallakar_BINTA UMAR*

*LITTAFIN MALLAKI NA NE KUN BIYA KUD'IN KARATU NE KAWAI DUK WACCE TASAN ZATA FUTA DASHI WAJE DON GIRMAN ALLAH TAYI MIN MAGANA NA DAWO MATA DA KUDIN TA.*

*34*

Yaya Aminu ne yake d'agawa masu dadin hannu. Daya daga cikinsu ya taso da sauri yana zare ido! Hannu Ya Aminu ya mik'a masa yak'i karb'a, fuska a had'e yace." Gurin wa kuka zo."? Shi kansa Aminu a lokacin daburce wa yayi kafin yace." Gurin *Amjadu Young millionaire*" wani irin kallo me gadin yayi masa yace." Bayin Allah yanzu duk irin kyauta da bawan Allah nan yake muku bai muka ba sai kun biyo shi har gidansa." Ya Aminu yace." Ba abunda kake tunani bane ya kawo mu, wata Matsalar CE,idan da hali muna so ka sada mu dashi." Cike da nazari me gadin yake binmu da kallo kafin yace." Bai shigo gida ba." Shiru mukayi dukaninmu. Me gadi ya koma gurin zaman sa yana fadawa 'yan uwa tare da nuno mu da hannunsa suna dariya. Duk sai naji na kaskanta Ashe haka Ya Aminu ya juyo gare ni a zafafe kamar zai kurma min mari yace." Kin kyauta Asma'u kinga wulakacin da kika jawo mana ko." ?
Kasa nayi da kaina cike da tsoro domin kar ya dake ni.aunt tace." Yanzu meye abinyi." Ranshi a bace yace." Tafiya zamuyi domin tsayuwarmu a gurin bata da amfani domin bamu San sanda zai dawo ba."

Hon! Mukaji da k'arfi  dukaninmu muka juya da sauri! Gabana ya fad'i ganin motarsa, Aunt tace." Allah yasa shine." A hankali nace "shine ma" duk suka kalle ni cike da mamaki.

Gefe muka matsa me gadi ya bude get din motar ta silala ta shiga ciki, karninkan da suke kwance a gurin suka mike da gudu suka nufi motar, dake akwai haske ko ina a gurin muna kallon abunda yake faruwa daga waje. Ya Aminu ya kaskantar da murya yana rarrashin me gadi kan yaje ya sanar da shi tunda ya dawo.

Yace.' Da kunyi hakuri gobe Ku dawo domin nasan a gajiye ya dawo ko baku San abunda ya faru dashi bane."? Ya Aminu yace." Mun sani shiyasa ma muka zo muyi masa jaje." Me gadi ya kalli Aminu cike da mamaki minti biyu yace." Bari in fada masa." Ya Aminu yayi masa godiya ya wuce ya barmu tsaye bakin get muna hangosa ya isa gurin shi yana daf da shiga part din shi.

Tsayuwa naga yayi yana kallomu, minti biyu ya nufo inda mike wannan dog din nasa da nagani farkon fara gani na dashi ya biyo bayansa, tare dasu rambow. Tun kafin ya k'araso na sunkuyar da kaina kasa.

Shi ko *Amjadu* tun kafin ya isa gurinsu ya gane ta, ko cikin mata dubu yarinyar zata shiga yana iya gane ta, ballanta guri da haske futulo dal-dal tamkar rana, mamaki yake me ya kawo ta gidan shi, kuma? Ya karasa fuskarsa babu yabo babu fallasa. Da sauri Ya Aminu ya mik'a masa hannu alamun su gaisa, ba tare da girman kai ba ya mik'a masa NASA sukayi musabaha, kamar bai sanmu ba nida Mimi haka ya nuna ya kalli aunt da Aminu a nutse yace." Ina fatan lafiya ko." Ya Aminu ya diririrce domin guy yayi masa mugun kwarjini ashe jinsa kawai yake a baki wannan shine jinka yafi ganin ka, duk taurin kai gami da dakiya irin na Aminu sai da ya risina. Ya sunkuyar da kai tare da fadin" Yallab'ai magana ce take tafe damu ina fatan babu damuwa." Ni ya kalla ina kallonsa a fakaice ya d'auke idonsa daga kaina yace." Babu matsala amma ku shigo ciki ko." Aminu yace." Godiya muke." Wuce wa yayi ciki muka bi bayansa tuni dog d'insa ya fara wani irin ihu! Yana tsalle zai cafke ni! Da gudu na matsa ina zare ido!! Wan!wan!wan!wan! Dog din kawai yake yayo kaina tare da kama bakin hijabina da yake Jan k'asa!! Ihu!! Na kurma ina k'ank'ame jikina guri guda." Cikin tsawa naji yace." Tegar"!! Stop."! Daina haushin yayi ya tsaya yana kallona. A hankali ya ja siririn tsaki ya kalli Ya Aminu tare da fad'in "wannan black din abun da ya gani a jikinta ne yasa yake tunanin ko Anjalina ce." Wato matar shi, cikin dizgi! Ya Aminu yace." Dama ya cije ta ai da mun huta da halin taurin kai. Ita b'aka ta kama ta sanya b'akin abu ba dole karnuka su biki ba." Babu abunda yace yayi gaba muka bishi a baya gabana sai bugawa yake yi na tsinewa dog din nan yafi sauri dari, shima Ya Aminu yanzu wani mugun haushin sa nake ji

Rambow ya bude masa kofa ya shiga muma muka shiga, ina kallon aunt Hauwa sai kalle-kalle take a parlor ni da Mimi dama gidan ba bakonmu bane, shi kanshi Ya Aminu zare ido kawai yake yi sai kallon parlor yake yi
Bedroom dinsa naga ya nufa, na kauda kaina zuciyata na tuna min abunda ya faru dani da shi kwana biyu da suka wuce.

Muna zaune kimanin mintuna ashirin babu Wanda yacewa da Dan uwansa uffan! Dukaninnu jiran futawar sa muke. K'amshin tura ransa ne ya tabbatar mana da ya iso, tunda na daga kaina sau daya ban sake kallonsa ba, saboda nasan na tsananta to Zan iya tonawa kaina asiri.. Yana sanye da wasu had'addun kayan shan iska black and White rigar sharara k'irjinsa a bude shi kuma wandon iya kacin sa gwiwa da alama Wanka yayi ganin yanda fuskarsa take shek'i gashin girar shi da danshin ruwa, zama yayi kan kujerar dake fuskanta ta, ya kalli Aminu a nutse yace. " na barku ko kuyi hakuri nayi Wanka ne." Ya Aminu yace." Babu komai yallaby." Yace." Ok ina jinka." Cikin daburcewa Ya Aminu ya fara magana kamar haka.

"Yallab'ai waccan yarinyar dake zaune kujerarar dake kallon ka, k'anwar mu, ce d'azu misalin k'arfe hudu bayan an idar da sallahr la'asar kenan ta shigo mana gida da kudi da kaya wai Kaine ka bata, shine hankalin mahaifiyar mu ya tashi tace bata yarda da ita ba, Dole tace azo a tambaye ka."

Sunkuyar da kaina nayi zuciyata kamar tayi bundiga wai ni ake wa wannan tozarcin humm! Lallai ya Aminu.

Ta kasan idona nake kallonshi yana Dan satar kallona, ya kalli Aminu tare da fadin" Abunda nake so na fahimta anan shine dama can yarinyar tana bin maza ne ? Ko ko kuna zargina da ita ne."? Yadda ya fad'i maganar zaka san ranshi a bace yake. Ya Aminu yayi saurin cewa"Ko daya Yallab'ai ita yarinyar muke zargi ba kai ba.". Shiru parlor yayi mintuna biyar sannan yace." Duk abunda tazo ta fada muku a gida hakane nine na siya mata kaya kuma nine na bata KUDI don ra'ayina ba don wani abu ba, saboda haka Ku daina tuhumar ta, a kan aikata alfasha, naji dad'i da samun ku iyayen jajurtattu gaskiya na yaba k'okarin Ku." Ya Aminu yayi murmushi had'e da godiya, aunty Hauwa ma sai washe baki take..Mik'ewa yayi yace." Ni zan shiga ciki Ku sauka lafiya kai idan kun futa doh-doh na tsaye a waje kace injini ya kai Ku har gida." Ya Aminu yace" godiya mukeyi" hannu kurum ya daga masa ya shige bedroom dinsa.

Jiki a sanyaye na mik'e tsaye sosai nake mamakin halin ko in kula da guy nan yake nuna mini in ya ganni cikin mutane sai ya nuna sam bai sanni ba, yanzu ma dubi yanda yake wani shan kamshi ba, tab'e bakina nayi na futa daga parlor cike da taikacin wulakamcin da yayi mana, gaba nayi kawai ina jin ya Aminu ya tsaya yana fadawa  doh-doh sak'on da oganshi yace..

Aunt hauwa ta kwala mib kira nayi nisa ma ina daf da fita tace." Kizo mu shiga mota mana ko baki ji abunda aka ce ba." Ba tare da nace komai ba na dawo da baya, sai da suka gama shiga tsaf! Sannan na shiga doh-doh ya ja motar muka futa daga gidan.

*****

Tsaf Ya Aminu ya zayyanawa Umma komai tayi hamdala gami da godewa Allah, ta kalle ni tare da fadin"Allah ya cece ki wallahi." Ni dai shiru kawai nayi ina mamakin halin Ya Aminu, aunty hauwa tace." Mara mutunci gurin siyar kayan ko ki tuna dani ko Isilam baki tuna ba balle ki siya mata ko pant ne." Shan kunu nayi domi itama aunt hausshin ta nake ji.Mik'ewa nayi ba Tare da nace mata komai ba. Hararata tayi tace." Sai kije kiyi tayi ai gaskiya ce dole a fada miki..

Dakinmu na shiga na kwanta kan katifa gami da rintse idona suffar sa kawai nake tunawa lokacin da ya futo daga bed d'insa, a d'azu tsigar jina ta tashi da idona ya hasko min k'irjinsa  na cije leb'ena gabana na fad'uwa da na tuno abunda yace da Ya Aminu wai yayi min siyayya ne ba don wani dalili ba kawai ra'ayin sa ne. Wannan kalma da ya fada sam ba tayi min dad'i ba.. Mimi ta shigo dakin tana buge gurin kwanciya tare da fadin "bakiyi sallah ba kinzo kin kwanta." Mik'ewa zaune nayi nace." Mimi Wanka ma nake so nayi hummm! Ai ni yau 'yan gidan nan sun bani mamaki ."  Mimi tace." Wane mamaki kuma"? Cike da takaici nace" baki ga irin zargin da suke min ba Mimi."?

Murmushi tayi kawai ta cigaba da gyara shimfid'a na mike zuciyata babu dad'i na futa, ina kallon aunt Hauwa zata tafi suna sallama da Umma Ya Aminu na tsaye yana jiranta DOMIN ya raka ta hanya saboda dare ya fara yi, ko kallonsu banyi ba na dauki bokiti na cika da ruwa na shiga band'aki abuna.

Wanka nayi na futo na tsuguna bakin rijiyar na d'aura alwala, lokacin da na shiga dakinmu Mimi ta kwanta tana lumshe idonta dama ita sarkin bacci, duguwar Riga na zura na sanya sabon hijabina na tada sallah duk sai da na rama sallolina nayi addu'a sannan na mike had'e da ninke daddumar na aje ta, ba tare da na cire hijab dina ba na nufi kicin Fula's din da ake zuba mana abunci na dauko  na dauko dugon jug na Debi ruwa  a randa na wuce dakinmu ba tare da na kalli kofar dakin Ummamu ba.

A hankali nake cin abunci kamar me cin magani ko rabi ban ci ba na rufe Fula's din, ruwa na d'auka nasha. Jin gina kaina nayi jikin katifa INA addu'a Allah yasa nannauyan bacci ya d'auke ni domin bana so tunanin guy nan ya dame ni.. Haka kurum daga na tuna shi a ko wane hali sai gabana ya yanke ya fad'i!

Allah ya amshi addu'a ta bacci naji a idona nayi saurin hayewa katifar had'e da runtse idona kafin minti biyar bacci ya kwashe ni, me nauyin gaske!

*****

Shi kuwa Amjadu bayan tafiyar su, mamaki yake sosai yanda iyayen ta suke da kula da tsantse ni gaskiya sun burge shi sosai kuma yarinyar ta kara samun girma a cikin zuciyar sa,, kashe wayonyinsa yayi duka ya kwanta shima domin wani irin bacci yake, abunda da Wanda ya kwana ya yini a tsaye.

*Asubah ta gari Young millionaire*

******

Me girma governor hankalinsa ya kai kololuwa tashi sosai yanda jama'ar gari suke zaginsa kuma suna zargin sa, dole ne ya zauna da manya 'yan kasuwa kamar su Mai citta, hankalinsa bai kara tashi ba sai da ya saurin Maganar *Amjadu* ta yau inda 'yan jarida suke masa tambayar shin yana sha'awar shiyasa, hankalinsa ya tashi sosai da yaga jama'ar gari suna ihu tare da fadin"Muna sonka zamu Mara ka baya duk inda kake." : Lokaci kankani yaji wata irin

muguwar tsanar yaro ta kara shiga zuciyarsa yana ganin da alama yaron yana da farin jinin jama'a, kuma alumma zasu yi sauya masa ra'ayin sa ya fara sha'awar siyasa Wanda yake ganin haka kamar karshen mulkinsa ne yazo gashi yana so yayi tazarce, dole nema ya sake tsaurara matai kuma zai k'irk'iri abubuwa Wanda zasu jawo hankalin allumma su dawo kansa. Da wannan shawarar ya kira Alhaji Hashimu ya fada masa cewar gobe k'arfe goma na safe ya zo gidan gwamnati zasu tattauna magana me muhimamci.

******

Ko da na tashi da safe babu Wanda na kula ita kanta Umma gaisuwa ce kawai ta shiga tsakanina da ita, na koma dakinmu na kwanta zuciyata duk babu dad'i. Mimi ta shigo dakin hannunta d'auke da jug cike da koko d'ayan hannun kuma takardar k'osai CE,ta aje tare da fadin " ki tashi mu karya duk wannan nukufurcin babu inda zai kai ki." Ganin yanda ta damu dani ne yasa na mike zaune muka fara karya wa.

Bayan mun gama tace." Ya Aminu yace." Mu dauki kud'in atampar a cikin kud'in jiya." Nace" kudina ne babu Wanda ya Isa ya tab'a min bayan sun gama ce min 'yar iska kuma zasu ci kud'in iskan ci kenan." Na karasa maganar raina w bace.!! Mimi tace" duk abunki dai ba a canzawa towo suna dole kiyi hakuri dasu,kuma ni banga laifin su." Nace" ai baza ki gani ba Mimi tunda ba ke aka yi wa ba." Mimi dai shiru tayi min ganin yanda na hayayyak'o mata da masifa.

Muryar Umma naji tana kwala min kira, amsa wa nayi na mike da sauri. Daga bakin kofa na tsaya nace" Umma gani" Sam naki kallon Ya Aminu dake tsaye  yayi shirin makaranta.

Tace." Idan anjima aunt Ku zata zo sai kuje Ku siyo shaddar da atamfar ga dubu ashirin a cikin kud'in dole a fada miki tunda hakkin ki ne."
"To" kawai nace na kama hanya zan koma daki. Ya Aminu yace." Dawo Dan ubanki ba,a gama magana ba zaki tafi." Rai abace nace" nifa na tsani wannan abunda kake min haka kawai sai ka dinga yi min tsawa kana hantara haka jiya a gaban mutane ka tsinkani ni gaskiya ka daina min irin haka bana so."Hannu ya kawo zai dake ni na kauce da sauri ina zumb'ura baki! Yace." Idan na kara me zaki min? kaji min Mara kunyar yarinya ko." Umma tace"kai tsiyata da kai saurin duka ka daina don Allah." Yace" Umma wannan yarinyar ai duka ne maganin ta." Nace"wallahi Umma baga yanda jiya ya dinga min masifa ba a gaban mutumin nan. " Umma tace." To ke meye damuwar ki.? Shiru nayi kawai. Ya Aminu ya wuce Yana mata sallama ita kuma sai fatan alkairi take masa, kallona tayi tace" kuyi sauri Ku gama aikin Ku kafin tazo domin kun santa da azazzala." Nace" toum Umma" Mimi na kwalawa kira ta futo muka fara aikin gida.

********

Yana zaune a gefen bed jikinsa daure da wani faffad'an towol da alama daga Wanka ya futo Loptop dinsa ce a cinyar sa, suna magana da babban abokin shi  Anthony dake can Chana.

Dama duk yana da labarin abunda ya faru da abokin nasa shine suke shawarwarin abunda za'ayi.Anthony yace." Company uku ya kamata a bude Wanda zai dinga kawo ko wane irin kaya daga na hausawa har na turawa, daya a Chana d'aya a America d'aya a nan kano din, saboda haka k'wararraun ma'akata zai zo dasu cikin wannan satin a fara aikin gurin." *Amjad* yaji dadin wannan shawara da abokisa ya bashi gashi dai arne ne amma yafi wani musulimin kishin musulunci, nan ya amunce da shawarar abokin nasa.sun tsaida rana Monday Anthony zai shigo najeria tare da ma'aikata domin a fara gudanan da aikin sabon company me zaman kansa.

******

Me girma governor ya kalli Mai citta murya a cunkushe yace." Ina fatan jiya ka saurarin maganar wannan yaron ko."? Mai citta yayi kamar bai fahimci wa yake nufi ba.
Yace." Ranka shi Dade wane yaro ne."? Me girma governor ya daki! Tebur din da yake gabansa ransa a bace yace." *Young millionaire* ne zaka ce baka fahimta ba, ko wace kafar sadarwa tana watsa muryarsa jama'ar gari suna ihu! A kansa tare da bashi goyon baya ko ta Ina, wannan nasarar da ya samu ina me tattabar maka da cewa, ni asara ce a gare ni, domin mutukar mutanan gari sukayi mubayi'a dashi to babu shakka kashina ya bushe 4+4 din da nake so nayi bazan samu ba."
[10/30, 10:50 AM] Binta U Abbale👄: Mai citta  hau inda-inda! Cike da takaici da jin haushi governor ya kunna wayarshi had'e da bude rocouding na muryar Amjadu ya mika masa.

Shima sai da jikinsa yayi sanyi, jin hayaniyar jama'ar gari da ihu duk a kam Amjad. Gyad'a kai yayi yace." Yanzu meye abinyi."? Governor yace." Dole ne ku ne mi maslaha dashi, ko kuma Ku zauna kuyi shawarwari a tsakanin ku, Ku manyan yan kasuwa abunda zai fishhe Ku,  saboda duk abunda nasa  aka yi wannan yaron DOMIN in faranta muku ne, nima sai kuyi kokari kuga na zauna kan kujerarar mulki shekara takwas." Share gumi! Me citta yayi cikin zuciyarsa yake cewa" lallai ubangiji me kyauta a kan bawan sa wani lokacin akan yi wa mutum mugun Abu sai ya zama alkairi a gareshi, mutukar ubangiji ya so bawa da rahamarsa ta babu shakka babu wani d'an Adam d'in da ya isa ya hana faruwar haka.... Yace." Ranka ya dad'e ina ganin zamu fara bin malamai da 'yan tsubbu kan yaron nan domin naga kansa da tauri! Ina ganin idan aka nakasa masa wani b'angare na jikinsa tou sai ya nemi guri ya zauna, kaga kenan babu shi babu wani mulki."

Governor yace." Ni dai babu ruwana duk abunda zakuyi kuje kuyi kujera ta kawai na sani idan ba haka ba, kafin na sauka daga kan mulki wallahi duk sai na ruguza Ku." Mai citta yace." Duk baza'ayi haka ba ranka ya Dade zamu San abun yi, insha Allahu.".
Sallama sukayi ko wanne ransa babu dad'i.

********

Yau bai yi niyyar futa don haka da towol din a jikinsa ya kwanta kan bed ringingine yana lumshe idonsa, jiya yaso ya tsosi yarinyar nan, bai samu dama ba, abun ya tsaya masa a rai duk da halin damuwar da yake ciki hakan bai hana shi sakin murmushi lokaci zuwa lokaci ba, Zumbur! Ya mike jikin wardrobe dinsa ya nufa ya bude ya fara lalube can ya Ciro pant din ta, ya rike a hannu yana sakin wani miskilin murmushi. Bed din ya nufa hannunsa rike da pant din ya zauna had'e da tsira masa ido kawai yana kallonsa....yanayin jikinsa ya fara sauyawa tsigar jikinsa ta mike tunda yake mu'amula da mata iri-iri bai tab'a samun yarinyar da ta shiga zuciyarsa ba irin ta ya rasa meye dalili?? Kawai dai ya San yana mutukar son bakinta mussaman in tana tsiwa yanda take da zafi-zafi haka bakinta yake da tes miyau ta yayi masa sosai uwa uba albarka tun k'irjinta masu taushi gami da girma Wanda yake kasa ritsa su da hannunsa,, yarinyar tayi ta ko wace siga, d'an ya tsansa ya dago yana kalla, murmushi yayi had'e da Dan Sosa kanshi a fili yace." *Asma'u!!!!* zan San yanda nayi kika dawo gidanan domin kin d'an d'ana min zumar ki, mai wahalar mantawa.... Wayarsa ce tayi k'ara alamun ana kira. Yana dubawa yaga sabuwar numbar, Kamar kar ya d'auka sai kuma ya mik'a hannunsa ya dauki wayar tana daf da k'arshe yace." Salam"" Hibbah ta saki ajiyar zuciya jin muryar gwarzon zuciyar ta. Tace." My Apple gani nazo gidan ka masu gadi sun hana ni shigowa wai sai na nuna shaida." Mik'ewa zaune yayi sosai jin muryar kamar ya San me ita, kai tsaye yace." Wacece ke."? Wata irin shashshekar kuka tayi tace." Ka manta da kankanaty ka ko.? Nice Hibbah!!!" Take ya tuno yarinyar 'yar gidan me citta CE." Cikin basarwa yace." Oh! Hibbah ya kike? Ya gida."? " lafiya Lou Nazo yi maka jaje banzayen masu gadi sun hani shigowa kamar basu San wacece ni ba a gurin ka." Murmushi yayi yace." Akan aikin su suke so ina ganin basu da wani laifi anan... Nagode da kulawa, kije kawai ba sai kin shigo ba." Hibbah taji kamar ta kurma ihu!! Guy nan yana abunda yake so fahh!! Ta fada cikin zuciyarta a fili kuwa cewa tayi." Amm!!! Ai ina so in gan ka ne, kasan nayi missing din numbar wayar ka ranar na manta ban k'arba." Shiru yayi na minti biyu Daga bisani yace." Ok kashe wayar zanyi magana da rambow yanzu." Cike da farin ciki ta kashe wayar tana watsa wa masu gadi harara.
Wayar rambow ya kira yace yaje ya shigo da ita.

*Pls kuyi hakuri don Allah wallahi in da wadataccan chaji ni me faranta muku ce, Ku dai cigaba da bina yanzu aka fara kafcan*

*30/October/2019*
[11/1, 10:55 PM] .: *BABBAN YARO*

*mallakar_BINTA UMAR*

*LITTAFIN MALLAKI NA NE KUN BIYA KUD'IN KARATU NE KAWAI DUK WACCE TASAN ZATA FUTA DASHI WAJE DON GIRMAN ALLAH TAYI MIN MAGANA NA DAWO MATA DA KUDIN TA*

*35*

Mik'ewa yayi ya nufi wardrobe ya ciro wata shart fara k'al, ya sanya a jikinsa had'e da short nickar blue coular mai aljihuna gaba da baya had'e da wasu sark'ok'i a jikinsa, sosai yayi kyau lafiyayyar fatar sa tayi luki sai shek'i take yi, a haka ya futo palo ya zauna yana jiran shigowar Hibbah, ta shigo cikin takun k'asaita, suna hada ido dashi tane mi kuzarin ta ta rasa, tarasa wane irin kwarjini ne da guy nan Wanda daga zarar ka hada ido dashi shikkenan sai ka rasa nutsuwa. Kallo ya bita dashi har ta k'araso kusa dashi ta zauna jikinsa sosai tana masa wani Dan iskan kallo cike da tsantsar sha'awar sa."
Hannu ta kai zata shafa sajan fuskar shi. Ya rike hannun yana d'an hararata tare da fad'in" Ina fatan lafiya ko." ? Lumshe idonta tayi ta bude had'e da tsare shi dasu tace." My love lafiyar ce ta kawo haka, na kasa daurewa ne wallahi kayi min mugun kyau *Amjadu* ina mutukar kaunar ka a raina." Kallon baki da hankali yayi mata, yace." Dama abunda ya kawo ki kenan." ? Girgiza kanta tayi had'e da lumshe idonta ta d'an ciji lips dinta tace." No Nazo nayi maka jaje sannan na kalli wannan kyakkyawan fuskarta taka da nayi missing." Murmushi yayi had'e da cewa" bani ya kamata kiyi wa jaje ba 'yanta." Gyara zama tayi tana wani marmar  da ido cikin sigar Jan hankali tace." Ban fahimce ka ba." Sajanshi ya shafa as'usuel yace." Ina nufin ki fara yin jaje a gidan ku tun kafin ki iso nan, ko kina nufin zaki ce min bakin San har da sannun mahaifin ki akan abunda ya faru dani ba ne."? Cikin alhini da damuwa ta kalle shi tace" ka yarda dani my love wallahi ban san kan al'amarin ba, nasan dai tunda muka taso muke ji sunan mahaifin ka a bakin mahaifin mu,  yace suna da kyakyawar alaka dashi kafin ya mutu, kaine da bakwa shiri da juna." Gyada kansa yayi har yanzu hannunshi na kan gemun shi yana shafawa yace." Hakane ni da mahaifin ki kamar kura da nama ne,ba ma ga muciji da juna, kije ki tambaye shi dalili zai fada miki." Kamar zata yi kuka tace" ni kam babu ruwana da alak'ar ka dashi me kyau ko mara kyau soyayyata kawai na sani a cikin zuciyarka." Kai tsaye! Yace." Baza ki samu ba." Wani irin abu taji cikin zuciyarta ta kalle shi bakinta na rawa tace." Meya sa."? Kallonta yayi fuskarsa a had'e

yace." Ke baki Isa na fada miki dalili ba.". Kuka ta fashe dashi sosai had'e da girgiza masa kanta tana fad'in"kar muyi haka da kai my love wallahi ina ji wata muguwar soyayyar ka cikin raina ina ganin zan iya rasa rayuwa ta a kanka, na San waye kai so bazan tab'a yin sakaci gurin ganin ka sub'uce min ba."

Kuka take har da shashsheka! Yana kallonta hankalinsa a kwance, mamaki. Yake mace har mace ta dinga kuka Hibbah dai ta cika mace ta ko wane fanni tana damar auran duk Wanda take ra'ayi amma abun mamaki tana kuka har da sharb'e duk a kansa shi kam abun mamaki yake bashi. Mik'ewa yayi ya bar mata kujerar a nutse ya Isa gurin frige ya d'auko gwangwani Lemon cocar cola guda yayi sanyi sosai! Romot ya d'auka ya canza tasha sannan ya zauna kujera dake daf da kofar futa ya bude lemon shi yana shan abunshi hankalinsa na kan tv.

Hibbah taji kamar taje ta rungume shi haka take ji, wato yayi banza ma da ita lallai guy nan yana ji da wulakaci, fuskarta ta goge ta mik'e ranta babu dad'i ta Isa kusa dashi
Hannunta ta d'ora a kafadarshi tana d'an matsawa kad'an, ya dago kanshi Yana kallon fuskarta, kyau iya kyau gashinan amma bashi ne a gaban shi ba,zuciyarsa nacan tana tunanin wani Abu,
A hankali tace" ni zan tafi tunda ka wulakanta ni, Ashe dama laifin uba yakan shafi d'iyar sa, wato don na zubar da daraja ta a gurin ka yasa kake min kallon ban Isa b.......hannu ya daga mata fuskarsa a turb'une yace." Ke kike maganar Isa a gurin nan, tun farkon fara haduwa take na fada miki cewar ni bana maimaita Abu guda ko suttura ce in na gada yau idan na sanya ta zai iya bada ita, tsarina ne haka." Ya cigaba da kallonsa hankali kwance. Cike da tsantsar b'acin rai! Hibbah ta futa daga parlor kamar zata kifa, tsaki ya ja kawai yana tab'e baki.

********

Sai da muka kammala komai sannan muka dawo gida, hatta da kud'in dinki sai da muka biya, Munnu ta dinga murna tana fadin ta samu kudi, domin ba zata mayarwa da Kawu kudinsa ba,a cewarta ta siyi wani abun ita...aunt Hauwa sai wani ji dani take ni kuwa ina shareta DOMIN har yanzu ban gama sakko wa ba, muna koma wa gida Umma ta gama abunci don haka na zage naci sosai dama akwai yunwa sosai a jikina

Bayan mun gama cin abunci ne a na zaune ana hira nace"Umma ki bani dubu goma sha biyu a cikin kud'in I'n siyi waya."

Tace" INA taki take."? Nace" Umma wayar nan dama lallab'a ta nake wallahi jiya ma ta fad'i gurin chaji ya lalace." Tace" kuma sai a kace Dole sai mai tsada zaki siya ko ina zaki kai wayar dubu goma."? Marairaice fuska nayi nace" Lallai Umma Don baki ga wayoyin 'yan ajinmu bane rafka rafka ko Mimi."? Nafada INA kallon Ta. Tace" hakane Umma dom Allah ki bata kin ga sai muje da karfinmu babu raini." Hararata Umma tayi tace." Saboda rashin kishin kai ke Kin yarda ita ta rike waya ke baki da ita." Dariya Mimi tayi tace."Ummanmu kenan a wayar ta kamar tawa

CE." Tace" duk da haka dai baza ta siya ita kadai ba ga dubu goma sha hudu kuje Ku siyi 'yar dubu bakwai bakwai ta ishe ku."

Bata fuska nayi nace"Umma wayar dubu bakwai ai me madannai ce ni da nake son toching." Aunt dake k'okarin shigowa dakin bayan futowar ta DAGA band'aki tace" sai ki siyi Vivo kawai in dole ne sai Kin rike babbar waya wannan ragowar kud'in da kika sakawa ido zamuyi amfani dasu ne gurin kara jari ki cire idonki daga Kansu, " ta karasa maganar ta tana shirin ta da sallah. Nace"aunty ko Vivo zamu siya tafi dubu bakwai indai sabuwa CE." Umma tace" sai Ku siyi ta hannu ai duk waya CE." Shiru nayi kurrum domin bana kaunar yin jayayya da Umma.

Sai daf da marigaba aunt Hauwa tabar gidan.Mimi ce kawai ta karata hanya ni ko kwanciya ta nayi ina jin haushin yanda take k'ara zuga Umma akan komai,wani lokacin ko Umma bata yi niyyar yin abuna to aunt Hauwa da Ya Aminu sai su sanya ta.

******

Yaya Aminu ne ya shiga kasuwar 'yan jagwal ya siyo mana Vivo ko wacce da ta ta, dake namiji ne sai suka bashi me kyau DUK bata wani sha jiki ba, yau saura kwana biyu Party mu duk mun tashi hankalin mu ni da Mimi mun fara gyaran jiki kamar wasu amare dilka da halawa kullum sai munyi aikuwa fatarmu ta goge mussaman ni da nake da chocolate din fata sai take wani irin k'yalli abun gwani sha'awa

Munnu muke jira tazo domin yau ne mukayi niyyar zuwa kunshi ja da baki can kabuga zamu je wata 'yar kawar Ummansu Munnu ce take yi, duk mun shirya Munnu kawai muke jira tazo

Goma da minti goma ta shigo ko zama ban Bari tayi ba na azazzale ta, a tsaitsaye suka gaisa da Umma muka kama hanya.a dai- adai ta sahu guda muka d'auka har kabuga muka sauka da kafa muka shiga lokon su Bahijja me kunshi.

Babu jama'a a gidan Dan dama mun sanar mata da cewar in mun zo baza mu bi layi ba, aikuwa dama lallanta a had'e yake kawai ta fara aikinta. Ja ta farayi mana, bayan shi dai d'aura mana baki a kai, wai!!! Kafin kace kwabo mun fito Tass!damu gaskiya Bahijja ba dai Iya kunshi ba, dunu uku na mik'a mata tace baza ta karb'a. Ummansu tace" akan Me zata karb'a kuje fa kud'in ku ai Ku na gidane." Aikuwa zura kud'in nayi a jakata dama a titi da muna tafiya naga wani gurin kwalliya gami da gyara gira. Muna futa nace dasu Mimi mu tsalla titi muje shagon kwalliyar can." Munnu tace"wane irin kwalliya kuma. ? Nace "ke dai muje." Suka biyo ni a baya cike da mamaki.
Duk kab'ilu ne a gurin, suna ta aikinsu ga wasu had'addun 'yan mata anayi musu kitso irin na gashin doki.. Sai hira suke gami da taunar cingam. Cikin turanci nace da wata in ya mura muna

so a gyara mana gira ne kuma za mu siyi gashin ido muna son su nuna Mana yanda zamuyi amfani dashi.

Aikuwa sunga costomas tuni suka bamu gurin zama muka zauna. Mimi ake wa ina kallonta naga tayi kyau sosai, murmushi nayi nace"Mimi kin ganki kuwa."? Fuskarta ta shafa a hankali tayi dariya. 'Yan Matan nan ne naji sun kwashe da dariya nayi saurin kallonsu cike da zargi, kawai idona yayi min tozali da budurwar nan da mukayi fada da ita shekaran jiya a Mudannsir&brots, shan kunu nayi sosai tare da tsare gira

Naji tana fad'awa kawarta duk abunda ya faru.kawar tata tace." Kawai ki karawo su Salmanu a waya suzo su sab'a mata kammani." Na fuskanci ni suke nufi. Mimi da Munnu Sam basu gane komai na sun fi tunanin cewar 'yan Matan hirarasu kawai sukeyi irin ta kawaye.

Bayan an gama wa Mimi sai Munnu nice ta k'arshe sosai nace su gyara min saboda ina da yawan gashin gira sosai...aikuwa suka shiga fed'e min had'e da red'e ta sai da ta dawo siririya sosai tayi wani irin kwana sannan suka bar ta, mudubi na kalla naga nayi kyau sosai, handbag dita na bude zan Ciro kudi kawai naji an wafce da sauri na d'ago kaina ina kallon su, wasu matasan samari ne sun sha askin 'yan iska leb'ansu bakikkirin dashi. Wannan vudurwar suka kalla tare da fadin "ita ce ko."? Gyda kanta tayi Tare da mik'ewa da niyar tafiya dama an gama musu kitson su....d'aya daga cikin masu aiki a shagon ta k'araso da sauri cikin turanci tace" me yake faruwa ne.? Safiyya ta mik'a mata kud'in aikin su ba tare da tace da ita komai ba taja hannun kawarta suka futa daga gurin
 Kaina suka yo suna jamin mayafi cikin sigar rashin mutumci! Da sauri na Mik'e tsaye ina gudun kar su cire min mayafi gani a kan hanya kuma a bakin titi domin daga inda muke muna ganin shige da fuce na jama'a gami da zurga zurgar ababen hawa.Mimi da Munnu suka mike hankali a tashe suna basu hakuri . ni ko cewa nake." Ku rabu dasu suyi min abunda aka sanya su Mimi sai ta fara kuka ganin har sun cire min mayafi. Duk ma'aikatan gurin suka rufe mu suna basu hakuri d'aya daga cikinsu ce ta dauki wayarta domin ta kira aunty su wato wacce ta bude gurin, ita kuma d'aya ta futa waje da sauri domin kiran jami'an tsaro.saboda wani lokacin suna zama bakin hanya kasancewar titin kabuga babban Titi ne bayan haka akwai many an masu kudi sosai a nahiyar saboda haka dole sai Da tsaro. Mimi ma futa tayi da gudu ta tsaya bakin titi ta diririce sai zare ido take......Fuuuuuuuuuu!!! Motar tazo ta wuce, yana kwance ciki ya hango Mimi da sauri ya mik'e zaune gami da bawa dravar sa umarni ya koma baya....doh-doh ya bi umarnin da aka bashi. Dai-dai santar shagon motar ta tsaya, ya hango duk abunda yake faruwa a ciki. Asma'u ce tsaye babu mayafi babu d'ankwali ga wasu maza tsaye a kanta. Sai mata uku suna kare ta.. Dake motar me tintac ce babu Wanda ya ganshi a ciki cikin tsantsar b'acin rai gami da bak'in ciki da takaici ya kwatsawa rambow tsawa tare da fadin yayi maza ya bud'e motar nan yaje ya kawo masa 'yan iskan samarin nan, har da ita kan ta Asma'u.

Rambow ya bude motar da sauri ya nufi shagon, tunda nesa ta hango rambow sai gabanta ya fad'i tana mamakin me ya kawo shi gurin? Fad'uwar gabanta ne ya tsananta da ta tuna nan

hanyar gidan shi ce tsakanin kabuga da jambolo ko da kafa mutum ya karasa, taji dadin zuwan rambow tasan zai taimake ta daga hannun 'yan iskan samarin nan. Wanda suke k'okarin yi mata tsirara, daya daga cikin ma'aikatan gurin ce ta rike rambow tana fadin" please oga zo ka taimake mu ka futar Mana da wad'ancan 'yan iskan samarn." Rambo ya shiga ciki sosai take 'yan iskan suka shiga hankalin su, domin sun yi wa rbow kyakyawan sani, yace." Me ya hada Ku da ita."? D'aya daga cikinsu yace." Oga sunyi sa'insa da wata ne kwanaki shine ta kira mu muzo muyi mata tsirara." Shi kanshi rambow da yaji abunda suka ce sai da ya tsorata, mayafin ya d'auka ya mik'a mata da sauri yana waiwayen bayansa, yace." Ku muje mota dama akwai aikin da zakuyi mana a company ." aikuwa suka wuce da sauri suka tsaya jikin motar su duk a tunansu babu kowa ciki rambow ne kurrum, To shima *Amjad* din yana sane yaki futowa saboda gudun idanun jama'a DUK da haka yana kallon yanda mutane suke zurga-zurga a gurin motar tunda duk inda motocinsa suka shiga dole a gane saboda sunanshi dake mak'ale a bayan motar wato *AA AbulAbbas Mai nasara*.shiyasa yak'i futowa amma dukanin abunda yake faruwa yana hangowa, rambow ya kalli Asma'u yace." Ku muje in kai Ku gida, don Allah Ku daina kula irin wannan 'yan iskan samari marasa kamun kai."
Fushina na sauke a kansa na watsa masa harara tare da fadin" kaga munyi kama da 'yan iskane da zaka fad'i wannan maganar, mtssss." Su Mimi da ma'aikatan gurin suka Bini da kallo cike da mamaki! D'ankwalina na d'aura sosai na ya fa mayafina kudinsu na mik'a musu,nace" Ku mu tafi." Su ka biyo ni abaya , Rbow ko dake yasan halin rashin kunyar yarinyar bai damu ba, kuma yaga ogonshi yana ji da ita, shiyasa yake kaffa-kaffa.

Tsayuwa mukayi bakin titi rayukanmu babu dad'i mussaman ni tunani kawai nake hanyar da zanbi in rama rashin mutumcin da wannan 'yar iskar tasa akai min a bakin titi don ma mutane nasu ankara ba, da kunyar da zanji sai Allah.
Tunda ta futo daga gurin yake kallon har suka zo suka tsaya bakin titi bai d'auke idonsa daga kanta ranshi in yayi dubu ya b'aci! Ya kalli 'yan iskan samari yana nazarin su. Meye alakatar dasu ? Da har take biye musu suna shirme a titi ko dai maganar da 'yan uwanta suka fada a kanta gaskiya ne, in ko hakane tabbas zata fuskanci hukunci a gurin shi, take yaji k'irjinsa tayi masa wani mugun nauyi zuciyarsa na kara fada masa haka ne dama can tana biyewa 'yan iskan samari su lalube ta, shiyasa ta saba kuma take da sha'awa sosai! Idanunsa sukayi jazuri lips d'insa na kasa ya ciza had'e da dukan kujerar mota da k'arfi! Doh-doh ya juyo da sauri yana kallon ogan nasa alumu sun nuna ogansu ya fad'a tafkin so, a hankali yace." Sorry sir."

Da k'yar Rambow ya lallab'ata, ta yarda zata shiga motar, ganin yana k'okarin bude motar ne yasa ya gyara zaman sa had'e da murtuke fuska tamau!!! Da kansa ya bude motar rambow ya k'araso gurin da sauri.. Minti biyu tsakani ya nufi inda matasan samarin suke tsaye ya kirasu jiki a sanyaye suka bi bayansu domin sun fara tsarguwa ido hudu sukayi dashi a take suka zube a gurin. A hankali ya d"ago kanshi yana kallonsu yace." Me ya had'aku da waccan budurwar." Da sauri d'aya ya fara yi masa bayani." Murmushin takaici yayi yace." Ban yarda ba ko dai buduwarku ce? Ko kuma wani ne saurayin NATA ne ya sanya ku kuyi masa aiki a kanta." Girgiza kai sukayi suna rantsuwa yace." Ya sunan wacce ta sanya Ku wannan aiki ? Suka ce "Safiyya sunan ta." Gyda kansa yayi cike da takaici yace." Saboda rashin aikin yi kuka zo bakin

titi zaku walakanta hallitar Allah ko? Aiko zina zakuyi sai Ku je Ku b'uya a wani gurin kuyi tozarta mutum bashi da dad'i fa." Duk jikinsu yayi sanyi suka fara bashi hakuri, yace." Kuje Ku bata hakuri Ku dawo kuji wani Abu." Aikuwa da sauri naga sun nufo inda muke tsaye.

Mimi tace." Gwarafa mu San abunyi Asma'u. " nace " kyalesu suzo gurinan wallahi sai na ci musu mutumci." Fuskokinsu da alhini suka tsaya gabana d'ayan yace. " Kiyi hak......kafin ya karasa na zabga masa mari!! Shima d'ayan ya bude baki kenan zai magana na bashi kyakyawan mari guda nace" dukaninku hakurun me zaku bani."? Sunkuyar da Kansu sukayi kamar wata zarrariya nace "Ku bani guri don Allah 'yan iskan banza da wofi." Simi-simi suka matsa daga gurin.
Duk yana kallon abunda yake faruwa, miskilin murmushi yayi zuciyarsa babu sauk'i ko kad'an yace." Zaki shigo hannuna ne yarinya." Kafin suyi magana yace." Naga komai Ku rabu da ita." Suka CE." Insha Allahu." Shiru yayi na minti biyu kana yace." Rana ita yau insha Allah sabon company na zai fara aiki saboda haka ina buk'atar ku a gurin za'a baku 'aikin yi Ku daina wannan shashanci. " sai da suka kusa fad'uwa saboda godiya kana kallonsu zaka fahimci suna cikin farin ciki godiya kawai suke yi, kudi ya Ciro ya basu tare da sallamar su, suka bar gurin cike da murna da farin ciki.

Zuwa yanzu na tabbatar da yana cikin motar, nace dasu Munnu mu matsa gefe guda ma fara Neman abun hawa domin baza mu shiga motar ba. Aikuwa nesa da motar muka yi. Rambo ya biyo mu a baya kamar wani jela, sai rarrashina yake ni kuma ina botsarewa, a hankali Mimi ta rad'a min a kunne "Asma'u don Allah mu shiga wallahi mugun son ganinsa nake kwana biyu ni nasan halin da nake ciki a kansa duk abunda nake kokari nake." Kallonta nayi cike da mamaki !! Sai naga idonta ya tara k'walla tausayi ta bani mutuka Mimi tana sona tana damuwa da damuwa ta idan na shiga wani hali tana damuwa sosai,sai inda karfinta ya kare, ta bani tausayi sosai nace "Ku muje to" aikuwa suka biyo bayana. Rambow yaje ya bude mana kofar motar da sauri. Ni na fars shiga, k'amshin mugun turaransa yayi mun sallama, d'auke kaina nayi ban kalli shashen da yake ba, saboda shi kanshi haushisa nake ji sai ya dunga nunawa mutane kamar bai tab'a ganin mu ba wannan ai munafurci ne.

Kusa dashi da nazauna Mimi ta zauna sa Munnu rbow ya bude ya shiga ya zauna kusa da d'an uwansa muka tafi.

Munnu da Mimi duk sunyi sanyi sau sunkuyar da Kansu k'asa suke a hankali naji Munnu tace." Ina wuni." Shiru bai amsa ba, da wutsiyar idona na kalli gefan sa, sai naga idanunsa a lumshe tab'e baki nayi.Munnu rashin zuciya ta kara maimatawa "Ina Wuni" wannan karon da d'an k'arfi tayi maganar, idanunsa ya bud'e a hankali ya kalleta tare da fadin" lafiya 'yan mata ya kike."? Munnu tace." Lafiya lau." Murya a sanyaye Mimi ta gaishe shi ya amsa a sake tare da fadin sunan ta rad'au!! "Mimi me ya kawo gurin nan har kuke rigima da wad'ancan 'yan iskan kan." Mimi inda -inda ta fara DOMIN ta rasa abunda zata ce masa,  shiru motar tayi ni kuwa sai kauda

kaina nake bana so ma na kalle shi ballanta na shiga wan mi yanayi.

Cikin hikima ya zura hannunshi guda ta bayan mayafina naji ya shafo mazaunai na, da sauri!! Na gyara zamana gami da kallon gefan sa hankalina a tashe. Ido ya tsura min! Wanda sukayi ja kad'an. Da sauri na d'auke kaina gabana na fad'uwa.

Har yanzu hannunshi guda na cikin mayafina yana shafa min jiki, in banda ni dashi babu Wanda zai gane hakan. Motsi na fara yi INA duk a k'okarin na buge hannunsa, hakan sai ya bashi damar d'age rigata ta baya ya zura hannunsa a ciki yana shafa cikinsa zuwa ramin cibiya ta... Ji nayi kamar in kurma ihu!!! Na kalle shi da Jan ido! Kauda kansa yayi da sauri ya cire hannunsa had'e da sakin wani shegen murmushi yana cije lips d'insa kamar yanda ya saba.
Jikina yayi wani irin sanyi ina mamakin tacewar wannan guy ta fannin iskanci sai yayi Abu kamar bashi ba, dai-dai ta kaina nayi had'e da d'auke kaina hannu na sai rawa yake.

Hannunta ya tsurwa ido yana kallon kunshin da ya futo yayi rad'au domin har ya soma yin duhu ma saboda lallan yaji had'i zanan fulawar ya futo dara-dara sosai lallan ya burge shi, ya lura yarinyar tana da kyawun fata mussaman a jikinta fuskarta ce me duhu had'e da wasu k'ananun kuraje Wanda yasan ki na meye, mafi aka sari duk budurwar da take fa wannan kurajen fuska kuma tayi magani sunki' mutuwa to ta bunkici kanta tana da tsantsar sha'awa ne, to itama Asma'u tana dasu a gefe da gefen fuskarta amma basu da yawa.

Munnu aka fara saukewa mukayi sallama da juna ta tafi. Shiru motar sai saukar nuffashi mu ganin munnu ta sauka ne yasa nace da Mimi ta matsa na gyara zamana sosai na rabu da jikinsa, a hankali ya Dan kalle mu ni da Mimi yace." Mimi na tambaye ki baki bani amsa ba." Mimi da soyayyar sa ta kusa kassarata ta d'ago kanta cike da kunya tace" munje ayi mana lalle ne sai muka shiga gurin domin ayi mana gyaran fuska shine fa kawai muka gansu sun shigo ciki."

Murmushi yayi a hankali yace." Kuma ba samarin ta bane"? Mimi tace" ko d'aya wallahi a sali ma mu bamu tab'a ganinsu ba kawai tsabar iskanci ne." Dariya yayi gami da d'an Sosa sumar sa as'usuel yace." Anya kuwa Mimi kin manta halin 'yar Uwar ki ko."? Murmushi tayi cike da kunya.

Duk ina jinsu dauke kaina kawai nake Sam! Bana so na kalle shi Allah ya Isa kawai nake masa cikin zuciyata jin damshi a jikin wando na nasan ko menene,tunda ya tab'a min jiki shikkenan nake zubah.

Yace." Buki kuke ko suna."? A hankali tace." Muna party ne na murnar kammala makarantar mu."

Gyad'a kansa yayi tare da fad'in "Yayi kyau, yanzu ni gest house d'ina na nufa zan je i n huta so

ina ganin zamu je daku tare zuwa anjima sai in sanya a kaiku har gida, na lura 'yan iskan samarin nan baza su k'yaleta ba ko bakya ganin yanda ta mammare su saboda tsaurin ido."

Mimi tace." Nagani wallahi halin Asma'u sai ita." Cikin zuciyarsa yace." Sai ni kuma ba,domin dai-dai nake da ita
A fili kuwa cewa" yayi kin gani ko, ina tsoran abunda zasuyi mata na wulakanci ni mutum ne me daraja mace, mussaman ita mace me daraja, saboda haka Ku muje can d'in kafin asan yadda za'ayi dasu. "

Wani mugun kallo na watsa masa wai ni zai yi wa wayo lallai ma, Mimi Sam bata fahimci komai take fad'in"aikuwa haka zamuyi don nima tsoro nake ji Asma'u  baga ita ba su baga su b......
Katseta nayi da sauri tare da fad'in" Dallah yi mana shiru! Anki zuwa d'in ke in zaki je kije babu Wanda ya rike miki k'afa Mtsssssss!!!!!

*31/October/2019*
[11/1, 10:55 PM] .: *BABBAN YARO*

*Mallakar_BINTA UMAR*

*LITTAFIN MALLAKI NA NE KUN BIYA KUD'IN KARATU NE KAWAI DUK WACCE TASAN ZATA FUTA DASHI WAJE DON GIRMAN ALLAH TAYI MIN MAGANA NA DAWO MATA DA KUDIN TA*

*36*

Shiru tayi tana kallona nace"kawai kiyi mana shiru kin kasa fahimtar inda ya dosa." Mimi taji haushin abunda nayi mata, d'auke kanta tayi had'e da bata fuska. Juyo wa nayi gare shi raina a

bace nace"bana so muyi rabuwar rashin mutumci da kai saboda haka tun wuri ka sauke mu a gida mu tunda muke bamu tab'a zuwa wani guest house ba.
Shiru yayi min kawai hankalinsa na kan wayarsa , ji nayi kamar in kama shi da kokawa, saboda yanda naji raina yayi wani mugun b'aci.. Murya a sama nace"kaji."!!!! Kallona yayi babu walwala a fuskarsa yace." Wai ke meyasa baki da d'a'a ne.? Uhum wallahi idan baki rufe min wannan bakin naki ba zan baki mamaki! Yanzu nan." Hararsa nayi had'e da d'auke kaina daga kansa ganin yanda yake min wani kallo hade da tsare girarsa.

Shuru ban k'ara cewa komai ba, saboda na fuskanci guy zai iya aikata duk abunda yayi NIYYA a gaban kowa ba damuwar sa bace.

Amma na kudurta a raina komai nacin sa yau bazai samu abunda yake so ba zan jajirce inyi yak'i da zuciyata domin kar ta bani kunya.

Unguwa uku muka nufa hanyar babu gidaje sosai sai kangwaye manya manya wasu an gama ginawa wasu ba'a gama ba, wani had'addan Gate naga mun nufa tunda ga nesa mai gurin naga ya mike da sauri yana k'okarin budewa.

Motar ta silala ta shiga ciki  can gurin parking spece ya nufa ya kashe motar, da sauri Rambow ya futo ya bude masa kamar yanda ya saba, ya futo nida Mimi muka futo jikinmu duk babu k'wari. Kai tsaye wani haddadan bene naga ya nufa ya ranshi suka rufa masa baya.
Ni da Mimi muka tsaya muna bin gurin da kallo kamar wasu shashashai  sai da ya hau sosai ya juyo yana kallonsu hade da rike karfen barandar benen  da ido yayi min magana wai mu zo, d'auke kaina nayi kamar ban ganshi ba.

Bude wata kofa yayi yai shigewar sa, muka wai waye gabas kudu da arewa babu gurin zama duk girman gurin bene guda ne shine Wanda ya hau ga wata Uwar rana da ake kwallarawa Sam babu gurin zama shima kansa me garin bayazamap rufe get din d'an d'akinsa ya koma saboda rana,
Wani irin jiri naji yana d'ibana na kalli Mimi fuskata babu walwala nace" kinga abunda kika jawo mana ko Mimi. "?

Tace. " me na jawo miki bayan ke aka taimaka wallahi na tabbata ba daban wannan guy yazo gurin nan 'yan iskan samarin nan sai sun wulakanta ki a banza don Allah ki daina yi masa rashin kunya." Kallonta nayi cike da takaici nace" Mimi so ya rufe miki ido bakya ganin illahr abunda nake hango mana ko? Wannan guy fa nafi kowa sanin waye shi, kin manta abunda yayi min ko Mimi wallahi da wata manufar ya kawo mu gurin nan."

Mimi tace." Koma dai meye gwara shi akan wad'ancan 'yan iskan, kuma na tabbata kaifin harshen ki ne ya jawo miki duk abunda yayi miki, ki kwantar da kanki tunda kinga ba tsaran ki bane ta ko wane fanni mu rabu lafiya dashi." Nace" Mimi abunda kike fada Sam bazai yihu ba wallahi bazan kwantar masa da kaina ba ni ba shashashar mace bace."

"Shikkenan Asma'u duk abunda zakiyi kije kiyi babu ruwana" Mimi tafad'a murya a cunkushe. Nace" muje mu zauna kan wad'ancan kujerun da nake hangowa a saman gurin duk sanda ya gadama ya futu sai ya sanya a kaimu gida. " kai tsaye benen muka nufa jikin nmu duk babu k'wari.

Duk abunda sukeyi yana kallonsu  ta CCTV CAMARA Yana zaune gefan bed da gajeran wando a jikinsa hannunsa rik'e da karan sigari yana zuk'a duk sanda ya tuno yanayin da yaga yarinyar d'azu sai yaji kamar ya kurma ihu!! Kishin yarinyar yake sosai yanzu shima ya fara gazgata abunda zuciyarsa take gaya masa a game da yarinyar "Sonta yake!"""""

Zama mukayi mukayi jungum Mimi ta dauko wayarta tana game kallonta nayi naga kamar wacce take cikin gudansu nace"Mimi baki damu ba ko." Kallona tayi tare da fadin" Asma'u in NATA da hankalina yaya zanyi nasan dai duk rintse sai yazo ya kaimu gida."
Gyad'a kaina nayi kurum zuciyata nayi min zafi!. Rbow da doh-doh na hango suna shawagi a kasan gurin sai kuma suka nufo benan, hankalina yayi wani mugun tashi ganin wani k'aton muzuru a hannun Rbow! Da k'arfi nace" Mimi kalli hannun Rambow kiga meye."?  Da sauri ta kalle shi, gabanta ya fad'i tasan duk a duniya babu abunda na tsana a rayuwata kamar mage to wannan ma uban mage ne k'aton muzu bak'ikkirin dashi

Cikin rashin sani Rambow ya jefar da muzurun nan a gurin da muke aikuwa yayo tsalle hade da d'afewa jikina, wata irin tsawa! Na kurma, had'e da ihu!! Me k'arfin ina fad'in"Bana so"!! Zumbur na mik'e tsaye waya ta ta fad'i kasa haka handbag dina, kamar Wanda aka kara tun zurawa yayo kaina a karo na biyu! Jikin kofar na silale na fad'i ban san inda kaina yake ba. Da sauri ya mik'e tsaye dalili duk yaga abunda ya faru ta cikin CCTV babu shiri ya bude kofar Wanda nake ji a sume Mimi na kaina ta cire min mayafi tana fiffita min,  yana bude kofar nayi ciki tare da yin plate a k'asa, cikin tsawa yace da Rambow ya d'auke muzurun ya futa dashi. Aikuwa da sauri ya d'auke shi . kaina ya dawo ba tare da tunanin komai na ya d'auke ni kamar jaririya ya shiga ciki dani, da k'afarsa ya rufe kofar.. Mimi ta tsaya jikin ta sai b'ari yake.

Shimfed'e ta yayi kan wata k'atuwar sofa me kamar gado, da sauri ya nufi frighe ya d'auko robar ruwa me sanyin gaske ya bude murfin ya fara an taya min a fuska,  ruwan ya kare Tass ban motsaba.
Da sauri ya burkitoto baya had'e da zage zif d'in rigar ya cire ta jefar da ita yayi k'asa, ya rasa me ma zaiyi  wani ruwan ya kara dauko wa a karo na biyu har ya bude zai zuba mata kuma sai ya aje shi, birkitota yayi suka yi fecing da juna fusakarta ya tsurawa ido tayi kyau sosai idonta a rufe ruf gashin idon yayi wani gazar-gazar dashi girarata ya kalla yaga an gyara kuma hakan yayi masa, idonsa ya sauke kan lips dinta, sirara dasu gwanin sha'awa, d'an ya tsanshi guda ya sanya yana shafawa hade da lumshe idonsa, ba tare da tunanin komai ba, ya haye kanta had'e da tallafo kanta da hanyenshi biyu ya dora bakinsa kan nata ya zura sosai ya fara hura mata nuffashi a hankali.. Kokari kawai yakeyi kar ya zarme!! Don hankalin sa yayi mugun tashi,

inaaaaa!!! Kasa daure wa yayi kawai ya sarkafo harshenta da NASA ya fara tsotsa kamar Wanda ya samu sweet me shegen zak'i!!!

Duk da ya fahimci ta dawo hakan bai sanya shi ya sauka daga kanta ba, cigaba yayi da tsotsarta kamar mayuwancin zaki da ya samu nama."

Nauyin mutum taji a kanta da sauri ta bude idonta da sukayi mata nauyin gaske ta sauke a kansa, ido suka hada dashi yana lumshe mata idonsa Wanda suyi bala'in k'ank'ancewa sunyi wani jazur dasu.
Duk da jikinta babu k'wari hakan bai hanata yunk'urin kwace kanta daga hannunsa ba, k'arfi ya sa sosai ya danne ta had'e da hard'e mata k'afafunta da nata. Cikin rashin kuzari ta daga hannunta guda tana dukan bayan shi hade da yakuso fatar bayan shi, dama babu riga a jikinsa, bakinta yayi nauyi sosai ta inda ta kasa masa magana sai kauda kanta take duk a k'okarin ta na k'watar kanta.

*Amjadu* sai da ya tsotsi bakinta iya son ransa sannan ya d'aga ta ido jazur yake binta da wani mayen kallo.... Yawun bakin ta tattauro ta taufa masa a k'irjinsa dake cike da kwantaccen gashi bakikirin dashi,abunka da farin mutum, har ta da kan nipple d'in wani gashi ne a kewaye yayi duhu sosai, mik'ewa tayi jiki babu k'wari ta fara k'okarin maida rigarta, mutukar tace zata yi magana a lokacin to kuka yana iya subuce mata.

Rik'e rigar yayi tamau da hannunsa guda d'aya hannun kuma ya d'ora shi a jikin birziyyar tata yana murza hannun kamar zai sab'ule mata.

Wani irin kukan takaici na saki had'e da fad'in"Allah ubangiji kayi min sakayya kan wannan bawa nake, wasu zafafan hawaye suka zubo min.

Hannunsa ya d'auke daga jikina ina kallonshi ya d'an dafa goshin minti biyu ya dago kansa yana kallona tare da fad'in" Ni ki kewa wannan muguwar addu'ar ko."? Cikin hayani nace"idan da addu'ar da tafi wannan zan maka, meye ruwanka dani ka dame ni ko ina naje sai kaje kai burinka kawai ka kawo ni gidanka kayi iskanci dani, gashinan ka fara jawo min zargi a gidanmu." Murya na rawa na k'arashe maganar.
Tsura min ido yayi naga fuskarsa ta d'an canza da b'acin rai! Yace." To sai ki fad'a min abunda nayi miki Wanda yasa kike fad'ar haka."? Nace" ni duk ba wannan ba, kawai ka tashi ka mai damu gida ko ka sanya a mai damu" nafada murya ta babu sauk'i. Hannuna ya kama tare da fad'in" zo ki gani abunda ya faru dake, in banda haka babu abunda zai sa na kusanta kaina dake." Fuzge hannuna nayi tare da fad'in" nasa ni ai suma nayi, haka nake yi duk lokacin da naga mage me kuma zan gani, ai da ka bari na mutu kan kayi min abunda kayi a yanzu, saboda ni nak..... Shiru tayi bata karasa ba jin tana nema ta tonawa kanta a asiri

Mik'ewa yayi daga kusa ni  tare da fad'in" Kar ki dame ni da surutun banza malama na k'yale ki, amma kafin in futo daga toilet ki rufe wannan balo din naki idan ba haka idan na futo na gani zaki raina wayon ki."

Da sauri na kalli jikina naga Ashe ban sanya rigar ba, tana dai hannuna, saurin gyara zif din nayi na hau zurawa da sauri.
Toilet ya shige abunshi ba tare da ya kara tanka min ba.
Bayan na sanya rigar tawa na fara neman inda mayafi na, kan kujerar ban gan shi, cike da mamaki na fara duba dube a dakin Sam babu alamar sa, takure jikina nayi kan kujerar  ina kallon yanda Mamana suka bulutsu ta saman rigar kasan cewar ya matse ni sosai dama rigar tayi min kad'an  sanya ta kawai nake, kuma ka'ida ne duk d'inkuna na kananu ne bana tab'a yadda ayi min babbar Riga. Motsin bude kofar toilet din naji nayi saurin kauda kaina daga kanshi, gabana na fad'uwa yana daure da k'aramin towol iya cinya zuciya ta nace shi kam bashi da kunya ko guda wallahi, INA kallonsa ta wutsiyar idona Yana shafefensa minti biyar ya futo da kayansa, mai makon ya sanya su sai ya k'araso inda nake zaune rike da kayan a hannunsa, na kauda kaina da sauri ina kara gyara fuskata addu'a kawai nake Allah ya bani rinjaye a kansa, zama yayi kusa dani tsigar jikina ta tashi na dake! Sosai ban kalle shi ba, cikin wani iri voice yace." Ungo balle min botoran rigar nan." Satar kallonsa nayi cike da mamaki sai ya dinga sanya ni Abu kamar wata matarsa.Nace." kan wane dalili da ni CE nake b'alle maka botiran rigar ka, ni ka k'yaleni kawai." Matsowa yayi jikina sosai naji wani sanyi a fatar jikinsa, nan take na tsinci kaina da wata irin a zababbiyar sha'awar sa, yace." Yanzu na ganki a arha shiyasa nace ki b'alle min kuma na da lokaci k'ank'ani hakan zai zama aikin ki domin baiwa ta zaki zama ta ko wace siga." Kallonsa nayi ina ya mutsa fuska nace" wannan duk kana fad'a ne domin kaji dadin bakin ka, ni dai na farko ba matarka bace balle kace haka  ni baka da iko dani da duk wani abunda ya shafe ni."

Murmushi yayi hade da shafa fuskarsa as'usuel yace." Karya kike ko yanzu na gada zanyi iko da abunki kuma babu yanda zakiyi dani, wallahi kuma na kara ganin kina rigima a kan titi sai ranki yayi mugun b'aci sai na miki horo me tsanani, kullum kina kiran kanki mace me daraja amma kin kasa hankali kina shashanci, rigima da 'yan iska  ki kiyaye wallahi."!!! Yafad'a. Da murya a kausashe.
Mamaki yaba ni sosai nace "To kai meye damuwar ka meyasa da ka ganmu bakayi tafiyarka ba, duk abunda nayi rayuwa ta ce."!!! Na fada haka cikin tsiwa da sigar bada haushi.
 A zafafe! Ya juyo dani muna fuskantar juna, fuskar sa a hade yace." Ina magana kina girgiza jiki don baki da kunya, wa ya fad'a miki saboda ke na tsaya a gurin? K'ifk'ifta ido nake tsoro ya fara shiga ta ganin yanda yake wani muzurai duk wannan fara'ar babu ita a fuskarsa.
Ya cigaba da cewa"Saboda Mimi na tsaya na lura yarinyar kamila ce ita yafi kamata ta kira kanta mace me daraja bake ba, tunda duk ganin da zanyi muku bata tab'a aikata mummunan abu ba, ke kuwa fa.? Yafad'a yana zare min ido! Kasa nayi da nawa cike da tsoro! Girgiza kafad'a ta yayi da k'arfi yace." Ki bani amsa mana".? Shuru babu magana. Yace." Mimi tafi kirki tafi ki kyau ta fiki hankali da sanin ya kamata,   Ko ba haka bane."? Shiru nayi masa bakina na rawa, tsaki! Yaja had'e da fad'in." Ko kwana uku ba ayi na 'yan uwanki suka zo nan suna

tuhumar ki, kan rashin yarda saboda sun San halin ki, hakane koba haka ba ne."?

Wasu zafafan hawaye ne suka soma zubo min a fuska na fara kifta idona domin in mai dasu Sam bana son yaga gazawata.
Sakina yayi yace." Wannan ya zama na farko da k'arshe a gurin ki, wallahi wallahi kar in kara kama ki da aikata Abu makamcin haka, zan tsaurara bunkice a kanki domun nima ban yarda dake b........... Hannu na d'aga masa murya ta na rawa na mik'e tsaye cikin tsananin b'acin rai nace." Duk abunda zaka fad'a ka fad'a akaina dai-dai ne a gurin ka, ka fad'e shi son ranka, Idan iyayena sunyi zargina kai meye alak'arka dani da zaka tasa ni a gaba kana zagina had'e da fad'amin bak'ar magana, idan iskancin nakeyi Kaine ka koya min, tunda nake a rayuwata babu namijin da ya tab'a kusanta ta sai kai, me yasa na rufa maka asiri a don duniya? Meyasa na rufa maka asiri a gidanmu?! Ka sani ina da damar da zan shiga ko ina ne in b'ata maka suna me yasa ban yi ba?!! Sai kai ne zaka turke ni kana tuhumata kan abunda ban aikata shi ba. To wai ma meya shafeka dani idan a *Ibedi*  nake ina karuwanci! Babu abunda ya shafeka dani, zan dauki hakan daga makusanta na, wato iyaye na, amma bazan dauki raini da k'azafi ba daga gurin wani gardi."!!!!!! Ganin ya mik'e a zafafe! Ne yasa na ruga da gudu bakin kofar futa ina k'okarin bude wa, kulle gam!! Finciko ni yayi da hannu guda ya jefar kan kujerar a zafafe ya Fidda hannu ya gaura min mari, Wanda sai da naga wasu taurari, yana haki! Yake cewa." Ni kike fad'awa wannan maganganu ko."
Hannu na nasa na dafe kuncina zuciyata nayi min suya, tsura min ido yayi fuskarsa kamar Wanda aka aikowa da mala'ikan mutuwa yace." Ana fad'a miki meye rayuwa kina k'okarin zagin mutane, Dan kinga na damu ke shine kike wannan iskancin!? Kije ki tambayi waye. *Amjadu* a gari zasu fad'a miki, ko kuma kije ki tambayi 'yan mata irin ki, wad'anda suke da kyau da wayewa ilimi kud'i ba irin ki ba bagidajiya da ko kwalliya baki iya ba, idan kika tambaye su zasu fad'a miki wanene ni,  idan mace bata yi min ba, ko kallo ba ta ishe ni ba, duk kyawun ta da waye warta don ke kin samu wannan damar shine kike mun iskancin har da su zagi,."!!!!
Hannuna na sanya ina dukan k'irjinsa da yayi min rufa dashi INA kuka nake fadin" Babu ruwana dasu tunda ba Kai ne a gabana ba, da kake maganar Mimi tafi kyau tafi ni kirki da komai, to sai me? Idan sonta kakeyi to Bari kaji wani Abu, itama sonka take sai me? Ni babu abunda zai dame ni, daku  kuma daga yau ka futa daga rayuwata in huta da jaraba! Idan haka gaskiya take to bana bukatar ta a gurin ka, duk halin da na fad'a kai ne sila."!!!!!!!! Na k'arashe maganar ina kuka wiwi! Bakin ciki kamar ya kasheni, wai ni suke zargi!! Lallai na yarda da maganar hausawa da suke cewa namiji sai yayi Abu ya zama ado a gare shi, mace ko da tayi sai duniya ta  ji ta. Yanzu dubi babu sata babu zina babu mayyata amma suna zarginta.

Kuka nake ina dukansa a k'irji hade da ya kushin sa, so nake kawai ya d'aga ni. Yak'i sai kace wani maye ya zuba min idonsa da suka yi jazur dasu. Minfi minti goma a haka sannan ya sauka daga kaina, na mik'e da sauri! Had'e da d'aukan k'ananun pillows ina jifansa dasu hade da fad'in"I hit you! I hit it."!  Kayansa ya ke sanyawa ranshi a mugun b'ace ya zama dole ya cire yarinyar nan daga ranshi domin ya lura tana da mugun taurin kan tsiya ga rashin kunya dole yayi nesa da ita da rayuwarta dama tausayin maraicin su yake ita kuma bata duba wannan. Dole ya aje ta gefe guda ya fuskanci abunda yake gabansa bata tab'a b'ata masa rai ba irin yau. Yana jinta har ilayau tana jifansa hade da surutai share ta kawai yayi ya dauki turaransa ya

fesa jikinsa, dashu. Juyo wa yayi muka hada ido, gani fuskar sa nayi kamar ta zaki! Da sauri na jefar da pillow hannuna hade da zubewa kan kujarar ina shashshekar kuka.

Ba tare da yace min komai ba ya bude kofa ya futa, zumbur na mik'e nima na bi bayansa, Mimi ta mike da sauri hade da mikomin mayafina na yafa muka sauka k'asa.

Ina kallonshi shida rambow suna magana sai kuma naga Rambow ya nufi parking spece da sauri ya bude wata lafiyyayr mota yana buge ta shiga yayi ciki ya futo da ita kana ya fito daga ciki hade da bude murfin motar.

Cikin yanayin tafiyar sa ta jarumai ya k'araso gurin hade da karb'ar key din motar hannun Rambo ya shiga ya zauna mazaunin dravar, rbow ya k'araso kusa damu tare da fadin" kuje Ku shiga motar.

A zuciyata nace"Yau shi zaiyi dravin din kenan Mtssss. Baki na tab'e kawai INA d'auke kaina muka Isa gurin motar
 Mimi ta kama murfin kofar baya zata shiga yace.'"Mimi dawo nan kusa dani." A hankali ta saki murfin ta bude na gaba ta shiga ta zauna tana sink'e kai. Tsaki nayi a fili na bude na shiga. Kunna motar yayi had'e da kallonta da murmushi a fuskarsa yace." Ko kina so in zama dravar ki ne." Mimi ta sunkuyar da kanta cike da kunya tana mamakin yanda yake mata magana, cikin nutsuwa motar gidan, ta hau kan kwalta. Music na tashi kad'an-kad'an.. Sam naki dago kaina in kalle shi balle in San wane irin kaya ne a jikinsa, shiru motar kusan minti goma yace." Mimi naji wata magana gurin 'yar uwarki hakane."? Mimi gabanta ya fad'i kaddai Asma'u ta fad'a masa, sai ta sanya mayafin ta ta rufe fuskar ta, naji kamar ina mangarta, saboda haushi tsaki naja me k'arfin gaske Wanda nasam duk sunji ni,amma abun mamaki ita dashi babu Wanda ya kulani.

K'asa-k'asa naji yace." Kinyi shiru my Mimi hummm! Wai ya sunan ki ne na gaskiya ne."? A hankali Mimi tace." Sunana Aisha." Cike da kulawa ya kalleta yace." Mommah na ce ashe haba shiyasa naji ina kaunar ki, kin San duk me wannan sunan tana da daraja irin sune ya kamata su kira kansu da mata masu daraja."!!! Gabana ya yanke ya fad'i. ! Babu shiri na dago kaina ina kallonsu, ni YAKE fad'awa magana kenan. Zuciya tayi min bak'ik'ikirin, haushi ya turnike ni, ganin yanda yake sakin wani murmushi yana kashe muryarsa Wanda sai na kasa kunne sosai nake jin abunda yake fad'awa Mimi.

Yace." Yaushe ne party naku."? A hankali tace." Asabar ta jibi." Gyad'a kansa yayi fuskar da a sake yace." Wane guri za'ayi."? Tace" cikin makaranta ne." "Hakan yayi wane irin tanadi kuka yi." Mimi tace"mun gama komai ma."
"A'a ki fadamin ko akwai taimakon da zan miki kinji ko." Mimi ta dago kanta muka had'a ido da ita ta mirror wani banza kallo na watsa mata gami da d'auke kaina, cike da mamaki ta d'auke kanta tana mamakin kallon da nayi mata. Ni kaina sai bayan nayi mata shi na dawo ina da nasa ni.

Yace." In kuna son a futa sai a ka ma muku guri ko."? Girgiza kanta tayi tare da fad'in" gidanmu baza'a bar mu ba." Murmushi yayi kawai, minti uku yace." Tom ya maganar mu dake." Mimi duk ta diririce tana kauda kanta. Dariya yasa har sai da hak'oran sa suka bayyana. Yace." Ko dai k'arya take miki ne? Ita ce ta aiko kanta. " Mimi ta girgiza kanta alamun A'a. Ji nake kamar in shako wuyan Mimi in ta dukanta ko na huce takaicina a zuciyata nace "Banza wacce ta rako mata kawai.!!!

Hira suke dashi sosai duk k'arfin hirarar shine yake yi ita dai sai Umm da umum kawai take yi, ni zaune a baya sun bawa banza a jiya ta, Allah-Allah nake mu sauka daga motar ko na samu in samu sassaucin rad'adin da zuciyata take min a game dashi.
Dai kwanar gidanmu yayi parking din motar, da sauri na bude na futo, babu Wanda ya kula ni a cikinsu, shiru-shiru Mimi bata futo ba, ga glass din motar duhu balle inga me ya tsare ta a ciki, kawai sai na tsinci kaina da k'urawa motar ido ina jin wata irin hajijiya na k'okarin ta yar dani a gurin

Duk abunda take yana kallonta, yaji mutukar dad'i ganin yanda ta tada hankalinta,sai ya nuna mata batada wayo wallahi tunda bata da kunya ita. Rike Mimi yayi da hira, Mimi kuwa ta saki jikinta suna ta hira abunka da zuciyar da ta narke a kan so. Idona ne ya fara kawo ruwa ganin kusan mintina goma Mimi bata futo ba yasa na fara k'okarin tsallaka titi nai tafiya ta duk sanda ta gama soyayyar ta tawo.

Wayarsa guda ya dauko hade da sanya mata wani sabon sim card Mimi taga ya mik'o mata dalleliyar waya k'arar Infinx yace." Ungo wannan ki sanya chaji na sanya miki sabon sim card zan dinga kiran ki muna gaisawa." Mimi taki karb'a tana sink'e kanta yace." Ashe ba so na kike ba ko."? Girgiza kanta tayi ta sanya hannu biyu ta karb'a tana godiya yace." Yawwa ko kefa." Bude mata kofar yayi da kanshi suka yi sallama.

Motar ya ja da sauri ya bar gurin.Mimi kuma ta fara Neman inda Asma'u take bata ganta ba, zuciyarta ta ayyana tabbas tayi tafiyar ta, sai ta tsallake titi cikin sauri ta nufi gida itama............

*Yanzu aka fara*